CIWON 'YA MACE

By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

GARGADI

Aguji daukan Labarin nan a daurashi a kowacce irin kafa batare da iziniba.

PAGE 1-2

BISMILLAHI RAHAMANIR RAHIM.

Dumin ruwan hawayen da ya sauka a kumatunta shi ya dawo da ita cikin hayyacinta, har ma ta samu damar sa hanunta ta share hawaye. Kodayaushe cikin yaba tarbiyan gidansu ta ke, duk irin tsaurara tsaron gidansu ba ta kallon shi a matsayin takura, asali ma sai hakan ya ke zamar mata abin alfahari.

Ajiyan zuciya ta yi mai karfi, sannan ta ci gaba tuna lokacin da ta yi ta ba wa Rahma damar sanar da ita duk wani zance komai muninsa da dacinsa.

Hawaye ta sa ke sharewa a karo na biyu, ta na me tuna furucin ta ga Rahma, "Zaman tare be ce haka ba Rahma. Domin ni duk abin da zan ji an fada a kan ki da 'yan gidan ku sai na fada mi ki."

"Yanzu me ki ka ga an yi ban fada miki ba? Ni ma din ai haka ne, babu wani abun da zan boye miki."

"Na gani a cikin kwayar idaniyarku wallahi. Na fa dago na ga irin kallon da ku ke mini, idan su za su mini haka bai da ce ace hardake ba. Amma ba komai."

Yunkurawa ta yi da nufin mikewa Rahma ta yi saurin riko ta ta na cewa, "Shikenan na ji, da ga yanzu komai na ji zan dinga fada miki. Amma karkiji haushina." Cikin sauri ta sa hannunta ta dafe kumatunta tare da runtse idonta ta na me jin zafi har cikin tsakiyar kan ta, dalilin tuna marin da ya zazzabga mata daren jiya.

Ji take kamar ta na jin a zabar marin har yanzu, dan haka hawaye su ka zobo mata.

Hannu ta mika ta share, sannan ta yi saurin mikewa cikin yanayi irin na mai tunani, komawa ta yi ta jingina bayanta da bango tare da kara yin zurfi cikin tunani, zuwa can ta shiga fadi afili, "Bansan yadda zan yi ba ne, domin ya na sama da ni, sosai na ke jin bakin cikin marin nan da yayi mini, a can baya ina amsan kowanni irin hukunci da ga gareshi, banajin zafi sam, saidai ma abin ya zamar min abin alfahari. Me yasa wannan karon ya sauya? Jiya da safe da hannun sa ya miko mini sakon Mamy, fuskar sa cike da walwala, zuwa dare komai ya sauya, saidai bana bakin cikin sauyarwa ta shi, domin yadda ya ke ji na a ranshi inajin shi fiye da haka a kasan zuciyata, domin da ina da dama ba marin biyu kawai zan mishi ba, saina mishi doka da ko lada aka bashi bazai iya mikewa ba, amman Kash sai daman yazo a hannun shi." Nisawa ta yi a daidai lokacin da ta ji kiran da Mamy ta ke kwala ma ta, cikin yar karamar muryanta da bata fita

sosai ta amsa, sannan ta fice ba tare da walwala ba.

"Nur! Lokacin fa yana kurewa, kizo karki makara."

"Mamy ni gaskiya a canza min makaranta." Wani irin kallo Mimy ta mata da mamaki akan fuskarta, sannan ta ce "Lallai Nur kina da aiki, idan an canza miki makarantar kofar gida ma zaki daina fita ne? Ko kuwa jama'ar unguwan ma zakibar haduwa da su ne?

Shirun da taga Nur ta yi yasa taci gaba da cewa "Bana son irin wannan, maza kizo ki wuce." Cikin dakin ta juya batare da ta ce komai ba, a cikin kankanin lokaci ta fito fuskarta babu walwala.

Kallon ta Mamy ta sake yi a karo na biyu sannan ta ce "To ki saki ran mana, me zaisa ki takurawa zuciyarki bayan ke ce auta mowar 'ya'ya" Murmushi ne ya subuce mata, duk yadda taso ta daure ta kasa, dariya ta yi kadan sannan ta hade fuska tare da cewa "Na tafi"

"Adawo lafiya Allah ya tsare. Kuma daga yanzu sai ki dinga kiyaye bakin ki, shi mai tarkon tsuntsaye baya ɗaga kara. Kome zakiji karki tanka."

Jin furucin Mamy ya kara tada hankalinta, cike da bacin rai tabar gidan.

Bayan ta dauki hanyar ma tafe take tana waiwayen bayanta har ta kawo kofar wani dandasheshen gida, duk unguwar gidan ne ya haska layin sabo da kyan sa da tsarin shi, karamar kofar da ke jikin get din gidan ta nufa, kai tsaye ta tura kofar ta shiga, mai gadin gidan ta gaida, sannan ta wuce ciki, a harabar gidan ta tsaya cikin daga murya tace, "Helen!" Batare data rufe baki ba wata buduwar yariya ta fito yar kimanin shekara goma sha 16. Baka ce amman ba can ba, kyakyawa ce sosai, uniform ne a jikinta riga da siket daidai guiwa, kanta babu dankwali yasha kananan kitsu, hannu suka sha da Nur da ke tsaye itama cikin uniform din ta ke, saidai akwai banbanci domin ita Nur siket dinta ya wuce guiwa, kuma bayan dankwalin dake kanta akwai dan karamin hijjabi, bayan sun sha hannu da Helen su ka juya suka fice a gidan.

Da alama gaba dayan su cikin damuwa su ke, domin gaba dayan su tafe suke suna tunani, suna daf da barin layin wata zungureriyar mota da ta fito da ga bayan su ta faka a gaban su. Tun kafin sukai ga inda motar ta faka Helen ta ce, "Poul ne"

Kallon motar Nur ta yi domin sai a yanzun ta dan ji nutsuwa tazo mata tun fitowanta gida, ita ko Helen da saurin ta ta karasa gaban motar, lokacin da Nur ta iso gurin yayi daidai da lokacin da yake mikawa Helen kudi. Kallonshi Nur ta yi ya na zaune a mazaunin driver, kyakyawa ne na gaske, domin sabo da kyanshi baka iya yi masa kallo daya ka cire Ido, sai dai akwai tarin jin kai tsiya a tattare dashi. Shigarshi akodayaushe kamar ta cikekken bahaushe, daker Nur ta iya dauke idon ta a kanshi  badan ta gaji da kallonshiba sai dan kar ya fahimci tana kallonshi. Kasa ta yi da murya sannan ta ce  ta ce "Ina kwana? " Kawar da kai ta yi tare da runtse ido, sai dai harta bude idon be tankataba. Duk cewa Tasan yaji sarai amman be amsa ba. Bata ji mamakiba dan tun da ta ke gaidashi be ta ba amsawa ba bare ya dago idon sa ya dobe ta, saidai hakan be taba damun ta ba, kuma bata taba jin kyashin gaidashi ba aduk lokacin da zata ganshi. Wajen ta bari bayan ta kara gaba ta tsaye jiran Helen.

Wucewan motar ya sa ta waigowa ta kalli Helen, ita kanta fuskanta babu walwala, dan haka ta ce "Helen Duk da kyautan kudin da aka baki banga kinji dadi ba, kuma da alama ya bakine dan ranki yayi fari tunda har ya biyoki hanya ya baki, ni ai dauka nake ko ke baya iya gane ki, dan bantaba ganin ya kalleki ba bare yayi magana da ke, ni fa wallahi ada da farko na dauka kurma ne, sai ranar da nazo na ji yana balbala balaki a cikin gida, kuma har yau bantaba jin sa yana

maganar arziki ba, idan har zakaji muryansa to fadane kawai."
Murmusawa Helen ta yi tare da cewa, "Ko maganar arzikin ma yake haka zakijita kamar yaki, maganar sa babu yawa kuma babu dadi" Itama Nur dariya ta yi sannan su ka ci gaba da tafiya, bayan sunyi tafiya me tsawo Nur ta sake kallon Helen, rashin kwanciyar hankali karara akan fuskanta dan haka ta zungureta tare da cewa, "Helen wai me ke damun ki ne haka?"

"Badan mun yi nisa da gida ba da na koma na bawa Mama wannan kudin"

Lumshe Ido Nur ta yi, domin dama tatsuniyar gizo bata wuce ta koki, cigaba ta yi da tafiya tana cewa, "Ki boye idan kin koma sai ki bata." wannan karon Helen ba ta ce komai ba, tun da ga lokacin har suka isa makarantar babu me ma wani magana.

Haka har suka tashi daga ita har Helen din basu da wani walwala, wadda duk wadda ya san su yana iya fahimtan hakan.

Helen ce ta fara shigewa gida sannan Nur ta isa na su gidan. Tana saka kafa a falon ta hangi shi zaune ya daura kafa daya kan daya; tare da ware hannun shi duk biyun a saman kujira. Tsoro ne ya so dirar mata, saidai wata zuciyar nacewa karki sake kiji tsoron sa, dan haka ta dake ta shiga kwalawa Mamy kira. Har sau uku ta kira bata amsa ba dan haka ta tabbatarwa kanta cewa Mamy bata cikin gida nan. Duk kokarin ta wajen ganin ta dake saida gabanta ya shiga faduwa, daki ta nufa saidai tana daf da shiga dakin ta ji ya kirayi sunan ta cikin kausarsiyar murya, "Ke Nur!"

Juyowa tayi ta na kallon shi, Ido cikin Ido suke kallon Juna tsawon lokaci, zuwa can ya fesar da numfashi cikin sanyin murya ya ce "Idan Mamy ta dawo ki tabbatar kin gyara abin da kika bata, idan ba haka ba kuwa zaman gidanan zai gagare ki.

Har ya gama zancen bata cire idonta akan nashi ba, ganin haka yasa shi kara kafeta da ido "Au kin tsaya ne kin kafe ni da ido? Na lura baki san waye ni ba, ni mugu ne ki bar gani na haka, Kuma karki yi abin da na gaya din ki gani. Me yasa zaki min haka? Nasan har yanzun zaki iya tuna lokacin da nake goya ki a bayan nan nawa na kaiki kitso. Idan an gama haka zan goyoki har mu dawo gida kina min kuka, rigana haka ya ke baci da hawaye da majinar ki, har yanzun ina mamakin ta yadda akayi irin wannan maganar ya fito daga bakin ki, basan baki da kunya ba sai jiya. Ashe ke din fitsarriya ce, ni sa'an kine ko nataba wasa dake ne?"

Tunda ya fara magana a wannan karon tai kasa da kanta, bata sake dagowa ba har yazun da yake mata tambayan, tana jin yadda yake kallon ta tsayon lokaci,acikin ranta take jin kamar bata kauta ba duk da cewa ba shirri ta mishiba sai dan girmanshi da mutuncin sa da take gani, muryan shi ta ji ya ci gaba da cewa "Ina jin ki? Me na miki kika tsane ni?"

Can kasa ta yi da murya sannan ta ce "Ni ban tsane ka ba kafin jiya"

Kafar sa da ya daura kan daya ya sauke, sannan ya mike tsaye ya fara takowa inda ta ke, tsoro ne ke son mamaye Nur, saidai tana ta kokarin ta na jawo ma zuciyarta dakiya, a gabanta ya tsaya sannan ya ce "Kafin jiya baki tsaneni ba? A cikin mu waye zai sha wuya da daya ya tsana daya?" Kafada ya daga batare da ya jira amsantaba ya ci gaba da cewa Wannan matsalar ki ce, amman ina son in san dalilin da ya sa kika min haka?"

Kasa ta kara yi da kanta yayin da jikinta ya fara rawa. Tuna azabar marin da ya yan-yan ka mata a jiya, a kuma gaban Mamy, yau Kuma gashi babu Mamy daga shi sai ita. Ganin yana matsowa ta fara ja da baya cikin muryan mai Shirin yin kuka ta ce "Yaya Abdallah karka mare ni, hannun ka akwai zafi."

"Haba? Ashe akwai zafi? To kinajina? Da zaran Mamy ta dawo ki gyara abin da kika bata

jiya."

Kallo ya bita shi tsayon lokaci bata ce komai ba illa bugun zuciyarta da ke tsananta bugu, "Zaki yi abun da na ce ko baza ki yi ba?"

Mutsi ta fara da bakinta tsayon lokaci amman ta gaza furta komi, kula da hakan da yayi ya sa shi cewa "ina jin ki?"

"Yaya Abdallah cewa na yi Kaine ya kamata ka gyara ai"

Lumshe Ido ya yi zuwa can ya bude sannan ya ce "Shikenan, kijira abin da zai biyu baya, da kanki zaki gane maida ruwan rijiya ba barna ba ne, Kuma ke kin yi kadan ki ja dani, ki shirya ganin azaba, ukuba, zalinci, daga gare ni"

Zalinci Kuma? Nur ta yi tambayan tana me bude idonta a kanshi. Sosai take mamakin sauyarshi lokaci guda. Ayanzun gani take kamar wani ne aka sako ba waccen wadda ta sani a baya ba. Katseta yayi da cewa "Tambaya ki ke yi?"

Yadda ya zaro ido ya sata lumshe ido sannan ta ce "Yunwa nake ji zanje inci abinci."

Hannunsa ya mika ya dungure mata goshi, kasancewar ta yi dafda bango hakan ya haddasa mata kumewa da keya, koda ya ga kanta ya hade da bango ta baya be hanashi kara dannan goshin nata ba, yana kara gurza mata kai da jikin bango, kokarin rike hannun shi ta ke amman ya ki ba ta daman yin hakan. Yana kara dannan kannata yana fadin, "Kin yi kadan ki dagula min lissafi, idan har kina son ki zauna lafiya a gidan nan kibini sauda kafa, ki kuma gaggauta yin abun da na fada miki, idan ba haka saina bata miki jikin ki da tabban duka, kuma wallahi saina saki kinyi nadamar zuwan ki duniya, sai kin fada da bakin ki ince ina ma ba'a haliccekiba."

"Wayyo Yaya Abdallah ka sa ke min wuya na zan mutu."

Kara danna kannata ya yi yana fadin, Da na yi farin ciki, me ake da irin ki, ki mutu mana, bana son in karajin maganar ki anan gurin. Hannun sa ya sauke a goshinta sannan ya d'ana mata shi a baki, ya bada sautin d'ass, cikin sauri ta runtse idonta, zafin da taji har cikin tsakiyar kwanyan kanta, har yanzun bata iya dawo da kanta ba, saboda wuyanta da ya kage, dan haka tai saurin sa hannunta ta dafe bakin tare da son taji ko hakorin wanni bangaren ne ya fita.

Hannun da ta dafe bakin yai saurin rikewa ya juyashi zuwa bayanta, sannan ya kamo dayan ya juya shi ya bada sautin kas, a wannan karon ta gama barma zuciyarta ta karye kawai. Hakorinta kuma ya fita, ga wuyanta da ya makale, zufane kawai ke yanko mata ko ta ina, bata sake wani yunkuri ba domin zuwa wannan lokacin sama sama ta ke jiyo azabar da ya ke gana mata. Yana murdeta yana aika mata tambayan zakiyi abinda nace ko bazakiyi ba, saidai ita ba sosai take jiyoshi ba.

Zuwa can taji yayi saurin sakin ta, galabaita da rashin karfin jiki yasata zubewa a kasa, cak ta ji ya dagata a tunaninta jifa zai da ita, amman ga mamakinta sai tajita kwance saman lallausan katifa.

CIWON 'YA MACE
By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Muryarsa taji a saman kanta yana cewa, "Saura naga kafarki a falo"

Lumshe ido ta yi tana me jin kamar a wannan lokacin ne jinin jikinta ke sakowa, karan kofa ta ji sannan ta shiga jin muryan Mamy tana kwada mata kira, har sau uku ta ji ta kirata da ganan kuma ba ta sake jin kiran ba, bazata iya tantance iya adadin da ta dauka a wurin ba, bayan wani tsayon lokaci ta fara jiyo muryar mutanan gidan a falo, kanta dake mata nauyi ta dafe, daker ta iya daurewa ta tashi zaune, duk da cewa duk wuraren da ya yi mata mugunta radadi suke mata. Runtse idonta ta yi sannan ta mike tsaye, tun da ta mike bata kara sanin me take ciki ba, sai-dai jinta kawai ta yi rike gam a hannun mutum. Waigawa ta yi domin tasan waye ya ke rike da ita, Mamy ta gani tsaye, saidai tun kafin ta kai ga karantar fuskar Mamy ta jiyo muryar Abban su cikin fada sosai ya na cewa, "Mai ya yi zafi haka? Kina hauka ne? Ko tarbiyar da mu ka baki kenan?"

Jin irin furucin Abba yasa ta waiga ta kalli falon, fasassun kwalabe ta ci karo dashi barbaje afalon, yayin da Abba da Yaya Bashir suke binta da kallon mamaki, da ga can gefe ta hangi Yaya Abdallah zaune babu riga ajikin shi, yana ta duba damtsen hannunshi yayin da fuskarshi ke bayyanar da yana cikin tsananin bacin rai, muryan Abba ta sake ji yana cewa "Da ke na ke magana, wanne irin rashin d'a a ne wannan?"

Nan danan Nur ta kara rikecewa, cikin yanayi mai cike da nadama ta ce "Abba ka yi hakuri, bansan lokacin da nafito ba, a nan gurin kawai na ganni."

Kallon sosai Abban ya kare mata, sannan ya ce, "Ko da wasa kada irin wannan ya sake faruwa." hawayen da ya zubo mata tasa hannun ta share sannan ta ce "Toh Abba"

Hannu Abba ya daga mata alamar dakatarwa tare da cewa "Zo ki tsuguna ki bashi hakuri"

"Basai ta bashi hakuri ba domin nasan da abun da yai mata" Mamy ta fada ta na wa Abdallah kallon tuhuma.

Abba katse Mamy ya yi cike da fushi ya daga hannunshi yana cewa "Wannan be zama hujjaba, gaskiyar daya ce, ko an kita sai an bita za'a zauna lafiya." Cikin gamsuwa da maganar Abba Mamy ta saki hannun Nur, ahankali Nur ta fara takawa harta isa gaban Yaya Abdallah ta tsuguna, hade hannunta ta yi wuri guda tare da fadin, "Dan Allah ka yi hakuri."

Kamar jira ya ke ya mike tsaye batare da ya ce komai ba, rigarshi da ke gefen kujera ya dauka ya maida ita jikinshi sannan ya nufi hanyar dakinshi. Har yanzun Nur na tsugune bata motsa ba.

Ganin yana kokarin wucewa Abba ya ce, "Babana Nur ta na baka hakuri" Waigowa ya yi tare da sunkuyar da kanshi ya ce, "Bakomai Abba ya wuce"

Ya na shigewa hanyar da zata sadashi da dakinshi Abba da Yaya bashir ma suka fita, Nur kuwa zamewa ta yi tai zaman dirshen a wajen. Muryan Mamy ta ji ta ce "Tashi kije kicire kayan makarantar ki yi sallah sai kici abinci" Mikewa ta yi da sauri ta nufi daki kamar yadda Mamy ta ce haka ta yi, abincinne kawai ta ji sam bata sha'awarshi. Dan haka ta koma gado ta kwanta ruf da ciki, sai a yanzu ta cigaba da jin rikewar wuyanta da duk wani guri da Yaya Abdallah yai mata mugunta, da ga bisani ta shiga tuna irin fadan da Abba yai mata a yau, be taba mata hakan ba, a cikin ranta ta ce, ban kyauta ba sam. Hakan ba daidai bane, be dace ace ina fada dashi ba, kuma ba yau ya fara min hukunci ba. Mai ya sa zan mishi haka? Yana rike mutuncin shi, ko kadan bebar wata kafar da wani zai rainashiba, Yamin duk wani abu da ya kamata dan

uwa yayiwa yar uwanshi, kafin jiya Ina alfari da Yaya Abdallah, da wuya ya taba lafiyar jikina kafin jiya, mai yasa zan mishi haka? Duka na kai mishi ko jifanshi na yi ne ban sani ba. Tunawa da ta yi da lokacin da ya mike ya na maida rigar shi ya maido da ita da ga tunanin da ta tafi, afili ta ce, Dole Yaya Abdallah yayi fushi, dole ya kasa magana, abin akwai mamaki." Motsin da ta ji ya sa ta rike bakinta tare da kallon kofar, "Au kwanciya ki ka yi ba zaki fito kici abincin ba?" Mamy ta fada tana mika mata wayar hannun ta; tare da cewa Rahma ce"

Hannun Nur na rawa ta amsa kafin tasa wayar a kunnenta sai da ta ambaci Allah domin tun da Mamy ta ambaci Rahma gabanta ya yanke ya fadi.

Tana amsan wayar Mamy tafita tana cewa, "Ki na gamawa ki fito"

Wayar Nur tasa a kunnenta sai dai tsawon lokaci ta kasa cewa komai, acikin zuciyarta take ayyana sunan wadda za'a kira mata yau kuma, daker ta iya cewa,"Hello Rahma" Da ga can cikin wayar aka ce ce, "Yauwa Nur kinajina?"

Ajiyan zuciya Nur ta yi sannan ta ce "inajin ki"

"A cikin yan gidan ku waye baya gida?"

Wanni irin mummunan faduwan gaba ne ya sameta dan haka tasa hannunta ta dafe kirjinta tare da fadin, "Rahma mene ne kuma?"

"Ya na ga kamar a firgice ki ke?" Rahma ta fada ta na kallon cikin idon Nur.

"Bawai na firgita bane Yaya Bashir da Abba ne suka fita, su kadaine basa gida yanzu"

"Yauwa, zaki iya fitowa yanzun?"

"In fito in yi me? Rahma idan wani abu ki kajiyo a kan su kawai ki gayamini."

"A'a kizo dai kikagani da idonki shi zaifi"

"Kina ina yanzu?"

"Ina cikin gari yanzu haka, ke kadai nake jira"

Cikin rike cewa Nur ta ce, "Ai ya yi nisa bazan iya zuwa ba Rahma, Mamy bazata barniba, tun da ga nan Kabala har cikin gari? Tafiyan akwai nisa ki gaya min kawai mene ne?"

"Nur toh zan taho ki yi kokari mu hadu a makabarta yanzun nan"

Sauke wayar ta yi batare da ta iya amsawa ba, saukowa ta yi a gadon ta na tunanin yadda zata yi tabar gidan, hijjabin sallah ta dauka ta sanya sannan ta fito falon gidan, wata zuciyar ke bata shawaran ta fice kawai wata kila har ta je ta dawo Mamy ba ta fito ba, saidai ta kasa yin hakan sabo da rashin sabawa da fita ba'a sani ba, juyawa ta yi ta nufi dakin Mamy, ta na tura kofar ta gansu ita da Aunty Saratu da alama wata mgn su ke mai mahimmancin domin su na jin an turo kofar suka yi shiru tare da waigowa suka kalli kofar.

Cikin dakin ta karasa tare da kirkiro murmushi ta ce, "Mamy zanje gidan su Rahma in amso littafina"

"Zaki gidansu Rahma ku je gidan su Helen zakice mini, Kinga Nur ku raba kan ku da gidan yaron nan, domin wallahi miskili yafi mahaukaci banhaushi, na san ku gani ku ke besan me ku ke ba, toh bari kiji, na gaya miki ko be kalle ku ba ya na kare mu ku kallo ta gafen idonshi, ranar da ya gama raina wayonku, zakusha mamakinshi.

Duk da cewa Nur ta na cikin damuwa sai da ta yi dariya sannan ta ce, "Ba abun da zai mana Mamy, aishi jarabar shi akan Mama da Helen yake sauke ta, ko muna cikin gidan be ma kallon inda muke."

Aunty Saratu ce ta ce "Waye dama ya ce miki zai kalleku, shi da be kalli babba bare yara, ai Poul be da mutunci ko kadan, yaron da be wuce sa'an Bashir ba amman jira ya ke ka gaidashi."

Karaf Nur ta ce, "Aunty ko kin gaidashi ma baxai amsa ba, karake mgnr ta yi tana kallon Mamy sannan taci gaba da cewa "Mamy na tafi yanzu zan dawo" Mamy nabin bayanta da kallo ta ce "Ku dai bi ahankali wallahi.
"Cikin d'aga murya Nur ta ce "Mamy wallahi bacan zamu ba"
Aharabar gidan ta ga motar da Yaya Abdallah ya ke hawa, amma babu motar Abba kuma tare da Yaya Bashir suka fita, cikin sauri take tafiya, acikin zuciyarta take cewa,"Yau Kuma me zan gani da idona bayan jiya na ji mummunan labari da ga Rahma, a jiya na yi mugun ji yau Kuma zan yi mugun gani kenan? Koma mene ne nasan ba abun Alheri ba ne, idan ina ganin laifin Yaya Abdallah Yaya zan yi kuma idan idona ya gano min aibun wani bayan Yaya Abdallah, tsayawa ta yi cak ta na kallon gidan na su tsayon lokaci sannan ta ce "Me za'ayi agidan nan anjima bayan naje na dawo? In je ne ko kada na je? Rasa wadda zai amsa mata yasa ta kara kallon gidan sannan ta fice da saurinta.
Tana isowa bakin layin su ta tare me mashin tahau, saidai har suka dauki hanya kirjinta bebar dukan uku-uku ba, da ke mashi ne nan danan ta fara hango makabartan, dan haka ta shiga raba ido, a wannan lokacin duk ta manta da wani ciwo da jikinta ke mata, da ga can gefen makabartan ta hangi Rahma tsaye, tun da ga nesa take kare ma wajen kallo babu kowa tsaye a wajen sai Rahma sai tarin motocin da mashinnan dake wucewa. Agogon da ke daure a tsintsiyar hannunta ta duba, karfe 04:45pm ta gani, dago kanta yayi daidai da isowan su inda Rahma ke tsaye dan haka ta tsayar da me mashin din.
Sauka ta yi akan mashin din, sannan ta biya kudin, in da Rahma ke tsaye ta nufa tana me cewa, "Rahma men ene?"
"Ni yau sai na ga duk a firgice kike Nur, inason in kara nuna miki abu nagaba ne bayan wadda na gaya miki jiya, in dai kin amince da hakan?"
"Hmm na amince mana Rahma, ai ni tun da kika gaya min jiya na yadda, saidai na yi tsananin mamaki dan ba ma ni ba har Mamy ta yi mamaki sosai. Kuma ta yi mai fada sosai, ina sa rai hakan bazai sake faruwa ba, dan ya ji kunya sosai, harma ya rasa bakin magana, Sannan ciwon Mamy ya tashi adaren, hakan ya kara mishi damuwa sosai, abun na damun shi har yau, nasan zai gyara in sha Allah."
Lumshe Ido Rahma ta yi sannan ta ce "Yanzun kina son ki gannin ma idon ki ko kuwa?
Me zan gani?, Kina son kice min bayan Yaya Abdallah akwai Kuma wani me yin abun dabe dace ba agidanmu?
"Bance ba, ina magana ne akan shi Yaya Abdallah din."
"Me zaki nuna min to akan shi? Kin ga Rahma karki raina min hankali, abin ya isa haka, Yaya Abdallah kamilin mutun ne duk jama'ar unguwarmu zasu iya bada shaida akan haka, waccen ma ina kyautata zaton akasi aka samu, duk gidanmu bayan Abba babu me kamun kanshi, idan an kamashi da wani laifi bashi zai baki daman da zaki dinga yi kowanni irin magana akanshi ba."
Jikin Rahma a sanyaye ta ce "Ki yi hakuri Nur sabo da gudun irin wannan ya hana tun farko na gaya miki, yanzu ma dan na ga kin nuna kina son ki sani ne, Kuma ke kika bani damar sanar dake duk wani abu da zanji akan gidanku, Dan haka nasan wani abu kan Abdallah, amma tun da kince haka shikenan mubar kaza cikin gashin ta."
Baki Nur ta lashe sannan ta ce "A'a inajin ki?"
"Idan kin amince kizo muje naf club ki gani..."

"Ina ne haka?" Nur ta tambaya bayan ta tsurawa Rahma ido.

Daya ne da ga cikin wuraren shakatawa mafi kyawun otal a kaduna, naf club ya na da wurin shakatawa. Dakunan suna da kyau saidai suna kusa da mashaya, waje ne wanda wani lokacin ya ke zama da hayaniya musamman da daddare, abincin gurin na da kyau, akwai dakin motsa jiki, da filin wasan. Akwai zauren taro. kuma wurin gabaɗaya yana raye komai dare..."

"Ina ruwana da kyawun gurin ko rashin kyawunshi, ni kawai ki gaya min me zamuyo acan din?"

"Yaya Abdallah zan nuna miki."

"Rahma Yaya Abdallah ya na gida be je ko ina ba wallahi, can na baroshi a gida, bashi ki ka gani ba. Dan a gidama na same shi Kuma har na fito dinan ya na gida."

"Shine Nur, baya gida, kuma idan kinzo munje zaki tabbatar da hakan."

"Shikenan muje" Nur ta fada tare da tare me keke, shiga suka yi tare da gayawa mai keken in da za su, Ko da suka kama hanya babu me ma wani magana.

Misalin karfe 05:10pm su ka sauka agaban shararren Otal din, Rahma ce agaba Nur na binta a baya, tafe take tana waige-waige sabo da rashin sabo da shiga irin wannan wajen, Rahma ko ajikinta ta kama hanya tiryen-tiryen ya yin da Nur ke daura kafarta a in da Rahma ta cire tata, bayan sun shiga harabar wajen ne kuma suka rasa hanyar da zasu bi, da ga can babban kofar da tazamo nanne mashigar gurin suka hango maza da mata suna fitowa, dan haka Rahma taja Nur su ka boye a bayan wata mota, cigaba suka yi da kallon masu fitowa da ga ciki tsayon lokaci domin gudun cin karo da idon sani, ganin kowa na harkokin shi wasu na shiga wasu na fita ya sa suka fito daga bayan motar.

Nur ce tabi wajen da kallo sosai, tun da ta ke bata taba zuwa irin wannan wajen ba, tsoro ne karara akan fuskarta yayin da yanayin ta gaba daya yake cike da daburcewa, musamman ganin da ta yi ita kadaice aduk wurin take sanye da zunbulelen hijjabi har kasa, kallon Rahma ta yi gyale ne ajikinta, haka duk mutanen da suke wajen ko kusa babu me shiga irin tata, dagowa tayi ta kalli Rahma ta ce, "Rahma mubar wajen nan be dace damu ba"

"Ki Bari mu shiga ciki ki gani."

Gaskiya ni bazan iya shiga ciki ba, hannunta ta dago ta kalli agogon batare da ta ce komi ba ta fara tafiya ta nufa hanyan ficewa daga Otal din, sauri take yayin da Rahma tabi bayanta tana Kira "Nur! Ki tsaya mana."

Jin wata murya ta kira yi sunanta wadda ba na Rahma ba yasa ta ja ta tsaya cak, namiji ne ya kirayi sunan nata sai dai ta rasa gane ko wanene dan haka ta waigo da sauri.

Ido hudu suka yi da Auwal, abokin Yaya Abdallah ne kut da kut, kallo take kare mishi kamar yadda shima yake kare mata kallo, ganin yadda ya ke kallon ta ya sa tai saurin kallon jikinta.

"Me kike anan gurin Nur?"

Cike da kidemewa ta ce, "Babu komai" tafiya ta fara dan haka ya ce, "Zonan!"

Nur na jin haka ta cire takalmanta ta kwasa a guje, ganin haka Rahma ta rufa mata baya tana me kiran sunanta, saidai ko da wasa Nur bata tsaya ba. Aguje ta nufa titin tana kokarin tsallakawa, shiko Auwal kiran sunan Nur ya ke tare da bata Umarni tsayawa, amman ina Nur gudu kawai take.

Tsintan kanta ta yi dirshen zaune akasa, a wani layi me shiru sosai wadda bata iya banbance ko inane, layin ta kalla babu kowa sai gidaje masu dan karan kyau, cikin sauri ta mike ta fara tafiya, banda haushin karnuka babu abun da take jiyowa cikin unguwar, dan haka hakalinta ya

kara tashi, kokarinta kawai ta ga titi domin ta samu motar unguwar su, ganin ta yi tafiya me tsayo bata samu babban titin da zataga motocin haya ba ta fara zubar da hawayen dana sani. Da ga bayanta ta ji tahowan wata mota da mugun gudu, cikinta ne ya kara murdawa domin ko tantama ba ta yi ita ake bi da motar, yin wannan tunanin ya kara sata diriricewa tare da ja da baya tana kallon motar domin daf take da ta isowa gareta

CIWON 'YA MACE

By

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

https://www.wattpad.com/user/fadeelalamido?utm_source=android&utm_medium=link&utm_campaign=invitefriends

Page 5-6

Kwasa ta yi a guje, duk da gudun da take bata daina waiwayen bayantaba. Mamakine ya kamata a lokacin da ta ga motar ta wuceta batare da ta tsaya ba, cak ta tsaya tare da sakin a jiyan zuciya, acikin zuciyarta take cewa, "Ashe bani suke bi ba, Allah na gode maka, ina Rahma ta tsayane? Ni ta ina zanbi in koma gida? Na shiga uku" Irin wannan sake-sake take har ta samu ta fito bakin titi, duhu mangariban da ta gani ya kara daga hankalinta, tsoro da tashin hankali ya hanata tunawa babu takalmi a kafarta, tun da ta fara tafiya a unguwa ko motar haya daya bata cin karo da ita ba, illa zafafan motocin da suke wucewa jefi jefi wadda bata iya hangen mutanen dake ciki.

Zuwa can ta fara hango titi, wanni irin nannauyan ajiyan zuciya ta sauke duk da cewa bata da kudin mota, sauri ta kara har ta isa bakin titin ta tsaya, ga motocin hayanan burjik suna wucewa saidai kowacce a cike take zuwa, wannan ya Kara daga hankalinta, kusan minti talatin ta dauka awajen sannan ta kula da wata mota dake dawowa da baya, matsawa ta yi domin bawa motar wurin fakawa, ahankali har motar ta iso daidai inda take, kallon motar ta yi sosai, tunani ta shi yi domin tuna inda tasan motar, saidai duk iya tunaninta ta kasa tunawa, wannan yasa ta kasa cire idonta akan motar.

Tsaye motar take tsayon lokaci ita bata wuce ba kuma kuma babu wadda ya fito daga cikin ta, zuwa can aka bude motar ganin haka tasa ido sosai, wata kyakyawar kafa ta hango cikin hadeden takalmi aka aje a kasa, kafin aka dauko dayar acikin zuciyarta tace "Wannan ba Yaya Auwal bane Sam, duk da cewa shima dan gaye ne amman ko kusa wannan ba kafarshi bace, waye wannan ta sake fada acikin zuciyarta, wani irin daddadan murya ta ji tana cewa "Me kike yi anan?" Dan haka ta dago da sauri ta kalli fuskar mutumin da ke tsaye a gabanta, wanni irin faduwa gabanta ya yi dan haka tasa hannunta ta danne kirjinta, tunda na ke be taba mata magana ba, "Dama Ya sanni?" Nur ta fadin haka cikin zuciyarta, a afili kuwa yawu ta hadiye tare da mikewa tsaye tana karkade jikinta tare da kokarin barin wajen, "Ina zaki? " Mutumin dake tsaye agabanta ya fadi bayan ya tsareta da ido, ba ta iya amsa mishi ba illa kokarin

wucewa da take yi.

"Ke! Bakijin ina magana ne? Tsaya na ce!"

Tsintan kanta ta yi da tsayawa cak tana satan kallon fuskan shi.

"Daga Ina kike haka?"

"Gida zani"

"Cewa na yi da ga ina kike?"

Yadda ya ke maganar cike da karfin guiwa ya sata tuna zancen Mamy kafin ta fito daga gida, acikin zuciyarta ta ce, "Dama mamy ta ce Poul yana sane damu gashi kuwa, ni bantaba tunanin zai iya shaidani ba saigashi ya shaidani duk da cewa acikin duhu na ke, kenan idan nai wasa ma yana iya samin dukan kamar yadda Mamy ta ce." Yin wannan tunanin ya sa ta dago ta kalle shi, ido su ka hada dan haka tai saurin sunkuyar da kai. Murya kasa-kasa ya sake cewa ina takalminki?

"Kallon kafarta ta yi sannan ta ce, Na baro su acan."

" Can Ina?"

Wannan karon kanta ta sunkuyar dan haka ya wuce ya bude motar tare da fadin "Shiga mu je" A wannan lokacin kasa musu ta yi domin wannan shine kadai mafitar ta, don ko tabarshi ya tafi batasan hanyar da zatabi ta koma gida ba; asali ma bata da kosisi.

Motar ta shiga ta zauna sannan ya rufe ya zagaya ya shiga motar, kallo daya yama Nur ya tada motar, tun da ga lokacin be sake kallon inda take ba, i ta ko Nur mamakinsa ne ya sa ta kallonshi domin bata iya tuna rana daya daya dago ya kalli idonta dahar zai ganta a hanya ya shaidata, satan kallon shi take sosai abin ke bata mamaki a zuciyarta ganin abun take kamar mafarki, tafiya suka yi mai tsawo sannan ta fara gane hanya, kasa-kasa ta yi da murya ahankali ta ce "Anan zan sauka."

Ko motsi beba bare ya nuna ya ji ta, gudu kawai yake yi akan titin.

Ganin ya yi banza da ita ta juyo ta na kallon window motar sannan tai saurin juyawa ta sake cewa, "Anan zan sauka, ina son inje gidan Ummy ne ta rakani gida, idan na koma ni daya za'a min fada."

Wannan karon ma ko motsawa be yi ba illa kara tamke fuskarsa da ya yi.

Gani ta yi ya koma Poul dinshi sosai, yanayinsa da da zubinsa yafi kama da na yaran manyan malamai hakama shigarsa da kasunbarsa, yafi Yaya Abdallah da duk mazan da ta sani yin shiga ta mutunci irin na cikkkun Hausawa haka kuma ya na da Hausa radam a bakinshi, amman kash bashi da mutunci ko kadan, duk da cewa ya mallaki makudan dukiya tare da manyan motoci amman rashin kirkishi yasa besan ta yadda zai kashi kudin su amfane shi ba, tsaki taja afili batare da tasan lokacin da ta sakeshi ba, sabo da tsabar takaicin halin shi, duk da cewa ita bata yii tunanin ma ya santaba bare har ya iya shaidata amman ita tasanshi farin sani, bawani bane Poul ne yayan Helen mai share jama'a tare da sha musu kunu. Ta gafen idonta ta saci kallon shi, wannan kallon ya kara mata nutsuwa sosai domin fuskarsa kawai ta tabbatar mata da babu wasa kuma bazai taba sauraranta ba, dan haka itama ta gyara tata fuskar tare da tunanin yadda zata tunkari Mamy ita daya a wannan daren. Babu abin da motar ke yi sai zuba kamshi duk da cewa gudu sosai ya ke amman tankar suna tafiya sama babu gargada sam, sosai Nur ta kosa ta sauka a motar sabo da tsabar kyamarsa da ta ke ji.

Daidai kofar gidan su Nur Poul ya faka motar shi bayan sun iso, kokarin bude motar Nur ke yi ta hango su Abba na tahowa. Yaya Abdallah da Yaya Bashir suna biye dashi abaya da alama

da ga masallaci su ke, dan haka tai saurin komawa cikin motar ta zauna tana satan kallon su, hannun ta daya na rike da murfin motar.

Muyarsa taji cikin bada Umarni ya ce, "Fita!"

Da sauri ta kallishi tare da fadin, "Ina zuwa dan Allah bari su Abba su shiga gida"

"Fita nace na ce!"

"Ka yi hakuri su Abba su shiga gida"

"Fitan min amota!" Ya sake fada tare da zare mata Ido. Wanni irin kallo tamai sannan ta ce "Baza ka bari su shiga gidan ba?"

"Eh bazan Bari ba ki fita, sauri nake"

Wanni irin ajiyan zuciya ta yi tana rike da murfin motar saidai ta kasa budewa, gani ta yi ya rankwafo ya hankada murfin motar ta bude gaba daya dan haka ta zare ido tare da binshi da kallon mamaki, su Abba kuya yadda aka hankado murfin motar shi ya jawo hankalinsu suka dawo da hankilinsu wurin, Poul kuwa hannu ya daga da alama hankadata ya ke shirin yi dan haka tai saurin ficewa cikin motar batare da yin wani tunani ba,  hannun sa ya rufe motar da karfi sannan ya figita ya wuce abun shi.

Gaban su Abba Kawai ta ganta batare da tasan lokacin da taje ba, suma din cike da mamaki suke kallon ta, mamaki karara a fuskan kowannen su, sunkuyar dakai ta yi yayin da zufa ke yanko mata ko ta ina, domin tasan Abba baya wasa kuma ba a masa karya ko kauce-kauce, duk wayon ka duk dibaran ka kanayin magana yake gane inda ka dosa.

Jin shirun yayi yawa ta dago ta ta saci kallon su, gani ta yi su Yaya Abdallah na kallon Abba yayin da shi Kuma Abba ya kafe ta da ido, sosai yake kallonta dan haka ta ji kafafuwanta sun gaza daukanta, durkushe ta yi ta zauna akasa.

Zuwa can Abba ya gyada kai juya yayi ya  shige gida tare da fadin "Bashir dauko min yariyar nan."

Amsawa yayi da toh, sannan yai tsaye har Abba da Yaya Abdallah suka shiga gida, ahankali Yaya Bashir ya ce "Mike"

Babu misu Nur ta mike yayin da Yaya bashir ya bi bayanta yana cewa, "muje"

Tafiya take tana waiwaye har suka shiga cikin falon.

Mamy naganin shigowanta ta ce, "Ke Kuma da na ce miki kiyi maza ki dawo shine kikai dare, ita Kuma hajiya Salma ta barki har wannan lokacin?

Lumshe Ido Nur ta yi tare da kallon cikin idon Mamy ta ce "Na fito da wuri wasu ne suka biyo ni har na bace nara inda zanbi indawo gida"

Abba ne ya ce "Ku saurara min, kenan ke ce kika turata gidan Salma?

"Ita ta ce zata Alhaji"

"Ke Kuma kika bata dama?"

Shiru Mamy ta yi dan haka Abba ya ce "Dake na ke magana."

"Eh" Mamy ta fada tana kauda kai.

Shiru Abba yayi tsayon lokaci, zuwa can ya kalli Nur ya ce, "Waye ya sauke ki a mota?"

"Yayan Helen ne" Nur ta fada tana wasa da yatsunta. "Aina kuka hadu?"

Wannan karon Saida hawaye ya zubo mata sannan ta ce "Abba bansan sunan gurin ba"

Lumshe ido Abba ya yi sannan ya bude su a kanta tare da sake jefa mata tambaya "Ina takalmin ki?"

Kasa magana ta yi tsayon lokaci dan haka Abba ya mike Yana fadin "Bashir kabawa  yariyar

nan kashi"

Mikewa Nur ta yi tana cewa "Abba dan Allah ka yi hakuri saidai be ko juyo ya kalletaba ya fice abinshi.

Yaya Bashir ne ya zagoyo ya zauna falon yana cewa, "Nur me yasa bakyajin magana, dazon nan fa kika yi laifi fushin be saki Abba ba amman kin sake yin wani, duk kinbi kin canza kamar ba ke ba"

"Yaya Bashir ka yi hakuri kaba Abba hakuri dan Allah" Nur ta fada tare da share hawaye.o

"Zaneta a kace ka yi ka wani tsaya kana lallashin ta" Ya Abdallah ya fada Yana zafgawa Nur harara.

"Yaya mu rufa mata asiri dai sai in ta kuma tunda Abba ya fita"

Tsaki Abdallah yaja tare da mikewa yana kokarin kwance bel din dake daure ajikinshi, Mamy ce ta kalle abin da ya ke kokarin yi dan haka ta ce "A'a karka taba ta, mikewa ta yi tana cewa ke Nur muje daki"

Akofar dakin Nur Mamy ta tsaya itako Nur ta na sauke ajiya azuciya ta shiga cikin dakin, cak ta tsaya dalilin hango takalmanta saman gadonta juyawa tayi ta kalli kofa da alama watso su aka yi, cikin sauri ta kwashe ta boye gudun kar Mamy ta gani,sosai taji damuwanta ya karo, hijjabi ta cire sannan ta shiga bayi tai wanka tare da daura alwala tana fitowa tai sallah, bayan ta idar kwanciya ta yi domi bazata iya cin komai ba, tunani kawai tai ta yi da sake sake har bacci ya sace ta, washegari ma bata fitaba saida ta gama shirin ta tsaf, sallama taima Mamy ta wuce makaranta sai dai ko tantama bata yi Mamy ma ta yi fushi da ita dan haka take jinta tamkar mara lafiya.

Gaba daya duniyar jinta take ta canza mata komai ya cakude mata, yau ce rana ta farko da taki biyama Helen domin haushin yayanta da take ji sosai ya shafi Helen din.

Har aka tashi makarantar bata wani saki jikintaba, ita da Helen din suka jero kamar yadda suka saba, saidai akwai alamar itama Helen din cikin damuwa take.

Bayan Helen ta shiga gida Nur ta harari gidan tare da Jan tsaki, tsintan kanta ta yi da cewa a fili, "Da wannan dauko ni din da ka yi har gara ace ka barni inda ka ganni" tsaki ta Kuma ja tare da kara sauri domin idan tana ganin gida ji take kamar yanzun ne ya ke mata abun da yayi jiya.

*****

Nur ce zaune ta na cin abinci, shigowan Mamy tagani dan haka tai saurin tsame hannunta cikin abinci; jikinta a matukar sanyaye.

Gefenta Mamy ta zaune, sannan ta zuba mata idon tana kallon ta tsayon lokaci, Nur kuwa tuni cikinta ya duri ruwa saboda tsabar firgicin da damuwan domin taji ajikinta Many fada zata mata akan lefinta na jiya. "Nur!"

Can kasan makoshi Nur ta amsa. "Nazo in yi magana dake ne kuma gaskiya nake son ji karki kuskura kice zaki gaya min karya" Ahankali Nur ta ce "Toh Mamy"

"Jiya ina kukaje ke da Rahma? Dan na tura gidan akace Rahma batanan ke kuma bakizoba"

Idon Nur akasa tana wasa da hannunta ta kasa cewa komai.

"Dake nake magana fa?" Mamy ta sake fada bayanta tsare Nur da Ido.

Ahankali Nur ta ce "Mamy Rahama ce ta kirani awaya"

"Eh, ai na sani, bani na kawo miki wayar ba? Yanzun cewa na yi ina kukaje?"

"Can wajen makabarta muka hadu Mamy" Kara sunkuyar da kanta ta yi tana tunani ta ina zata fara ne mawai

Mamy ce ta sake cewa "Ina jikin ki, ki bude baki ki mini magana mana"
"Mamy Rahma ce ta ce mini in zo inga Yaya Abdallah"
Lumshe Ido Mamy ta yi sannan ta ce "A ina?" "Wani Otal ne wai sunan shi Nafclup"
Wani irin faduwan gaba ne ya samu Mamy daker ta dago ta kalli Nur ta ce "Can ku ka je?" Wannan karon da kai Nur ta amsawa Mamy.

Kara sunkuyar da kai Nur ta yi, tsayon lokaci ta dauka tana jiran jin muryan Mamy amman shiru dan haka ta dago ta ta saci kallonta, sosai ta ji gabanta ya fadi ganin inda hawaye ke gudu akan fuskar Mamy dan haka ta dago sosai tana kallonta.

Ganin Nur ta dago tana kallonta ya sa ta fara share hawayen tare da cewa "Kina jina ko Nur, karki kara zuwa wani waje da nufin bin Abdallah, zuwan ki babu abun da zai amfanar illah zubar mana da mutunci, asalima kin yi kankanta a dinga ganin ki a irin wannan wajen, shi din ba danki bane, ya na sama dake ne, ko mu da muke iyayenshi sai dai mu gaya mushi gaskiya amman bazamu bibiyeshi ba bare har mu kai mishi duka, Jiya kinban mamaki gaban kowa kika fito kina jifanshi da kofuna duk irin tsawan da ake miki baki saurari kowa ba, jifanki nasamun shi ya fadi kasa kofin ya bashi kikacigaba da daukan kina jifanshi har saida aka rike ki Nur, har yau da safen nan saida Bashir ya cire kwalba ajikinshi, sama kike dashi da zaki mai hukunci?"
Cikin sauri Nur ta girgiza kai sannan tai kasa da murya ta ce "Mamy wallahi bansan lokacin da nafara ba ni dai kawai ganina na yi rike hannunki, Amman Mamy kafin ku dawo shine ya min duka afalon nan ya murdemin hannu yaita gana min azaba"

Jimmm, Mamy ta yi idonta akan Nur zuwa can ta ce "Kin mishi wani abu ne?"
"Ba abin da na mishi ina dawo makaranta ya tareni yaita hadamin kai da bango"
Ajiyan zuciya Mamy ta yi sannan ta ce "Idan ya sake miki irin haka karkice komai kawai ki gaya mini, amman duk abin da zakiji akanshi karki sake binshi wani waje. Koda wasa banson in karaji, Abdallah ba karamin yaro bane, ki barshi kawai kowa ya gyara ya sani haka kuma kowa ya bata ya sani, ki daina tunanin zaki iya canza komai, kuma banda abinki Nur lokacin da kika fita ai Abdallah yana gida shina tura gidan su Rahma nemanki danaga kin jima baki dawoba."

Cike da mamaki Nur ta ce, "My to waye ya dawo min da takalmana gida, acan fa na bar takalmina amman ina shiga daki na gansu a kan gadona"

Jimmm Mamy ta yi zuwa can ta ce, "Ai banki ta takun ba Nur, amman ai ansan da wuyan biri ake daure shi a kafa, dan haka karki sake binshi, Rahma ma karki sake sauraronta" Amsawa Nur ta yi da to sannan Mamy ta mike tana share hawayen ta fice adakin.

Nur ma mikewa ta yi jikinta a matukar sanyaye, hannunta ta wanke sannan ta zauna a bakin gado cikin zulkumi da tunani, sosai take son ta ga komai ya gyaru, Sam bata son irin wannan matsalar a gidan su. afili ta ce, yanzun kenan babu yadda za a yi da shi ya bari? haka za a zauna ana kallon shi? wani irin zafi ta ke ji a zuciyarta mara misaltuwa sosai take jin zuciyarta na mata kuna afili ta sake cewa, "Mataki ya kamata su Mamy su dauka, idan kuwa ba haka ba bansan ranar da zuciyata zata daina min zafi ba, ina ma ace nice Babba agidan nan, wallahi da daga yau Yaya Abdallah bazai sake fita ko kofar gida ba. Sallah ma ya daina bin ta a jam'i, Tsaki taja tare da mikewa tana tunanin ta yadda zatabi ta share lamarin Abdallah kamar yadda Mamy ta fada.

Misalin Biyar na yamma Nur ta fito ta zauna afalo tana yanke farce, ganin babu motsin kowa a gidan ya sa ta shiga kwalawa Mamy kira, da ga can cikin kitchen taji muryan Aunty Saratu ta na cewa "Ka da ki tadata tasha nagani ta kwanta batajin dadi"

Jimm Nur ta yi ta na tuna hawayen da Mamy ta yi dazon, sosai ta ji damuwanta ya karo domin tasan mgnr dazon ita ta tada ciwon Mamy, tun daga lokacin ta shiga tunane-tunane ba ita ta dawo cikin hankalinta ba sai da taji dawowan su Abba. Sallah magarin da ake kira ya sata mikewa, dakinta ta nufa tai alwala tai sallah sannan ta ci gaba da aikin tunani. Tana cikin wannan yanayin tajiyo muryan Aunty Saratu ta na kwala mata kira. Amsawa ta yi tare da mikewa ta fito falon tana fadin "Aunty gani" "Abban ku na kira"

Cikin sauri Nur tasa hannunta ta dafe kirjinta domin in dai Abba yai kira to wani abu ne me mahimmancin, kofa ta nufa batare da ta sauke hannun da ta dafe kirjin dashi ba, sashin Abba ta nufa gabanta na tsanta faduwa. A kofar falon ta tsaya ta sauke hannunta a kirjinta ta na me karanto addu'oi, yadda take juyo muryan su Yaya Abdallah da Yaya Bashir acikin falon ya kara daga hankalinta.

Da Sallama a bakinta ta shiga falon duk dagowa su ka yi suka amasa sallaman nata cikin sakin fuska, amman banda Abdallah da Abba da su ka hade fuskokin su. Baffa ta hanga daga gefe dan haka taji gabanta ya sake faduwa

Fadila Lamido
CIWON 'YA MACE

By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

https://www.wattpad.com/user/fadeelalamido?utm_source=android&utm_medium=link&utm_campaign=invitefriends

Page 7-8

Zama ta yi a kasa ta na gaida su, sai dai yadda ta ga sun amsa cikin sakin fuska ya sa ta ji nutsuwa kadan. Shiru falon ya yi tsayon lokaci, zuwa can Baffah ya ce "Nur ya karatu?"
"Lafiya lau Baffah"

"Karatun ne lafiya lau? Alhamdulillah za ki ce" Bashir ya fada ya na kallon fuskar Nur yana dariya. Baffah ma murmushi ya yi yana kallon Nur din ya ce "Ina labarin saukan ki"
"An kusa Abba saura kwana arba'in da hudu yau"

"Allah ya nuna mana lokacin" Baffah ya fada cike da farin ciki. Abba ne ya yi gyaran murya wadda ya sa duk wani dake cikin dakin maida hankalinsa kanshi, sosai Baffah yabi Abba da kallo bayan tsayon wani lokaci sannan Abba ya ce, "Dama na yi kiran ka ne akan Nur" Cikin Sauri Baffah ya kalli Nur sannan ya juya ya kalli Abba ya ce "Me ke faruwa ne?"
"Ina son ne ka tambayeta me take so?"
"Ban fahimce ka ba Alhaji?" Baffah ya fada tare da gyara zamanshi, shima Abba gyara zama ya yi sannan ya bude murya sosai yace "Gani na yi ta girma, wata kila akwai wani abun da take so, kasan akwai wasu shekaru wadda yariya ke kawai ta dinga ji ajikinta daidai take da kowa, Nur tana cikin irin wannan shekaron duba da yanayin dabi'ar data da data yanzu ba iri daya

bace" Sosai hankalin Nur ya tashi saidai har yanzun bata gane inda Abba ya sa gaba ba. Yaya Bashir kuwa shuru ya yi tare da sunkuyar da kanshi kasa, shikuwa Yaya Abdallah har yanzun wayarsa ya ke dannawa kamar besan me a ke yi ba.

Juyawa Baffah ya yi ya kalli Nur sosai cike da hade fuska,

Shiko Bashir satan kallon Baffah ya fara tare da mamakin furucin Abba. Cikin kausasiyar murya Baffah ya ce Nur me ke faruwa kwana biyu?

Kasa Nur ta yi da kanta tare da yin kwalkwal da idon ta. Ganin haka Baffah ya sake cewa "Inajin ki gaya min me kike so?"

Can kasa tai da murya sannan ta ce "Ba komai Abba"

"A'a ki bude baki ki yi magana, kina son aure ne?"

Cikin tsananin furgici Nur ta dago kai tare da fadi  "Wallahi a'a."

"Eh mana idan ba hakaba me yasa baki da nutsuwa?"

"Baffah wallahi ban yi komai ba, yayan Helen kawata ne ya dauko ni jiya a hanya ya ganni, lokacin na rasa in da zanbi inhau motar da zan dawo gida" Abba ne ya katse Nur cikin fada ya ce "Yau ki ka fara zuwa gidan Salma dahar zaki mance hanya? Yarana maza basu bani wala wajen tarbiyan su ba dan haka ke mace bazaki walar dani ba, duk da cewa na so ace kin yi karatu sosai amman idan babu dama aurar da ke zanyi in huta, don ina son ki karatu bazan barki ki lalaceba"

"Dama ya fi Abba, amata aure kawai, idan ma karatun ne ta yi shi a dakin mijinta" Abdallah ne ke  fadin haka cike da nutsuwa. Cikin Sauri Bashir ya ce, "Nur din za'a ma aure? Haba Abdallah"

"Idan ba ta natsuba ba dole a mata aure, koko sabo da muna son tai karatu sai mu barta ta lalace?"

"Ai Abba karatun ma be da wani amfani, a mata aure kawai, ko an barta ta yi karatu karshen ta dai aure za ta yi, karatun ba wani amfani da zai yi mataba, dan mafi yawancin mazan basa barin mace ta fita aiki bare wannan yariyar da bata jin magana"

Cikin bacin rai Bashir ya ce "Ko mace bata fita aiki ba Karatu dole zai mata rana ko wajen tarbiyan yaranta ne."

Gyara zama Abdallah ya yi sannan ya ce "Wadda ta yi yanzun ya isa tabawa yaran na ta tarbiya"

Ta gefen ido Nur ta saci kallonsa, cikekken mutum managarci me cikar zati da haifa, ga kasumba cike da fuskarsa kai kace na Allah ne, acikin zuciyarta ta ce, "Yaushe ya tsane ni har haka? kawai dan nafada gaskiya sai ya bada shawaran amini aure?" Muryan Baffa ne ya dawo da ita cikin hakalinta, dalilin jin da ta yi yana cewa "Gaskiya ne Abdallah da ace ta lalace gara amata aure shiyasa akoda yaushe nake yaba hankalinka, tunaninka irin na manyane"

Fashewa Nur ta yi da kuka ta na cewa "Wallahi ban son aure Abba, ni karatu zan yi, wallahi bantaba yin irin wannan tunanin ba, karatu na ke so,  yayan Helen ne ya kawoni gida, kuma aje a tambaye shi"

"Ke dallah rufewa mutane baki! Baffa Karku saurareta, karatun da ta samu yanzun ya isa ta kula da yaranta, aure shi yafi dacewa da ita, idan aka barta haka wlh za ku yi da kun sani"

"Ni badan in kula da yara na ke son in yi Karatu ba, ba na son aure sam, karatu zan yi abba kum..."

"Ke! ina wasa dake ne? Dake nake Magana?

Shiru Nur ta yi tare da sa hannun ta tana share hawaye. Abba ne ya ce, "A baya nasan kudirin Nur na son Karatu, dacan ta taba cemin likita take son ta zama, ina shiga farin ciki aduk sanda ta gaya min kudirinta, kuma na yi mata alkawarin ko nawa ne zan kashe mata ta yi karatu, amman kwana biyun sauyawan nan nata ya daga min hankali, daren jiya ban iya runtsawa ba."

Bashir ne ya ce "Abba ai mata hakuri dan Allah, yariya ce, wata kila ta na da wani damuwa ne kwana biyun zan yi mgn da ita inji"

Tunkafin Abba ya amsa Abdallah ya cigaba da danna wayarsa, sai dai har yanzun fuskan sa a hade ta ke, Baffa ne ya yiwa Nur fada sosai sannan ya ce ta wuce.

Mikewa ta yi tai godiya sannan ta koma cikin gida tana share gutun hawaye, kai tsaye shashin Mamy ta wuce. Akan sallaya ta samu Mamy jikinta ta rakube tare da shashshekar kuka tare da fadin "Mamy kinga ya Abdallah ya na bawa Abba shawaran abin aure ko?"

Gyara zama Mamy ta yi ta kalli Nur sosai tare da cewa "Auren lafiya? babu me miki aure yanzun, nasan abun da ya sa Abban ku zaice haka, tun da besan meke faruwa ba a gidan, kema nace miki ki kwantar da hankalin ki..." Shigowan Yaya Bashir ya hana Mamy karasa zancenta, zama ya yi gafen su ya na kallon yadda Nur ke kuka sannan ya ce, "Mamy wai me ke damun Nur ne, a rikice ta ke fa, yanzun gashi har Abba ya kira Baffah wai gani ya ke aure take so?"

Tsaki Mamy taja sannan ta ce, "Wanni irin aure, Nur fa duk wannan abun da kuke ganin tana yi ita da Abdallah ne, Kuma na gaya mata ta rabu dashi baza ta iya ba, kowa ya gyara ya sani haka kowa ya bata ya sani."

Cikin rashin fahimta ya ce "Me ya ke faruwa ne Mamy?"

"Bashir babu abun da be faru ba, ko wanne mutun da irin halin shi, na lura Yayan ku riga biyu ya ke amfani da ita, azari mutum me mutunci acikin zuci kuma shi kadai yabarwa kanshi sani, idan Yayan ku ya na yin abin da bedace ba Nur ba ta isa ta canza Shiba dan haka banga amfanin damun kanta da take ba, ni kaina saidai in gaya mishi gaskiya in kuma nemar masa shirya gurin Allah."

Shigowan Abdallah ya sa duk suka kalli kofar, cikin dakin ya shigo ya zauna, babu wadda ya yi magana shikuwa Abdallah kallo ya bi Nur dashi cike da tsana, ayanxun ji ya ke babu abun da ya tsana sama da Nur a duniya. Acikin zuciyar shi ya ke cewa, "Idan har ki na son zama lafiya dole ki gyara abun da kika bata, idan kuwa ba haka ba dole acikin biyu za'ayi daya kodai ki bar gidan nan ko kuma auren, dan bazan taba barinki ki zauna acikin gidan nan kina Karatu ba." Dawowa yayi da ga duniyar tunanin ya kalleta saboda tsabar haushinta ji yake kamar yasa kafar sa ya latseta, mikewa yayi ya fice batare da ya bari kowa ya fahimci halin da yake ciki ba.

Misalin Karfe 8 na dare Aunty Saratu ta gama hada abincin daren akan babban teburi da kowa ke halarta kowanni dare, kira ta kwalawa Nur bayan ta fito ta zauna ta na jiran fitowan sauran, saidai aunty Saratu na wucewa ta hango Yaya Abdallah na tahowa, bata ji komai ba domin sun saba irin wannan zama, kujara ya jawo baya sannan ya zauna akai, tunda ya zauna take jin kamar idon sa na kanta, tsayon lokaci su ka dauka amman taki kallon sa, dan ta na ji a jikinta kallo ne irin na tsana yake mata, zuwa can Mamy ta fito saidai bata karaso ba can falon ta zauna ta ce akawo mata nan, aunty Saratu ce ta deba na Mamy ta nufa kai mata, juyawanta ya yi daidai da lokacin da Abdallah ya ce, "Idan har ina numfashi babu karatun da zaki yi, wallahi summa tallahi bazan taba bari kisamu abin da ranki ke so ba, a haka ma kina neman ki yi mana tsayayya ina ga kin yi karatu? Ki na kara girma agidan nan sai mun rasa inda zamu yi

da ke."
Kin dagowa Nur ta yi bare ta kalleshi, dan haka ya sake cewa, "Kina ji da wani dan baki dan curr kamar na tsuntsu, abu daya ya rabaki da sadar fulani, shegiya magananna, sai kinbar gidan nan tunda ba gidan ubanki bane!"
Cikin Sauri Nur ta dago ta kalli Abdallah sam bazakace daga bakinshi wannan zantukan suke fitowa ba, ganin in da ta ke kallon shi  yasa shi ya miko kafarshi ya mutsuke na ta, tare da fadin "Zaki rama ne?"
Cikin Sauri ta girgiza kanta tare da cewa "A'a akwai zafi dai, ka daga min kafa"
"Idan har ki na son ki zauna lafiya kibar gidan nan, idan Kuma kin ki burinki bazai taba cika ba, kin yi kadan ki zubar min da mutunci, in zauna ina kallon ki, saina saki hawayen da har ki mutu bazaki daina kuka ba.
Zuwa wannan lokacin sosai Nur ta hada zufa sabo da radadin da take ji, daurewa take domin kada su Mamy suji bare har tayi abun da Abba zai kara daukan zafi, amman sosai ta kara kulewa da Abdallah jin muryan Abba ya sa  Abdallah ya shafa kansa tare da cire idon shi akan Nur saidai har yanzun yana take da kafarta.
Zama Abba ya yi tare da aunty Saratu da Yaya Bashir kowa sannu yaiwa Abba Abban amman banda Nur da take cikin jin azaban radadi. Dan haka Abba na zama ya kalleta cike da mamaki ya ce ke lafiya kike hada zufa haka?"
Kasa bude baki ta yi ta bawa Abba amsa dan haka ta shiga cije lebe. Ganin haka Abdallah ya sauke kafarshi a hankali batare da ya cire idon sa a kanta ba. Abba ne ke kallon Nur ba, ganin ta bude ido ya ce mene ne ke damun ki?
Ba komai ta fada kwalla cike da idonta, gaba daya gurin hankali aka maida kanta harda Abdallah da yake kallon inda kafarta ta ke Yana cewa wani abu ne a kafar taki?
Jin muryan Abdallah na mata tambaya ya sa ta kara ware idonta dake cike da hawaye tana kallon shi. Gani ta yi fuskarsa warkan tamkar besan me ke faruwa, bata gama mamakin yanayin na sa ba taji yana cewa "Nur wani abu ya samu kafar taki ne?"
Cikin Sauri ta cire idonta akan shi tare da girgiza kanta alamar a'a.
Cikin rashin gamsuwa Abba ya ce "Abdallah duba mata" Ahankali ya aje cukalin abincin sannan ya durkusa kasa Yana leka kafar Nur tare da cewa "Ina ke damun ki?"
Ganin in da Abba ya tsareta da Ido ya sa ta saurin cewa Abba bigewa na yi a kafa dazon, Aunty Saratu ce ta ce, "Me ya sa baki fada ba tun da wuri, ai irin wannan saiki fada da wuri aduba miki kafin ya yi tsami" Karake mgnr ya yi tare da kallon Aunty Saratu yana cigaba da cewa, "idan tagama cin abincin a duba mata."

Amsawa aunty ta yi, shiru wurin ya dauka tsayon lokaci kowa cin abincin yake, ita ko Nur daker ta dan ci sannan ta mike ta ce ta koshi, ta na shirin barin wajen Abba ya ce, "Zo nan naga kafar." Dawowa ta yi gaban Abba ta zauna akasa, shi ko Abba kujerarsa ya ja baya tare da rankwafowa ya na kallon kafar Nur, gannin in da gurin yayi jawur ya sa shi shafa gurin tare da fadin, "Wannan saidai idan wani abinne ya fado miki amman ba begewa ba, idan kin shiga daki kishafa man zafi a wurin."
Amsawa ta yi sannan ta mike ta wuce dakinta, a bakin gado ta zauna yayin da hawaye ya taro acikin idonta,  zuciyarta cike fal da sake-sake, so ya ke ya tunxurani naita fada dashi Abba kuma ya ce bani da kunya, idan ba haka ba Kuma me nai mishi yanzu? gashi Mamy bata da

lafiya, idan takuma jin irin wannan bazataji dadi ba, ta fada cikin zuciyarta a fili Kuma cewa ta yi, "Bazan sake tanka mishi ba kuma ba ruwana da duk wani abinda zai yi da ga yanzu, hannun ta tasa tana shafa saman kafarta inda yayi jawur, wata zuciyar kecewa kimai Allah ya isa ya yin da wata zuciyar ke kwabanta tare  tare da tuna baya kadan, tsitan kanta ta yi da cewa, "Bazan mishi Allah ya isa ba, kila nan da wani lokacin ya huce ya dawo cikin hankalin shi"
  Washegari misalin karfe 8 na safe Nur sanye cikin kayan islamiyya tun da ta fito gida take murmushi domin yanayin garin sosai ya ke burgeta haka nan kuma taji yau tanajin farin ciki, sosai ta kosa ta isa makarantar dan haka take ta sauri.
   Ta na dafda isa kofar gidan su Helen ta fara jiyo muryan Mamma cikin kuka tare da hayani take fada sosai. Wannan ba bakon abu bane agurin Nur domin idan da sabo ya kamata ta saba da ganin kukan Mamma, saidai tana ji na yau ya banbanta, gashi har mama ta fusata ta na fada har ana jiyota a titi, akwai alama Poul ya kai ta bangon da bazata iya hakuri ba, tsintan kanta ta yi da tsayawa cak ta kasa wucewa, tunawa ta yi da wulakancin da yai mata daren daya rage mata hanya, sam bashi da kirki, tsitan kanta ta yi ta na kokarin shiga gidan da har yanzun fadan Mamma ke tashi...

Fadila Lamido
CIWON 'YA MACE
By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 9-10

Ahankali ta tura kofar ta shiga, matar dake zaune wajen shakatawan gidan ce ta dago ta kalli Nur hannunta rike da jarida, yanayin da be nuna irin na wadda ake tashin hankali a gabanshi ba, cikin kwanciyar hankali take, babu alamar damuwa a tattare da ita.
   Cikin sauri Nur ta kalli daya gefen, Helen ta gani tsaye tana share hawaye, yayin da Mamma ke rike da rigar Poul ta na maganganu cikkn fada sosai, tsaye ya ke cikin shadda me dan karan kau hannun shi ya daura akan na Mamma da ta rike wuyanshi dashi yana magana cikin hargagi yayin da Mamma ma take fada sosai. Matar da ke hakimce Nur ta sake kallo, wannan lokacin idonta da hankalin ta ya na kan jaridar da ke rike hannu ta, dan haka Nur ta sake mayar da hankalin ta kan Mamma.
   Duk da cewa bata san me suke cewa ba, ta ga laifin Poul din sosai, domin Mamma ba sa'arshi ba ce, a Kodadaushe bashi da aiki sai na saka Mamma kuka, sam baya darajata, gashi kamar mutumin kirki, sosai take son ta ga karewar abin amma sai kara daukan zafi suke yi; da shi har Mamma, abin da ya ke shirin yi yau yafi na kullum dan ba karamin balaki ya ke yi ba, da alama so ya ke Mamma ta sakar mishi rigar shi amman sai kara rikeshi ta ke, hawaye Nur ta fara sharewa kamar yadda taga Helen na yi, ganin hakan bazai mata ta nufa matar dake can

gefe zaune tana fadi, "Aunty dan Allah kizo ki mishi magana" Waini kallo da matar ta wurga mata ya sata saurin barin gurin, tsintan kanta ta yi ta na rike da Mamma, cikin Sauri Poul din ya sa hannun sa ya banbare na Mamma tare da hankadata takoma da baya da karfi tai zaman dirshen a kasa.

Rungume Mamma Nur ta yi hakama Helen da ta karaso yanzun nan, kuka sosai Nur ta rushe dashi ganin Inda Poul ya ci gaba da balbala masifa ya na nuna Mamma da yatsan shi, ita ma Helen rungume Mamma ta yi ta na kuka sosai, zuwa wannan lokacin kuka kawai Mamma ta ke yi batare da ta furta komai ba, shikuwa Poul saida ya yi bala'inshi ma'ishi sannan ya juya kanshi a fusace ya fice a gidan. Haka Helen da Nur su ka yi ta bawa Mamma hakuri, ganin in da suke kuka ya sa ta miki tare basu umarnin mikewa, ko in da matar nan ta ke mamma bata kalla ba ta wuce ciki abinta, Helen ce tabi bayanta yayin da Nur ta nufi kofar fita daga gidan zuciyarta cike da tausayin su.

Akofar gidan ta tsaya tana kallon hanyar da zatabi ta isa makaranta, sosai ta yi latti, ko ta je ma korota za'ayi, dan haka ne dokar makarantar su, ta jima a tsaye sannan ta kama hanyar gida, har yanzun hawaye na zubowa a idon ta, tun da ta doshi gida gabanta ke faduwa, hakama da ta tura get din gidan su har wani rawan jiki ta fara. Bashir ta hanga zaune saman motar da mamaki ya juyo yana kallonta tare da fadin "Ba'a biya miki kudin makaranta bane?" Kai ta girgiza alamar a'a, kallonta ya ci gaba da yi ta na kokarin wuce shi ya sake cewa "Dukan ki ayi ne a makarantar?" Wannan karon ma kaita girgiza ahankali ya furta, "Allah ya kyauta to, aiki ne ya same ki haka kenan"

Cikin gidan ta shiga batare da ta tanka mishi ba, ta na shiga falon gidan Mamy ta ce "A'a lafiya?" Gefen Mamy ta zauna tare da rufe fuskanta da tafin hannunta ta fashe da kuka.

Aunty Saratu ce ta ce "Mene ne haka Nurr" shiko Abdallah da ke can gefen aunty kallo daya yai mata ya dauke idon shi. Mamy ce ta kwantar da ita akan kirjinta sannan tai kasa da murya tace"Gaya min yaya a ka yi?" Ta na shashshekar kuka ta sanarwa Mamy komai, ta na mgnr Abdallah na satan kallonta Ya na kuma mamakin halinta, bayan takai aya Aunty Saratu ta ce, "To ke me ye na ki na shiga gidan su?" Dagowa Saratu ta yi tana kallon Mamy tare da cewa, "Idan ba an yi da gaske an hana Nur shiga gidan can ba akwai matsala" Mamy Kuma bayan ta gama karema Nur kallo ta ce "Be kyautaba Nur, amman to yanzun me ye abin yi?" Idon Nur a kasa ta ce, "Mamy ki je kimai fada ya daina hakan babu kyau"

"Ni nahaifeshi kenan?" Mamy ta yi tambayan ta na kallon fuskan Nur. Wannan lokacin idon Abdallah ya na kan Nur. Cikin sanyin jiki Nur ta girgiza kanta, ganin haka Mamy taci gaba da cewa "To ko d'an da ka haifa yanzun saika bishi ahankali bare wani baligi da na ke hangensa da ga titi, haba Nur yanzun sabo da wannan kika fasa zuwa makaratar? Ki fita sabgar gidan nan, babu ta inda mu ka hadu dasu, dan haka  dabi'ar mu ma bazata zama daya ba. Fada Mamy taita ma Nur har ta dawo cikin hankalin ta da ga karshe ta ce, "Tashi kije ki cire kayan makarantar" Mamay ta fada ta na bin Nur da kallo, ta na kokarin mikewa Abdallah ya mike ya juya yana kokarin fita yana fadin "Ta zo muje in rakata makarantar" Mamy ce ta ce "A'a yanzun yan mintina ya rage a tashi da yamma ta je"

Batare da ya juyo ba ya ce, " Mamy tazo mu je babu abin da za'a mata"

Ficewa ya yi, tu na yar tsama dake tsakaninta dashi ya sa Mamy ta ce, "Ku je Nur"

"Mamy ai yanzun an kusa tashi" Nur ta fada cikin Yana yin da ke nuna tsoro.

Mamy ce ta ce, "Nur bishi neman abin magana ya ke, ya na iya hadaki da Abbanku" Dole tabi

bayan Abdallah badan ranta ya so ba, acikin mota ta same shi zaune tana shiga ya figi motar sa, be tsaya ko Ina ba sai a cikin makarantar tasu, batare da ya kalleta ba ya fice acikin motar dan haka itama ta fito jikinta a sanyaye, tuni ya shige Ofishin din da malamai ke zama, ganin haka ta tsaya a bakin Office din, bayan wani lokaci ta ga ya fito, wannan karon ma be kalli inda take ba ya wuce abinshi. Daga cikin Office din aka kira sunan ta dan haka ta nufa shiga ciki tana waiwayen Abdallah data hango ya shige motar sa ya tafi abin shi.

Cikin Office din ta shiga da Sallama a bakinta, gaba daya ta ga malaman sun dago suna kallonta, Dan haka ta sunkuyar da kanta kasa, Daga can taji muryan Malam Zubairu ya na cewa "Tsuguna anan" Tsunawa ta yi kamar yadda ya ce, saidai yadda suke binta da kallon ya sa ta kasa da go idonta ta kalle su. Muryan Malam Zubairu ta sake ji yana ce wa, "Ina kika tsaya tun dazun da aka turoki makarantar?" Shiru Nur ta yi idonta a kasa har Malam Zubairu ya sake cewa, "Da ke na ke magana?" Cikin samyin murya Nur tace Malam na fada fa a gida, ai daga gida muke yanzun."
"Da aka ganki ba!" Malam Zubairu ya fada cike da tsawa sannan ya mike yana cewa Malam Sale miko min dorinar can" Dorinar aka mika mishi sannan ya taho yana cewa, " Me kikaje yi a Nafclup kuma?" Wani irin mummunan faduwan gaba ne ya samu Nur tare da zaro duk idonta waje saidai ta rasa kalmar da zata yi amfani dashi dan haka hawaye suka shiga zubo mata, tarowa sukayi duk Malaman akan ta gaya musu me ya kaita can, ganin ta kasa cewa komai Malam Zubairu ya fara zuba mata bulalar tare da tambayanta in abun da ya kaita, ganin taki mgn duk suka dauki bulala gaba dayan su suke kaimata dukan tare da neman amsa amman ta gagara gaya musu komai dan haka saida suka yi mata lilis sannan suka barta.

Bayan Malam Zubairu ya koma ya zauna ya na huci ya ke cewa, "Ba mahaifinki ba, koni malamin ki kin bata min rai, duk acikin daliban da zamu yaye wannan shekaran ke ce abun alfaharinmu, abin bakin ciki ne ace mana kina zuwa irin wannan gurin, baki tashi sama rayuwarki shiririritaba saida kikakai wannan matakin? Ki yi maza ki gyara dabi'ar ki, har aka tashi makarantar ba su barta ba, fada suke ta mata, yayin da jikinta ke mata azabar radadi sabo da dukan da suka mata, duk jikinta ya fashe. Daliban sun watse amman ita sunki ba ta damar wucewa. Bayan tsayon wani lokaci Malaman suka mike sannan suka bata damar mikewa tana gaban su suna binta abaya, abakin makarantar kowa ya kama hanyar gidan shi da ga ita sai Malam Zubairu agurin, fuskar shi a daure ya ce, "Muje" Gaba ta shiga kawai suka fara tafiya tare da Malam Zubairu saidai ba hanyar gidan su aka bi ba Dan haka abin ya shiga bata mamaki.

Hanyar gidan sa ta ga yabi, a cikin ranta ta ce "Ina kuma zai kai ni?" Afili kuwa ta gefen ido take satan kallon Malam Zubairu, Hango motar Yaya Abdallah da ta yi can nesa ya sa ta sakin ajiyan zuciya domin ta manta ma Malam Zubairu anguwarsu daya da Kaka, "Kenan Yaya Abdallah ne ya ce idan an gama jibgata akawo masani gidan kaka." Nur ta fada azuciyarta, sosai gabanta ya fadi, ahankali ta saci kallon Malam Zubairu, sannan ta dauke kanta, su na isa kofar gidan ya tsallaka kwatar kofar gidan ya na kwada sallama, kamar dama jira Yaya Abdallah ya ke saigashi ya fito, hannu su  ka bawa juna alokacin da Malam Zubairu yace "Ke shiga ciki"

Cikin gidan Nur ta shiga, ta na tafe ta na waiwaye, Allah-Allah ta ke ta shige bayan Kaka kafin Yaya Abdallah ya dawo. Koda ta yi sallama babu wadda ya amsa kasancewar dama gidan babu yara Kaka kadai ce a gidan dan haka ta karasa da gudu; dan kada Yaya Abdallah ya cin mata. Bata tsaya ko ina ba sai bayan Kaka tana mai da numshi, tun da Kaka ta ji shigowanta ta fara

fadin wacce almurance wannan?, Banbarakwai ta ji zancen a bakin Kaka domin bata saba jin irin shi da ga bakinta ba, Saida ta mayar da numfashi a bayan Kaka sannan ta kalli kofar da Abdallah ke shigowa yanzun nan tace "Ni ce Kaka"

'Toh, ke ce Nur ko? Kin iso?, Nur da ke bayan Kaka ta ce "Eh" Batare da Kaka ta juyo ba ta ce fito nan ki zauna.

Fitowa ta yi ta zauna domin dama Kaka bame wasa da jikoki bace, kodayaushe ta na cikin tsare gida tare da tsage gaskiya da adalci. Kallo Kaka tabi Nur dashi har Nur ta tsargu da kallonta da Kaka ke yi ta sunkuyar da kai. Kamar da ga sama ta ji Kaka na cewa "Idon ki kenan Nur ? Ashe baki da ta Ido? Ko kadan, ki rasa wadda zaki jefa da irin wannan sharrin sai Abdullahi, yaron da duk jikokina babu me nutsuwar sa, Ina ce ko mutum zai kashe ya binne a gaban ki zaki rufa mishi asiri, ashe abin ba haka yake ba, yar kankanuwar ki dake kina cin mutuncin gemo, ke Nur dago idon ki ki kalle ni nan" Kaka ta fada cikin daga murya.

Dagowa Nur ta yi ta kalli Kaka, yayin da kaka ta ci gaba da cewa "Juya ki kalli Abdullahi Kuma" Wannan karon ma kamar yadda kaka tace haka ta yi, sai dai kallo daya ta mai ta maida kanta kasa, muryan Kaka ta ji tana cewa "Kowa ya kalli tarin kasunbarsa yasan mutumin kirki ne shi, dan me zaki dinga aibatashi, dan wata shasha ta fada miki karya da gaskiya kike kokarin bata mishi suna? Ni wallahi kin yaudareni domin sai yanzun na ke hango tsayayya a idon ki, ke yanzu dan Allah ko kunyan gemun nan nasa bakya ji, yar kankanuwar da ke ki dinga lalibu sharri ki likawa mutum kirki, yaron da ko hannu aka saka masa a baka baya cizawa, to ki shiga hankalin ki tun muna shaida juna, idan ba haka ba zaman gidan nan saiya gagare ki, dan ko ni nan Ina iya karya ki akan Abdullahi, idan Bashir ne ko wani can babu abin da ya shafeni, amma wannan yaron me nutsuwa da hankali kin yi kadan ki matsa mishi, ai duk unguwar nan babu ne nutsuwarsa dan iyayen na ku daga maza har mata idan suna neman muhimmin shawara shine suke nema domin shine ke iya warware musu matsalolinsu cikin sauki sabo da basirarshi, dan haka ki fita da ga idona in rufe, idan ba haka ko zakisha mamakin rashin mutuncin dazan miki. Yadda iyayen na ku ke daukanshi mai mutunci da daraja kema dole ki kalleshi a haka ko kinki ko kin so, duk ma beson karar mishi da mutunci ya yi ya gama, yar kankanuwa da ke sai iya tsaro zance da iya cin mutunci gemo. Ashekarar da uwarki ta kasa zaman aure ta wurgar da ke a tsakar gida shekaranki biyu da rabi, nan Halima ta matsawa kan ta saida ta daukoki hankalinta ya kwanta, kan nan naki cike da kwarkwata, babu in da be yamushe ba a jikinki sabo da rashin kulawa, to idan baki yi hankaliba ungulu zata koma gidanta na tsamiya, ita Halimar wani dadin gidan mijin take ji?, ta yi hakurine sabo da yaranta, ke ko uwarki ta garara zama kuma bata damu da duk irin rayuwar da zaki taso ba dan haka bazaki takurawa Abdullahi

Tunda ta fara magana Idon Nur na a kasa yake, duk da cewa ba kuka ta ke ba amman idonta ya kara yin ja sosai, sannan hankalinta ya kara tashi fiye da abaya. Domin ba ta taba tunanin Kaka zata mata haka ba, ba abin da yafi makanta mata rai kamar maganar mahaifiyarta data sako, muryan Kaka ta tsinkaya da ga saman kanta tana cewa, "Kizo ki tsuguna ki nemi gafararshi sannan ki wuce kiban gurin" Kaka Nur ta kalla, sannan ta mike ta dawo tsakiyar su Kaka tasa guiwarta akasa kamar yadda Kaka ta ce, can kasa ta yi da murya sannan tace, "Dan Allah kai Hakuri na bari" Hannun sa ya sa ya shafa gemun sa tsayon lokaci be Bari ba, zuwa can ya ce, "Idan kin koma gidan ki wanke ni agurin Mamy" Sosai gaban Nur ya fadi, domin sam ba ta son wannan maganar, shi kanshi ai ya rasa kalmar dazai kare kanshi a lokacin. Muyar Kaka ta ji tana cewa "Ba magana ya ke miki ba?" Cikin sauri Nur ta ce, "To zanyi hakan"

Kaka ce ta ce "Ai ya zamar miki dole ki yi, ni tashi ki bamu guri" Mikewa Nur ta yi tare da kallon agogo gani ta yi har biyu ta gota, dan haka ta dan waiga ta kalli Abdallah tare da cewa "Yaya lokacin makaranta yayi ko in wuce da ga nan sai ka gawa Mamy a waya?" Tun kafin takai aya yai saurin daga kansa. Juyawa ta yi tana kokarin fita Kaka tace "Munafuka ta na tafe zakal-zakal kamar sandar fuluni" Dariyar Yaya Abdallah tajiyo dan haka ta kara sauri tabar gidan, tafe take ahanya tana jin duniyar tai mata zafi, sai wannan lokacin ta samu hawaye suka zobo mata; tasa hannu ta ahare, ta na isa makarantar ta wuce masallaci, alwala ta yi tai sallar azahar sannan ta wuce aji, da ka kalleta zaka kamar ba ta da lafiya sabo da tsabar damuwan da take ciki, mahaifiryarta ke ta fado mata a yau, tare da jin haushin Kaka mai tsanani ya na shirgarta, duk da cewa wannan ne karo na farko data fara samun matsala da ita, alkawari taita ma zuciyarta cewa bazata sake zuwa gidan Kaka ba, misalin karfe uku su na tsakiyar Karatu ta hango Mamy ta wuce ajin su cikin yanayin tashin hankali, da sauri Nur ta bita da kallo da alama Ofishin Malam Zubairu zata je, wannan tunanin ya sa gabanta kara faduwa acikin ranta ta ce "Kodai Yaya Abdallah be sanar da ita na wuce makaranta bane? To yanzun idan ta je me zatacewa Malam Zubairu?" Yin wannan tunanin yasata mikewa zubur batare da wani tunani ba ta fice a ajin.

CIWON 'YA MACE
By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

https://chat.whatsapp.com/G07V53Lfxp4KyFPbYSLjyS

Page 11- 12

Can ta hangeta bakin Ofishin su na tsaye da Malam Zubairu, hadawa ta yi da gudu domin ta isa wurin tun kafin Mamy na fadawa Malam Zubairu abin da ya kawota. Ta na daf da ta isa gurin tai saurin cewa, "Mamy!" Cikin Sauri Mamy ta kalleta adaidai lokacin da Mamy take cewa, "A'a ta dawo fita ce ta kama mu, ina tunanin kar a tashi makarantar ta dawo ta iske bama nan, shi yasa na ce barin biyo"

Cike da gamsuwa Malam Zubairu ya jinjina kansa, kallon Nur yayi kadan sannan ya wuce Ofishinsa.

Kallon Nur Mamy ta yi cikin daure fuska sannan ta ce, "Ina kika tsaya Nur baki dawo gida ba? Sawuna uku makarantar nan babu kowa aciki?"

Kwalkwal Nur ta yi da ido sannan ta ce, "Mamy Yaya Abdallah be miki bayani ba? Mu na tare da shi a gidan Kaka, Kuma na ce mishi ya gaya miki." Jimm, Mamy ta yi zuwa can ta ce, "Wanne Yayan?" Hawayen da ya zubo mata tasa hannu ta share sannan ta ce "Yaya Abdallah" Shiru Mamy ta yi a lamar nazari ta ke, zuwa can ta ce, "Shi na fara kira da na ga yaci ace kin dawo gida ya ce min shi tun da ya sauke ki ya wuce abin shi" Da Sauri Nur ta dago ta kalli Mamy "Mamy wallahi ba haka ba ne, Kuma a tambayi Malam Zubairu sannan mu je gidan Kaka kiji, a gaban ta na ce mishi dan Allah ya gaya miki..." Hannu Mamy ta daga wa Nur alamar

dakatarwa sannan ta ce, "Bazan tambayi Malam Zubairu ba, kuma bazanje gidan kaka ba, ke da bakin ki zaki gaya min in da kika tsaya, daure fuska sosai Mamy ta yi, sannan ta ce, "Wuce muje gida" Nur batai musu ba ta shiga gaba, Itako Mamy juyawa ta yi gurin Malam Zubairu, lokacin da Mamy ta fito makarantar Nur na tsaye tana kuka, hannunta Mamy ta rike tare da fadin, share hawayen ki  karki sake min kuka atiti, shasha kawai, so ki ke sai kowa ya fahimta me kike ciki?" Daker Nur  ta iya dakatar da Kukanta har suka isa gida, a harabar gidan su ka samu Aunty Saratu, tasowa ta yi itama cike da damuwa ta na cewa, "Ina kika tsaya Nur?, Kallo Mamy tabi Nur da shi tare da cewa "Ta ce, gidan Kaka ta tsaya, ta kuma cema Yayan su ya fada min" Mamy ta karake maganar tana kallon fuskar Yaya Abdallah da ya fito da ga cikin gidan yanxun.

Kallo daya Abdallah yayi ma Nur, sannan ya ce "Ke! Me kike cewa?"
Dagowa Nur ta yi da jajayen idonta ta ce, "Ai kai kace Malam Zubairu ya taho dani gidan Kaka, kuma da na ga lokacin makaranta ya yi nace maka zan wuce makaranta ka gayawa Mamy..." Afusa ce Abdallah ya tako gaban Nur cikin yanayin da ke nuna cewa yana cikin mamaki ya ce, "Maimaita in ji! Ke dan baki da kunya har ki iya kallon idona kimin Karya?" Ganin yana Shirin daga hannun sa tai saurin matsawa tare da fadin, "Karka da ke ni hannun ka akwai zafi" Kara yowa kanta yayi Mamy ce ta ce "Karka taba ta wuce abin ka" Wayar sa ya dauko a aljihunsa yana cewa, "Ba dai gidan Kaka ta ce ba barin kirata"
"A'a karka kirata." Mamy ta fada cikin bada Umarni. Juyawa ta yi ta kalli Nur, sannan ta ce muje ciki" Cikin gidan suka nufa, yayin da Abdallah yai ficewan shi waje. Bayan sun shiga ciki ma Mamy da Aunty Saratu matsawa Nur suka yi, akan ta fada musu in da ta tsaya, amsan nan dai da ta bada tun farko ita take sake badawa, dan haka suka barta kawai badan sun gamsu da zancen ta ba.

Washegari ta kama lahadi  Mamy bata barta taje makaranta ba, hakama ranar litinin daker Mamy ta barta, saida ta hada mata da magiya, daka kalli fuskar Nur kake gane tana cikin damuwa, idon ta duk sun kunbura ga yawan tunani da take yi.

Misalin karfe 8 na safe ta isa makaranta, ita da Helen kamar yadda suka saba, acan suka samu Rahma dake dama can tana riga su zuwa, wayar Rahma Nur ta amsa ta fita waje ta zauna, number data riga ta haddace cikin kanta tasa wayar sannan ta kara a kunnen ta tsayon lokaci tana jiran taji an dauka amman harta katse ba'a dauka ba, batare da wani bata lokaci ba ta sake danna kira, sai dai wannan karon ma harta katse ba'a dauka ba, dan haka ta hakura ta mike ta nufi komawa cikin ajin su, sosai ta ji jikinta ya kara sanyi tare da jin komai baya mata Dadi, ta na daf da shiga ajin wayar ta dauki kara, kallo daya tawa wayar sannan ta juya ta koma gefe tare da ansa kiran.

Kuka ta saka cikin wayar, bayan tsayon wani lokaci ta sassauta kukan nata, zuwa can kuma ta share hawayen tass, sannan tabar shashshekar kukan tare da fadin, "Eh ina ji" Shiru ta sake yi tsayon lokaci, da ga can  ta sake cewa, "Mamy kawai na fadamawa" Turo baki ta yi da alama fada ake mata cikin wayar, zuwa can ta ce, "Ai be dace ba abin da ya ke, kuma kowa kallon mtumin kirki ya mishi, ni ba sharri nake mishiba..." Shiru ta sake yi, bayan tsayon lokaci ta na saurare tace, "Sabo da Mamy" Sosai ta kara bata ranta zuwa can tai jifa da wayar can nesa, kallo tabi wayar dashi, kome ta tuna kuma saita mike da sauri ta dauki wayar, dake karamar waya ce babu abin da ta yi, ganin wayar bata katse ba ta sake maida ita kunnen ta tare da fadin, "Na bari" Shiru ta yi na wanni lokaci sanna n ta ce, ba yarwa na yi ba faduwa ta yi"

Wannan lokacin ma shiru ta sake yi, zuwa can ta sauke wayar sannan ta nufi ajinsu jikinta a sanyaye.

Bayan an tashi makaranta ta koma gida, har yanzun Mamy fushi take da ita, dan haka ta cigaba da yin duk wani abu da tasan zai faranta wa Mamy  rai, shiko Yaya Abdallah ba ta sake barin sun hado ba domin ya zun ta lura dashi ya riga da ya tsene ta.

Haka ta cikaba da lallabawa har saukanta ya rage saura kwana biyu, duk wani shiri ta gama yin sa, Abba da Mamy sun mata komai da akewa yar gata daidai gwargwado, a na i gobe sauka ta je lalle da kitsu, bayan ta dawo farin ciki ne ya kama Mamy kallon kurulla tai mata tare da fadin "Ba karamin me sa'a bane mijin da zai aure ki, tubarkallah ma sha Allah, duk wadda ya same ki a matsayin matar aurensa lallai ya tsinci dami akala

Murmushi ne ya subuce ma Nur cikin matsanancin jin kunya ta ce "Mamy ai fushi kike da ni har yanzun"

"Eh, ai kece kika mata min rai, bedace ace kina boye min komai ba, ni uwarki ce, idan har bazan san me kike ciki ba meye amfanina?"

"Toh ki yi hakuri kinji? Kuma ban boye miki komaiba wallahi Mamy, Yaya Abdallah yasan ba in da naje wallahi"

"Na ji Nur, ni dai fatana ki nutsu, ke mace ce, dan haka ki daina karanbanin saka kafar a ko ina"

Amsawa ta yi da to, sannan ta mike ta nufi dakinta, Mamy ko binta da kallo ta yi duk wani alamar girma ya riga da ya bayyana ajikin Nurr, yariya ce kyakyawa fara sol me mayan idanu, siriri ce sosai, saidai duk da cewa shekarunta bazai wuce sha shidda ba kirjinta cike yake taf ma sha Allah, sauke kai Mamy ta yi, bayan Nur ta kule tare da cewa "Allah ya nuna min auren yariyar nan lafiya sai naji tamkar inzoba ruwa a kasa in sha"

Washegari tun da sassafe ta shirya cikin fararen kaya safar hannu da ta kafa baki haka ma fuskanta bakin nikafi ne, dakin Mamy ta shiga bayan ta gaisheta  ta dauki turaren Mamy kan madubi da fesa  cike da murmushi  Mamy tace "Allah ya kawo mu" Itama Nur murmushi ta yi tare da fadin "Mamy zan wuce dan Allah kuzo da wuri"

"In sha Allah Nur, dan ina ga ma ko Abban ku saidai ya saman acan" Da murmushi Nur ta nufi dakin Abba, acen ta samu Aunty Saratu zaune bayan ta gaishesu Abba ya shiga mata addu'a, in da ya kare da cewa,  Allah ya sa in ga ranar auren ki kamar haka, duk yawan family nan bamu taba aurar da diya mace ba" Cike da shagaba Nur ta fice tare da da cewa "Saura dai ka ga na zama likita Abba" Abba daya juyota bayan ta fice yayi murmushi sannan ya kalli Aunty Saratu ya ce, "In sha Allah tun da tana son karatu zan tsaya mata ta yi sosai" Gyara zama Aunty Saratu ta yi sannan tace "Ai daman yaran gidan nan suna Karatu Alhaji."

"Eh haka ne, sai dai ita mace ce, amman bazai garara ba, in dai ta maida hankali zan cika mata burinta" Nisawa Aunty Saratu ta yi sannan ta ce, "Amman Alhaji sai na ke ganin kamar rashin sa'aninta mata da babu cikin dangi yana taba ta sosai" Murmushi Abba ya yi tare da cewa, "A'a, babu wannan maganar anan gidan, sai dai da ya ke kinsan aski idan yazo gaban goshi yafi zafi, Bashir da Abdallah su na janta ajiki, ga kuma Jamal da Jamil, nan gaba kadan duk aure za su yi, matayensu suma 'ya'yayenmu ne"

Bude baki Aunty ta yi da nufin yin magana kome ta tuna kuma sai tai shiru tare da mikewa.

****

Misalin Karfe 10:am filin saukar ya cika ya tunbatsa, sai dai har wannan lokacin baza ido Nur

ta ke, domin bataga wani daga gidansu ba dan haka banda baza ido babu abun da ta ke,Tuni aka fara karatu, gashi an hanasu tashi bare ta nemi waya ta kira Mamy, ta na cikin wannan yanayin taji an kirayi sunan ta, Maryam Jibiril Mailafiya, mikewa ta yi tame jin kafarta na rawa, har ta isa kan munbarin ta amsa abin maganar, cikin nutsuwa ta ke rairo karatun ta, yayin da jama da dama suka maida hankali wajen sauraronta, bayan ta gama ta mika abin maganar ta sauka akan munburin tare da isa gurin zamanta, tana zama ta fara share hawayeta cikin nikabi, ganin har wannan lokacin babu kowa da ga gidan su, matar da ta dauki hoto ne a gurin tazo ta mika wa Nur hoton da ta dauketa wurin karatun, karba ta yi ta kalla, ganin bata da kudin da zata bayar yasa ta mika mata tare da fadin "Zan amsa anjima" Durkusuwa matar ta yi tace "Ina yan uwanki suke in kai musu?"

Hawaye ne ya zubo wa Nur alokacin da take cewa "Basu karaso ba"  kafadanta ta dan dafa alamar rarrashi, daker Nur ta iya rokon matar aron waya, saidai har sau uku ta kira number Mamy ba'a daga ba dan haka me hoton ta kara bata hakuri sannan ta wuce.

Acikin ranta ta ke tunanin ko menene ya hana su zuwa? sam bata tsammaci haka ba, nan taji komai yabar yi mata dadi, kiran sunayin yan saukan da aka fara domin basu shahada ya dawo da ita cikin hayyacin ta, agefe guda ta hangi mata nan nata mata wa su hoton dan haka ta nuna mata alamar ta habari, matsowa matar ta yi kusa da ita tace "Wani ya amsa hotunan ki ya ce, a kara miki wasu" Duk da cewa batasan wane ne ba dadi taji har tai ajiyan zuciya batare da ta sani ba, zuwa can aka kira sunan ta, nan ta miki akaro na biyu ta isa gurin, acikin ranta take cewa,  "Allah yasa koma wanene yazo min yamin kara kar a gane Abba da Mamy basuzo gurin nan ba, saidai ga mamakinta ta Abba tagani Yana tahowa  filin cikin babban riga da hula, bayansa Yaya Abdallah da Yaya Bashir ne sai dai Abba ya rigasu isa gurin dan haka shine ya karban mata Shahada, bayan angama masu hototuna suka koma gurin zamansu, sosai Nur ta cika da farin ciki acikin zuciyarta take cewa, "Abba ma yana farin ciki sosai, hakama Yaya Bashir ya kasa boye farin cikinsa sai yake hakora ya ke, shi ko Yaya Abdallah fuskarshi babu yabo babu fallasa, bayan an gama bawa kowa sannan aka sake kiran sunan Nur a matsayin wadda tazo na daya, nan farin ciki ya sake rufe su Mamy, fitowa ta yi ta amsa kyautuntuka, sosai taron ya kayatar, kowa na nuna sha'awarsa, bayan an tashi gurin zaman su Abba ta nufa ta kwanta kafadan Mamy cikin shagwaba tace, "Mamy bakizo da wuri ba"

"Injiwa ya gaya miki, Yaya Bashir ne ya ce muna nan aka  fara Karatu"

"Ni ban ganku ba har na fara kuka fa"

Dariya suka yi gaba daya da ga nan Yaya Bashir ya kira me hoton nan suka hadu suka yi gaba daya har da Baffah da iyalanshi.

Kowa cikin fara'a ya ke, adaidai wannan lokacin ne Nur ta hangi kyawawan samari guda biyu, tun da Nur ta gansu fara'ar fuskanta ya dauke, Mamy ce tace, "Nur ga su Jamal can ki maza kije ku gaisa"

"Mamy su karaso nan mana' kasa Mamy ta yi da murya ta ce "Ki je dai domin kema kinsan ba zuwa zasu yi ba"

Sakin hannun Mamy ta yi ta isa gaban su, tun tana cikin su Mamy su ke mata wani irin kallo har ta iso gaban su, cikin girmamawa ta gaidasu yayin da suka amsa a wulakance tare da fadin, "Da baza kizo bane?"

"A'a mu na yin hoto ne" Nur ta fada tana satan kallon fuskar Jamil wadda ko gaisuwar ma be amsa ba, Muryan jamal ta ji yana cewa "Ke ma kinsan idan ba dole ba babu abun da zai

kawomu cikin wannan unguwar bare wannan yar tsukukuwar makarantar dako iska ba shigowa ya ke ba"

Bakin shi kawai Nur ta kalla ta kara yin kasa da kai.

Jamil ne ya ce "Jamal mu je, ai dai ta gammu ko? Cike Da haushi Jamal din ya ce, "Ni wallahi ko bata gammu ba babu abin da ya dame ni. Tsoronta akeji ne? Ko zumuncin dole ne?"

Lumshe Ido Nur ta yi ganin suna kokarin barin wajen ta ce "Baku gaisa da su Abban mu ba gasu can"

Jamal dake baya ne ya ce "Ayya, haka ne fa, oya to mu je mugaida su" Yana maganar ne yana cigaba da tafiya dan haka ta bisu da kallo har suka shiga motar su suka bar wajen.

Bayan ta ga wucewan su tsaki ta ja afili ta ce "Dadin abun dai mu ma ba matsiyata bane, kuma da zuwan ku da karkuzo duk daya" A daidai wannan lokacin ta ji an gota ta bayan an hankade kafadarta, dan haka ta bi mutumin da kallo, mamaki ne ya kamata dan haka ta kara baza idonta domin gani ta yi kamar yayan Helen ne Poul ya wuce ta.

Tsaye ta yi a gurin tana son tabbatarwa, motar da ya nufa tabi da kallo, har ya isa gabanta na faduwa tare da tambayan kanta me ya kawoshi cikin musulmi? Yadda ya ke da shigarsa bazaka taba gane cewa ba musulmi ba ne, haka Kuma ko magana yayi babu alamar da zata nuna maka hakan, "Kenan ya yi amfani da hakan ya shigo makarantarmu?" Nur ta fada cikin zuciyarta tare da saurin takawa domin tabbatarwa, motar ta ga ya bude ya shiga ya zauna, sannan ya waigo ya suka yi ido hudu tamkar yasan tana kallon shi dama can. Sosai gaban Nur ya fadi faduwa me tsanani, ganin irin kallon da ya ke mata, haka ta tsaya cak tamkar an dasa ta agurin, fararen ya tsunsa ta ga yana karkadawa alamar tazo kusa...

CIWON 'YA MACE
By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 13-14

Saidai ta na daf da isa gurin ta ga motar ta tashi dan haka ta tsaya cak a daidai lokacin da ta jiyo Yaya Bashir yana kiranta. Juyowa ta yi cikin da sauri ta ke kokarin isa gurin tare da cewa acikin zuciyarta "Kodai dama idona ne ya nuna mani kamar ya kira ni." Da irin wannan tunanin ta ta koma cikin Mamy batare da tabar waiwayen bayantaba, har yanzun ta na mamakin zuwan Poul wannan gurin.

Hotona suka kara yi bayan sun gama suka wuce gida, suna isa gidan ma samunsa su ka yi cike da jama'a, Aunty Saratu ce ke kula da bakin, gaba daya dangin cike suke da farin ciki tare da sha'awan Nur tare da ganin kazonta, ga uwa uba nutsuwa da hankalin dake gareta.

Shima Abba sosai ya yi farin ciki saidai a kasan zuciyarshi ya na da wani tunani akan Nur; ganin inda kwana biyu yanayinta yake kokarin canzawa daga kyawawan dabi'u zuwa munana.

Ita ko Mamy a yau kallon tsananin kauna ta ke ma Nur; duk da cewa ta canza amman tasan wane ne sular canzawan na ta.

Washegari Nur ta tashi da tsananin gajiya lokacin da ta isa dakin Aunty Saratu zama ta yi cikin nuna gajiya. Kallonta aunty Saratu ta yi sannan ta yi murmushi tare da cewa "Ai zuwana uku kina bacci"

"Da kin tashe ni Aunty, ina tashi naji kamar an kwashe min 'ya'yan hanjina." Mikewa Aunty ta yi tare da fadin "Duk sabo da yunwar? Ai sai ki yi maza ki je ki karya ni na azama zaki makaranta ne"

"A'a saida yamma zani" Nur ta fada tare da gyara zamanta. Adaidai wannan lokacin Abdallah ya shigo dakin, sai dai ganin Nur yasa ya dan yi jimmm kadan, sannan ya shigo ya zauna tare da fadin, "Aunty ina son na yi magana da ke" Kallon Abdallah Aunty ta yi sannan ta mike ta isa kujeran da Abdallah ya zauna ta zauna gefen sa tare da cewa "Ina jin ka" Juyowa yayi ya kalli Nur ya ce "Baza ki bamu wuri ba ?" Kallon shi Nur ta yi sannan ta mike ta na kokarin fita taji ya ce, Kina kallona ne da wasu dakwa-dakwan idon ki kamar na mage, kallon aunty Saratu ya yi sannan ya nuna Nur tare da fadin "Wai dan Allah aunty kuna ganin abin da nake gani kuwa?" Jin haka yasa Nur ta tsaya cak, itama Aunty Saratu cike da mamaki ta ce me ye shi? "Jibeta fa kamar sanda daka kalleta babu abin da kake gani sai dai katon hanci da wasu manyan abubuwa da suke jan ta" Kirjinsa ya nuna da hannu dan haka Aunty ta yi murmushi kadan tare da cewa, "Nur ki je abinki" Wucewa ta yi a hankali tanajin lokacin da Aunty ta ce "Abdallah kenan, baka da dama"

"Wallahi Aunty da ka kalleta su kawai kake gani abun ko tsari babu, ko ta ina yariyar nan bata da hali, a baya tausayinta nake ji, yanzun ko dana kalleta saina rasa da wacce dambar zan kwatanta ta sabo da muninta da nake gani." Runtse ido Nur ta yi sannan ta wuce, sosai ta yi dana sanin sauraron kalamansa, cike da damuwa ta koma dakinta, a cikin zuciyarta ta ce, "Wato sabo da tsabar muni na ya rasa dambar da zai hadani da ita, hawaye ne suka zobo mata tasa hannu ta share sannan ta mike ta isa gaban madubi, kallon kanta take acikin madubin tare da rike hancinta sannan tace afili, "Mene ne wasu abubuwa da suke janna? Zan so nasan meye shi wannan abin dake jana" Kiran da taji Aunty Saratu na mata ya sata share hawayen sannan ta nufi dakin.

Wayar Abdallah ta miko mata tare da fadin, "Abdallah ne ya manta awayar shi, gashi ana ta kiran shi, ki kai mashi ya na gidan su Auwal."

Amsa ta yi sannan ta fice a dakin, dakinta ta koma ta sanyo babban Hijjabi, sannan ta daura nikabi ta rufe fuskarta, fitowa da ga cikin dakin ta yi tare da kallon wayar, wannan ne karo na farko da ta fara ma wayarsa kallon kurulla, tsintan kanta ta yi da danna wayar yayin da wani kyakyawan hoton budurwar yariya ya bayyana, sosai kyan yariyar ya dauke hankali Nur; har ma ta fara tunanin inama ace takai ta kyau, wani abin da ya kara bata mamaki wayar a bude take, cikin sauri ta shiga danna wayar, cika ta yi da mamaki lokacin da ta ga mutanen da yai waya da su daren jiya, duk sunayen mata ne har su tara, Kuma ko wacce ya dauki tsayon lokacin yayin da yai waya da ita, gurin adana hoton cikin wayar ta nufa, ta fara dubawa, nan ta fara cin karo da hotonanshi dare da taurarin finafinen Hausa mata da maza, tun da ta bude bakinbta ta kasa rufewa sabo da tsabar mamaki, tunani ta shiga yi shi kuma me ye ya hadashi da Yan fim din Hausa ko shima ya na fitowa ne aciki ko kuma Fim din yake son ya fara, gefen videos ta gani ta na kokarin shiga gurin taje motsin tafiya dan haka tai sauri ta maida wayar cikin hijjabinta tare

da fitowa daga cikin falon. Mamy ta gani ta na fitowa daga dakinta bayan sun gaisa Mamy ta ce, "Ke zani in tado ashe kin tashi ma."
"Na tashi Mamy, zan kaiwa Yaya Abdallah wayarsa gidan su Yaya Auwal" Ajiyan zuciya Mamy ta yi tare da cewa, "To yi maza ki dawo" Juyawa Nur ta yi ta fice da sauri take tafiya domin yunwa ke kwakular cikinta.

Tafe take tana sake-sake cikin zuciyarta akan wayar da ta ga yayi cikin dare, kenan baya bacci koma ya na yi to bana kirki bane, sannan ganin shi cikin yan fim yasa ta fara tunanin domin dama batasan aikinsa ba tasan dai ya na zuwa Office amman bata San me ya ke acan ba, wata zuciyar ce ta ce kila dai yana zuwa gurin yan matanshi ko abokanshi amman Abba nasan bazai barshi yayi wasan Hausa ba.

Tsakanin gidan su dana su Auwal babu nisa, dan haka nan danan ta isa, ta na tura get din gidan ta hangi takalman maza da yawa a bakin kofar wannan ya tabbatar mata da suna da yawa acikin dakin.

Bakin kofar ta tsaya ta rangada sallama cikin zazzakar muryanta, da ga cikin dakin ta ji an amsa ganin babu wadda ya fito Kuma babu motsin tafiya ya sata sake yin Sallama yayin da aka sake amsawa daga ciki tare da cewa shigo mana.

Yamutsa murya Nur ta yi sannan ta tura kofar tare da shiga cikin dakin, suman tsaye ta yi ganin Sumayya zaune Yaya Abdallah ya daura kansa akan cinyanta, idon shi rufe yayin da Sumayya ke wasa da kasunbarsa, kasa cire idonta ta yi a kansu, ta na mamakin wannan lamarin bakinta sake. Ita ko Sumayya tun da suka hada ido da Nur tai saurin cire hannunta a jikinshi tare da rasa abin yi.

Da ga bayanta ta ji ance, "Abdallah ga kanwarka." Da saurinshi ya bude idonsa tare da waigowa ya kalli Nur sannan ya fara kokarin tashi zaune yana me cije lebenshi na kasa, bayan ya tashi zaune ma saida ya damki sumarshi sannan ya ce, "da ga ina? Me ya faru?" Kawar da kai Nur ta yi sannan ta fito da hannunta da ga cikin hijjabin ta mika mishi wayar tare da cewa "Inji Aunty" Hannu ya mika ya amsa dan haka Nur ta juya da nufin ficewa a dakin, sai a wannan lokacin ta kula da wasu matan dake gefe su biyu tare da Auwal da wasu abokan nasu guda biyu. Cikin sanyin jiki sosai ta fice a falon a daidai lokacin da Abdallah ke cewa, "Inazuwa karki wuce, ki jira ni anan kinji" A harabar gidan ta tsaya nesa da dakin kadan, fitowan Sumayya ta gani dan haka ta bita da kallo, babu abin da ke daure mata kai kamar wannan al'amarin, wannan lamarin shine mafarin gigicewarta domin kuwa Sumayya tana da aure da yaranta biyu, "ina ta baro mijinta ta taho nan gurin? Anan ta kwana? Ko kuwa da safe tazo? Mijinta baya gari ne? Ko kuma yana garin amman ta tsallakeshi ta fito ta na dakunnan gemon katon kawai? Yaranta fa? Shiryasu ta yi suka tafi makaranta ko kuwa?" Nur ke tambayan kanta, ganin babu me bata waddan nan amsoshin ya sa ta sakin ajiyan zuciya tare da dauke idonta akan get din gidan.

Adaidai wannan lokacin Yaya Abdallah ya fito har ya kawo inda take bata motsa ba, cikin daure fuska ya ce, "Mu je" Gabanshi ta shiga ta fara ta fiya da sauri, ganin haka Abdallah yai saurin cewa "Ke tsaya" Nan take ta tsaya tare da kallon shi, kawar da kanshi yayi tare da cewa, "Me kike son nasiya miki?" Kawar da kai  ta yi sannan ta ce, "Babu komai" Yawo ya hadiye sannan ya ce, "A'a mu je na siya miki wani abu mana" Shiru ta mai har suka isa kofar gidan, cikin bada Umarni ya ce, "Tsaya a nan na dauko mota mu je ki zabi abin da ranki keso ko nawa ne zan biya" Turo bakinta ta yi gaba tare da cewa "Yunwa nake ji bari naje naci abinci tukuna"

"Ki tsayani nace ko" Abdallah ya sake fada cikin yar tsayawa.

Dole ta tsaya, domin ba yadda ta iya dashi, cikin gidan ya shiga ya fito da mota duk tana tsaya kawai tana binshi da kallo, "Shiga" Abdallah ya fada cikin bada Umarni, wannan karon ma shiga ta yi batare da tace komaiba,. sannan ya daga waya ya kira Mamy ya sanar mata da in da za su sannan ya sauke wayar yana satan kallon Nur.

Koda suka isa dankareren kantin da kanshi ya zabar mata kayan shafa da turaroka, sannan ya ce, idan akwai abin da take so ta dauka. Kallon shi kawai ta yi ta kauda kai bayan sun fito a gurin suka dauki hanyar komawa, ganin sun kusa gida ya waigo ya kalli Nur tare da fadin "Na miki siyayya bakice min kin gode ba? Can kasa-kasa Nur ta ce, "Na gode" Murmushi ya yi kadan sannan ya ce, "Ko ke fa? Kanshi ya shafa sannan ya ce "Nasan kiga Sumayya ko?" Kai Nur ta da ga alamar eh, Abdallah ne ya cigaba da cewa "Ta yiwa su Mama kara ne tazo duba jikin Auwal, kinsan ya kwana biyu babu lafiya" Sanyi jikin Nur ya kara; daker ta iya da ga kanta ta kalleshi. Ganin haka Abdallah ya yi ajiyan zuciya sannan ya ce, "Amma dai duk da haka karki fada ma Mamy, kinsan har yanzu ba dadinta nake ji ba, tun akan wancen batun da aka gaya miki karya ki ka hau kai kika zauna, ki ka kasa yiwa yi min adalci alhali hakan ba gaskiya ba ne, kuma kinfi kowa sanin ba halina bane, dan haka ina rokon ki dan Allah kada ki gayawa kowa.

Ta gefen ido Nur ta sata kallon shi sannan ta ce, "To" Numfashi Abdallah ya fesar sannan ya ce "Kin min alkawari?" Wannan karon kai Nur ta daga a dai-dai lokacin da suka shiga gida, kokarin Bude motar ta fara Abdallah yayi saurin cewa, "Nur nasan halinki ke din kina da sirri, kuma bakyacin amana" Wannan karon ma dai Kai Nur ta daga sannan ta fice acikin motar.

Lokacin da Nur ta shiga gida kallon mamaki Mamy ta yi mata, ganin ta rike da ledoji ga kuma Abdallah da ke binta abaya. Wani shashin na zuciyarta ne ya tuna mata baya kadan, dan haka ta kawar da tunanin komai. Abdallah ko bebar falon ba Saida ya ga Nur ta gama cin abinci ta kwashe ledojin siyayyar da yai mata ta shige dakinta.

Washegari ta kama Moday dan haka Nur da wuri ta wuce makaranta.

***

"Abdallah wai yau lafiya kuwa? Yanayin ka kamar mara lafiya" Mikewa yayi tare da fadin, "Bacci ne be isheni ba Mamy Sam ban rutsa ba" Da kallo Mamy ta bi shi sannan tace, "Kuma kace lafiya lau kake?" Yana Shirin barin dakin ya ce, "Eh banajin ciwo sam." Bayan ya fito kofar gida wani ajiyan zuciya ya sauke sannan ya ce afili, Tun da har ta fita bata gayaba nasha in sha Allah, hannunshi ya mika ya shafa suman shi sannan ya sake cewa dole tabar gidan nan, akullum kara tsanarta nake yi ta takura ni da yawa" Saman motarshi ya zauna tare da neman hanyar dazai yi maganin matsalar da take Shirin fin karfinshi

****

Nur da Helen akan hanyar su ta dawowa daga makaranta, da kafa suke tafiya yayin da Nur ke cewa "Helen ki dago kafa mana, yau naga kina nafiya ne lakakai-lakakai.

"Wlh yunwa nake ji Nur, kwana na uku basa wani kwakwaran abinci a cikina ba" Da sauri Nur ta kalleta tace "Sai me to?" Cikin halin ko in kula ta ce, "Ya ce bashi da kudi me gidan, kudin dake hannun Mamma kuma duk sun kare" Lumshe ido Nur ta yi sannan ta ce "Matar shi fa?" Hmm suna yin abincin su suci..." Tun kafin ta rufe baki Nur tace, "Wannan ba daidai ba ne, shiwai bejin tsoron Allah ne, kato dashi ya na yiwa Maman shi horon yunwa? Na ga baya jin tsoro ko shakkar mama, shiyasa ada bana yadda idan akace itace mahaifiyarshi, ya kamata asamu wani yayi mai wa'azi.wai ku baku da wani Malami ne da zai nuna mishi mahimcin

iyaye?"
"Hmmm, Mamma ta hakura da zama tare dashi, ta ce kudin mota kawai take nema mu koma Kauyen su, Nur kila karatu na zai tsaya kwanan nan"
Sosai maganar ta doki zuciyar Nur cike da tausayawa tace "Karki yi wasa da karatunki, gara kuci gaba da hakuri, ko Kuma ku dawo gidanmu ku zauna idan har kun gaji da zama anan"
"Mamma ta gaji Nur, kullum ta na kuka bata baccin kirki, idan ya ga tabar kusa dashi za'a iya samun saukinshi"
"Ni dai karku tafi Helen, yanzun kizo muje gidanmu kici abinci kafin kije gida"
"Da sauri Helen ta kalli Nur ta ce, bazan iya zuwa ba bayan nasan mama bataci ba, bama ta da lafiya tun shekaran jiya"
Adaidai lokacin da suka kawo kofar gidan su Helen din Nur ta ce "Mu je to idan kika ce saiki kamai Mama nata"
Jin haka yasa Helen tabi Nur sai dai Koda sukaje bata tsaya ci ba zuba mata a ka yi ta tafi dashi.
Bayan tafiyan Helen ne Nur ta bawa su Mamy labari halin da su Helen suke ciki, sosai suka tausaya ma su, saidai mama na tsoron taimakonsu saboda Poul ba kirki gareshiba

***

Washegari misalin karfe 04:12pm Abdallah ne zaune a gaban Abba, tun da Abba ya kirashi a waya ya zufa taki tsayawa har yanzun da yake zaune a gaban Abba, zallar bacin rai da damuwa kawai ya ke hanga a fuskar Abba, dan haka hankalin shi ya tashi sosai, kosawa yayi yaji dalilin kiran, sai dai Abba yaki kallonsa sai aikin Bude takardu yake kuma fuskarshi babu wasa ko kadan acikinta, rabon da yaga fuskar Abba haka har ya manta saidai wata zuciyar na ce mishi kila zato ne kawai yake yi, yayin da wata zuciyar ke tuna masa da matsayin Nur a gurin Abba, Sunanshi da yaji Abba ya kira shi ya katse mishi tunanin azabure ya dago ya kalleshi..
CIWON 'YA MACE
By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 15-16

Dagowa Abdallah ya yi da sauri ya kalli Abba, saidai gani yayi kamar bashine ya kira sunan nashi ba, dan haka gabanshi ya cigaba da faduwa, zuwa can ya dake cikin sunkuyar da kai ya ce, "Abba lafiya kuwa?" Fuskar Abba daure tamau ya dago ya kalli Abdullah sannan ya ce, "Na ji wani mummunan al'amari da ga gareka Abdallah, banso ace na yi maka magana yanzubaz saidai hankalina yaki kwanciya, nakasa zuba ido koda na kwana biyu ne, idan abin da naji gaskene zan gwammaci matuwa da ganin irin wannan al'amarin"
"Ni Kuma Abba?" Abdallah ya fada tare da tattara hankalin sa akan Abba gabanshi na faduwa sosai.
"Kai fa Abdallah, ina son in san menene alakanka da Sumayya? bana son zagaye-zagaye,

abu daya na tambaye ka, dan haka amsan na ke bukata, ina son in san ta in da ka kulla alaka da matar aure dahar, karkamin karya" Zufa ne ke kara yanko wa Abdallah, tare da nemo kalmomin da zai kare kansa da su wurin Abba, gefe guda na zuwaciyarshi kuwa na kara zuzuta mishi kiyayyar Nur, tare da rayawa azuciyarshi dole ne ya kirkiro sanadin da zatabar gidan.
"Da kai nake magana" Abba ya sake fada wannan karon a hasale ya ke.
Cikin tashin hankali Abdallah ya sunkuyar da kanshi batare da ya shirya ba, jin sunan Sumayya a bakin Abba, daker ya iya daurewa ya ce, "Abba waye ya fada maka?"
"Abdallah amsan kawai nake son ka bani, aina naji ko waye ya gaya min wannan ba matsalarka bace"
"Abba bani da wani alaka da ita" Cikin Ido Abba ya ke kallon Abdallah gani yayi zufa sai gangaro masa ya ke dan haka ya ce, "Hakika zan ji mamaki kwarai idan na tabbatar da ka na aikata irin wannan abubuwan, domin ko kadan be yi kama da ɗabi'un ka dana sani ba, kana da ilimin ka daidai gwargwado, sannan ka mallaki hankalin kanka, kasan cewa kebewan da macen da ba muharamarka ba haramun ne, bare Kuma matar aure, Babana me ya kaika wannan danyen aikin?"
"Abba ni ban aikata hakanba Sam, yadda dani da kuke yi yasa ake son a bata ni a gurin ku, kuma nasan cewa ba kowa bane zai yi irin wannan maganar sai Nur, dan yariyar nan yanzu..."
Katseshi Abba yayi da cewa, "Me yasa zaka ce Nur ce ta fada?"
"Abba baka sani bane, yariyar nan ta dade tana son taga bayana, kwanaki Nur ta hadani Mamy akan maganar Sumayya, bansan da ga Ina aka turota ta batani a wurin ku ba, taje ta ce ma Mamy wai ina neman Sumayya, haka ran Mamy ya faci kiris ya rage ta tsine min, na yi kokarin wanke kaina awurin amma Mamy taki bani dama, kuma har yanzu ta na akan haka, sabo da kawai Nur ta fada mata, kenan ita Nur bata karya nine makaryaci, aranar raina ya baci har na daki Nur, ganin haka ciwon Mamy ya tashi, bansan me na tarewa Nur ba acikin gidan nan Abba, idan baka manta ba kwanaki a gabanka ta jefeni da babban kufin kwalba batare da na mata wani abu ba, ko na mata wani abu ma ai be dace tamin haka ba, yanzun kuma wurinka take son batani, me na tare mata Abba" Karake maganar yayi kamar zai fashi da kuka; dan haka Abba ya ce' "Babu abin da ka tare mata, wata kila gaya mata ake waje, amman akwai wadda taci min adakin Auwal ta ganku tare da idonta ba gaya mata aka yi ba"
"Abba to ta kawo wadda ya fada mata, idan ma ita ta ganni ta kawo shaida, ni zan iya kiran su Auwal su zamar min shaida, waya yake kokarin dagawa Abba ya ce "Dakata Babana, duk ba wannan bane mafita, ko ka aikata ko baka aikata ba Ina baka sharawa kaji tsoron Allah a dukkan lamuranka, sannan abu na gaba shi ne, maganar aure. Ina son ka yi aure nan kusa, dan banga abin da kake jira ba."
Jikin Abdallah da sanyi sosai ya ce, "Abba ka manta da mgnr karutu da zan tafi nan da wata biyu masu zuwa, kuma zai iya daukana tsayon shekara daya kafin na dawo"
Kara daure fuska Abba ya yi tare da fadin, "Toh yanzun Yaya ka ke nufi?"
"Idan na kammala zan yi Abba."
"Babana bani da wani buri ayanxun illa inga ka yi aure, Kuma nan kusa nake so, idan tafiyan ta tashi saika wuce da matar ka.
Shiru Abdallah yayi tsayon lokaci, zuwa can ya ce "Shikenan Abba, zan yi in sha Allah"
Yauwa zan yi tsananin farin ciki da hakan, nasan a kodayaushe kai me bin umarnina ne, ina son akan auren ka burgeni kazo min da labarin nan kusa"

Godiya yawa Abba, sannan ya tashi ya fice jikin sa a sanyaye. Kai tsaye dakin sa ya wuce cike da haushin Nur dankare a zuciyar shi, tunanin ya shiga mai zurfi akan shakkun da Nur tasa azuciyar Abba da Mamy game dashi, mafita ya shiga nema idonsa jawur akarshi hankalinsa ya tsaya akan cewa yayi auren kawai domin shine zaisa Nur ta fita hanyarsa.

Bayan sati daya Nur ce kwance tsakiyar gado bayan ta dawo Islamiyya, har yanzun tunanin Abdallah da tagani tare da Sumayya take, sosai abin ke daure kanta, tana cikin wannan Yana yin ta ji muryan Helen dan haka ta tashi zaune a daidai lokacin da Helen din ta shigo dakin, yadda taga fuskan Helen ya sa hankalita tashi sosai tare da fadin lafiya?

Nur ni da Mamma ne, na zo in gaya miki ne zamu tafi, idan mama ta ji sauki kila mu dawo... Katse Nur ta yi tare da cewa "Karatun ki fa?"

"Ban sani ba Nur, ni dai kawai nasan Mama bata da lafiya shine abin da ya dame ni yanzu, nina ce mata ta zo muje mu nemi lafiyarta"

"Babu Inda zakuje Helen, ki shigo da Mamma nan gidan barin je inyiwa Abbanmu magana.

Jimmm Helen ta yi tana kallon Nur tare da mamakin Kaunar da take nunawa a garesu batare da ta damu da banbancin addinin dake tsakanin su ba, bayan Nur ta fita dakin tabi da kallo komai tsaf, duk da cewa gidan Poul keraren gidane amma sai ya fiye mata can ban sha'awa, haka nan taji kaunar gidan na ratsa sassan jikinta, dan haka ta saki ajiyan zuciya mai cike da kwanciyar hankali.

****

Nur zaune gaban Abba, bayan ya sallami wani dake zaune daf dashi ya ce, "Nur! Cikin wasa da hannun Nur ta dago kanta, Cike da fara'a Abban ya ce, har yanzun baki bar damuwan bane? "

"Na bari Abba"

"Yauwa ki kwantar da hankalin ki, komai zaizo karshe, na yi magana dashi sosai, a yanzun haka maganar da nake miki aure zai yi, bayan na yi magana dashi da kwana biyu yayi min bayani akan iyayen yariyar da yake so, mun kuma je mun nema masa kuma sun bamu, a yanzun haka su muke jira su tsayar mana da rana."

Cike da fara'a Nur ta ce "Abba yaushe za'ayi bikin?" Kara fadada fara'a Abba yayi sannan ya ce, mu a shirye muke su muke jira"

"Abba!"

"Na'am Nur, na lura akwai abin da kike so ko?"

"Eh Abba"

"Toh inajin ki"

"Abba kawata dinan Helen, itace Mamman su bata da lafiya wai zasu koma kauyensu da zama"

Cikin rashin fahimta Abba ya ce "An nema maganin ne anan ba'a dace ba?"

"A'a Abba, kudin maganin ne babu ko abincin da zasuci basa samu agidan, kuma idan helen ta tafi shikenan ba lallai azana jabawar karshe da ita ba"

Shiru Abba ya yi tsawon lokaci zuwa can ya ce "Mai kike so ne yazon?"

"Abba Helen na cikin gidan nan yanzun haka, dama ka barsu su zauna anan"

Shiru Abba yayi zuwa can ya ce, "Wannan ba mai yiyuwa bane Nur, idan d'anta ya kasa riketa kamata ya yi ta koma gida kamar yadda zasu yi yanzun, shi taimako wani lokacin yana da wuya musamman kinga su ba musulmai bane, duk da cewa sum dade acikinmu, yanzu Ina ga abin da za'ayi zan bada kudi a kaita asibiti sannan zan musu sayayyar kayan abinci ta koma gida

suci gaba da hakuri."

"Amman Abba bata da lafiya yanzu, Kuma ta riga tayi fushi da gidan, dan Allah Abba kadan barsu ko kwana biyu su yi a nan dan Allah, da mamaki Abba yabi Nur da kallo tare da ganin tana dauko ma kanta damuwan da yafi karfinta, jimmm Abba yayi tsawon lokaci zuwa can ya ce, "Shikenan"

Cike da farin ciki Nur ta shigo da su cikin gidan, ganin yanayin jikin Mamma Abba ya bawa Bashir izanin akaita asibiti, Mamy ce dauka zaninta na atamfa ta daurawa Mamma akan siket dinta dabe karasa guiwa ba, sannan ta daura mata dankwalin atamfar a kanta, bayan motar ta zauna saidai har yanzun rawan dari take dan haka Mamy ta kwalawa Nur kira bayan ta amsa ta ce ta kawo mata hijjabi, cikin gudu gudu Nur ta kawo hijjabin kasancewa Mamy na gaban motar bayan ta kawo Mamy ta ce tasawa Mamma, wannan karon cike da mamaki Nur ta nufa Mamma Helen dake zaune kawai tana rawar dari, cikin sauri ta zura mata, yadda Mama ta cure acikin hijjabin tamkar ba ita ba, sai da motar ta fice a gidan sannan Nur ta koma cikin gida, sai yamma su Mamy suka dawo, wannan lokacin babu wani rawan sanyi da take abinci taci sannan Tasha magani tai bacci.

Bayan kwana su uku sosai Mamma ta murje ta yi jawur da ita tamkar ba ita bace tazo da masassara, har yanzun ta na sanye da hijjabi tare da zannuwan da Mamy ta bata, ga abinci me kau har sai sunci sun barshi, komai da suka basu Mamy ta hada guri daya domin yaune Abba yayi Umarni su koma gida, misalin karfe uku na rana Mamy ta raka Mama gurin Abba domin su gaisa Kuma ta yi godiya, cikin Sakin fuska su ka gaisa da Abba, sosai ya nuna jin dadinshi ganin ta samu lafiya, nan ya bata kauta kudi bayan kayan abinci daya haka hada mu su, kuka ta fara tare da fadin, "Tun da nake a duniya ban taba tsintan kaina cikin nishadi da farin ciki kamar na yau ba, na sha wahala tun ina da cikin poul, mijjna ya mutu tun suna kanana nakiyin aure, duk domin ingina rayuwar Poul da kanwarshi,  ba irin wahalan da basha ba wurin biya bishi kudin makaranta, da hidimar rayuwar sa, har ya zama abin da ya zama yanzu, amma daidai da rana daya betaba faranta min kamar haka ba, yata min alkarin zanji dadi amma Yana yin aure komai ya canza, dakatawa ta yi da maganar ta share hawaye sannan ta ci gaba da cewa, "Da Poul kadai nake takama, akanshi duk na aje burina, na dauki tallar ruwa akaina na biya mishi kudin makaranta amman yaki kulawa dani alokacin da karfina ya ke shirin karewa, sai gashi ku da bantaba tunanin zaku taimakeniba ku ne ku ka taimakeni, acikin kwana uku da na yi da ku naji ina kaunar ku, ina jin kewan rabuwa da ku, Alhaji ni da Helen zamu musulunta" Cikin zare ido Abba ya kalleta sannan ya juya ya kalli Mamy da fuskarta ya cika da mamaki, koda wasa Bata tsammaci jin irin wannan kalamin ba, cikin daburcewa Abba ya ce, "Kina nufin zaki zama musulma?

"Eh  ta bawa Abba amsa cike da karfin guiwa, cike da sanyin jiki Abba ya ce, "Ikon Allah, mikewa yayi ya dauke hularshi ya sanya sannan ya Kira Mamy su ka fita, bayan tsayon lokaci Mamy ta dawo daf da Mama ta zauna tare da cewa Maman Helen kin yi shawara da yaranki kuwa?, Musamman shi babban kar abin ya kawo mu ku matsala."

"Karki da mu da shi Hajiya, bazai da mu ba, na yi magana da Helen mun yanke wanan shawaran Poul ba ma gabanshi, zai yi rayuwarsa ne mu yi ta mu"

Jimmm Mamy ta yi tsayon lokaci zuwa can ta sake cewa ba kuma fushin abin da yaron ki ya miki bane ya sa zaki musulunta? Ina nufin yanzu in da a ce zai bar abin da ya ke yi za yi zamanki a addinin ki? Cikin sauri Mama ta girgiza kai tare da fadin, nutsuwa da kwanciyar

hankali da na gani a tattare da ku ya jawo hankalina, kana uku da na yi a gidan ku na fahimci wasu abubuwa da dama a tare da ku da kuma yaran ku, sannan kuma bana iya tuna rabon da na samu kwanciyar hankali da nutsuwa irin wadda na samu cikin kwana ukun da na yi a gidan nan.

Ajiyan zuciya Mamy ta yi sannan ta fita, zuwa can su ka sake shigowa tare da Abba, zama ya yi sannan ya ce, "Yanzun abin da za a yi ki je gida ki kara nutsuwa tare da zurfafa tunani, ki yi shawara da yaran ki, zuwa gobe ko jibi sai kizo...." Katse Abba Maman Helen da ta yi da fadin, "Ni fa na riga na gama yanke shawara, yau nake son nabar addinin can" Murmushi Abba yayi jin furucinta saidai ya na dan bargaba akan labarin nata, dalilin tuna waye danta, tun da ya mallaki gida a unguwar ta su baya mu'amala da kowa, ko daga hannu baya yi, dan haka ba kowa ne ya san fuskarsa ba, da wuya kasamu mutumin da zaice ya sanshi a fuska, saidai ana iya shaida duk motocin da yake hawa, ajiyan zuciya Abba ya yi sannan ya ce, "Shikenan tashi muje wajen Malam Zubairu. Mikewa suka yi fuka fito, yayin da Mamy ta kwalawa Helen Kira bayan ta fito suka shiga motar suka tafi.

Ganin fitan su Nur tace Mamy naso na rakasu har gida, ba gida zasu ba, Mamy ta fada tana gyara zamanta sosai nan ta kwashe komai ta bawa anuty da Nur labari, sosai Nur ta shiga farin ciki hakama aunty Saratu, bayan kusan awa biyu su Abba suka dawo, wannan karon Helen sanye take da hijjabi, ganin haka kwallar farinci ya cika idon Helen rungume juna suka yi ita da Helen tsayon lokaci. Abba ne ya Umarci Nur da tazo ta raka su gida, fitowa suka yi har da Abba, sabo da kayan abincin da ya hada musu ya sa ya kaisu har kofar gida sannan suka dawo gida, sai dai har yanzun a cikin zuciyar Abba be gama gamsuwa da Helen da Mahaifiyarta ba, dan haka ya ke dan rage fara'arsa, wani abu da yafi daga hankalinshi shi tunda suka fara ganarwa komawa Musulunci gabanshi ya fara haduwa kuma har yanzun daya sauke su ya dawo gida faduwam gaban nasa gaba yake ba baya ba, aduk lokacin da gabanshi ya fadi fuskar Poul ce ke fado masa arai dan haka ya shiga karato addu'oi

*****

"Duk in da nake tunanin zasu je naje basa nan, na gaji sosai, Ina son in ganta tukuna in je wurin aikina, komai nawa ya tsaya, babu Mamma babu Helen, anan babu Mamma a can gida babu Mamma" Ajiyan zuciya matar dake tsaye a gabanshi ta yi sannan cikin hausarta da bata fita sosai ta ce, "Wai dama ba kai ka sauke su ba, ai sun shigo dazon da kaya mai yawa"

"Mamma? sun dawo?" Tabe baki Matar ta yi sannan ta ce sun dawo, amman fa akwai matsala kamar dai almajirai haka suka dawo, kuma sun saka hijabi ajikinsu.

Hijjabi? Poul ya fada cikin daga murya sannan ya nufa hanyar da zata sadashi da dakin dasu Helen suke yana tafe kamar mai shirin tashi sama.

CIWON 'YA MACE

By

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Kallon kallo ne ya shiga tsakanin Poul da Mamma alokacin da ya tsaya a tsakiyar dakin, shigar da ke jikin su ya bi da kallo, ganin kaya irin na Hausawa ajikinsu ya cika da mamaki, Mamma ko tun da ta kalleshi sau daya ta dauke kanta tare da cigaba da tufke wa Helen kai, daf da su ya karaso tare da fadin, "Ina kuka je kwana biyu?"

Cikin daure fuska sosai Mamma ta ci gaba da abin da take batare da ta bashi amsa ba, dauke kansa yayi ya maida wurin Helen domin wannan shine karo na farko da yaji nauyin sake jafawa Mamma tambaya, "Helen ina kuka je?"

"Sunanta Zainab." Mamma ta fada fuskarta daure tamau. Cikin Sauri ya maida kallon shi ga Mamma, "Bangane ba Mamma" Poul ya fada hankalin shi a tashi tare da ware idon shi waje yana Kara bude kunnen shi.

Cike da karfin haki Mamma tace "Eh abin da ka ji haka ne, ni da ita mun karfi musulunci yau...."

Me ya sa mamma? Poul ya fada cikin tsananin tashin hankali tare da kara matsawa daf da Mamma ya na ware idon shi waje. "Idan bazaka iya za ma damu ba zamu tafi kauye mu zauna"

Mamma idan wasa kike yi mini ki bari, hakan bazai taba zama gaskiya ba, idan kuma kin yi ne dan ki bata min rai wannan ba shi bane mafita, dan idan har kuna bin wannan addinin bazamu zauna inuwa daya ba, kuma bazan fita in nemo kudi inci da ku ba"

"Poul babu wasa a idona, ni da Helen mun karbi musulunci, sabo da hankalina ya fi nutsuwa dashi, yanzun hankalina ya kwanta, na samu lafiya"

Sosai ran Poul ya baci har kana ganin wasu irin jijiyoyim da ke  cikin kanshi saboda tsananin tashin hankali, idon sa kuwa wani irin ja yayi irin wadda be taba yi ba, cikin tsananin fushi ya ce, "Bazan zauna da ku ba, na ji ke da helen kun canza addini dan ku bata min rai, idan ni ne na mata miki rai ba wan ne mafita ba, da ga yanzun ko me kuke so ku fada min zan muku, amman bana son musuluncin nan, ko a mafarki bantaba tunanin zaki yi haka ba Mamma...."

Poul ko me zaka ba ni bazan taba barin wannan addinin ba, rabon da na samu nutsuwar da na samu yau na jima sosai, bazan ma iya tunawa ba, na gane  babu wadda ya kamata na dogara dashi sai Allah wadda ya halicceni ya halicci bayin da suka taimakeni; batare da mun hada komai ba, na samu nutsuwar da na rasa ko rabinta a gareka"

Wanni irin kallo poul yaiwa Mamma, bayan ya gama kare mata kallo ya ce, "Shikenan, ku tattara duk wani abu da kuka san da gumina kuka siya ko na saya muku, ku aje min sannan ku barmin gidana, bazan sake zama tare da ku ba, bana son in sake ganinku a rayuwata.

Bakin sa Mamma ta ke kallo a lokacin da ya ke furta wannan kalamin, sosai ya ke bata mamaki nan ta tuna yadda mazan gidan su Nur ke mutunta iyayensu, sannan ta tabe baki tare da daure fuska sosai ta ce, "Dare yayi amma idan mun wayi gari lafiya da safe zamu barmaka gidan ka."

Kallon Mama Poul yayi sannan ya juya ya fita adakin, afusace ya ke tafiya tare da sake sake, wata zuciyar ce ta ce, "Ka korasu mana a daren nan" yin wannan tunanin ya sashi yaja ya tsaya, sannan ya waiga ya kalli hanyar tare da tuna fuskar Mamma, besan me yasa ba haka kawai ya ke ganin fuskarta a yau ta mashi kwarjinin, ita kanta da alama cike take da kwarin guiwa, dan haka yaji Sam bazai iya kallon idonta ya ce sai sun fita a daren nan ba, saidai zuciyarshi cike take da bacin rai har ya isa dakin sa, Yana shiga yasa makulli ya rufe dakin.

*****

Washegari da safe Poul ne zaune saman motar sa idonsa jawur, da ka kalli fuskarsa kasan ya na cikin baccin rai, tun da ga nesa ya hango budurwar yariya cikin Hijjabi har kasa, jajayen idonshi ya kara bazawa afili ya ce Nurr ce, ganin tana Jan akwati ya ji faduwan gaba afili ya sake cewa, "Wato akwai sa hannun yariyar nan aka shirya min wannan abin, idan ba haka ba me take a gidan nan? Yaushe ta shigo min gidan? Tun da sauran duhu nake zaune a wurin nan" Sakkowa yayi sama motar a fusace ya ke takawa jikinshi har tsuma yake, waige ya shiga yi domin neman madoki domin mudin yace zai dake Nur da hannu tana iya mutuwa, ganin babu wani abu da zai iya dokan Nur din dashi ya maida hankalishi wajen da suke tahowa, sai yanzun ya lura da dattijuwar da ke binta a baya, itama sanye cikin Hijjabi har kasa, bayan ya kare mata kallo ya ce "Mamma?" Adaidai lokacin da Mamma ke amsawa ya juya ya kalli yariyar da ke gefenta, Helen ce tsaye badan fuskarta ba kaikace Nur ce tsaye, sosai ya zuba mata ido tsayon lokaci sannan yai saurin saka hannun sa ya rike hijjabinta tare da fadin, "Wannan abin na Nurr ne ko?"
Da ga Helen har Mamma sun yi mamakin jin sunan Nur a bakin Poul, Mamma ce tai saurin girgiza kai tare da fadin "Banata bane, masallacin da mukaje jiya acan aka bamu."
Lumshe Ido Poul ya yi sannan ya jawo Helen ya kai hijjabin hancinshi ya shinshina, dagowa yayi ya kalli Helen sannan ya cewa, "Na Nurr wanna, kenan gidan su ta kaiku?" Wannan karon ma cikin sauri Mamma ta girgiza kai alokacin da Poul ya ke cewa acikin zuciyarshi, "Amman zan nunawa yariyar nan ta yi kuskure mara kyau a rayuwarta, barinta da na ke tana shigowa gidan nan shine ya bata damar dauke min uwata da kanwata? Bazan taba bari hakan ya tabbata ba muddin Ina numfashi, saina koya mata hankali, da ma na lura da yariyar nan, akwai tsata me yawa a idonta, ko ma meye zan aikata domin in ga Mamma tabar wannan addinin da take kokarin jefa kanta acikin" zuwa can ya dago ya kalli Mamma cike da kwarin guiwa ya ce, "Ina zakuje?" Daure fuska Mamma ta yi sosai sannan tace, "Kauye, Ina ce kace in dai muna yin addinin musulunci sai dai mu barmaka gidanka?" Da sauri Poul ya dukar da kanshi kasa sannan ya ce, "Na sake tunani, zaku iya zama abin ku" Cike da mamaki Mamma ta kalli Poul, sanyin da taga yayi abin yai matukar daure mata kai, dan haka ta ce, Na gaji da zaman wulakanci da na ke yi a gidan nan idan har kasan zaka cigaba da mini abin da kake gara na koma kauye."
Lebensa na kasa Poul ya cize sanna ya ce, "Zan kiyaye." Karake maganar ya yi tare da amsan akwatin dake hannun Helen sannan ya juya cikin gidan, Mamma da Helen wadda ayanzun ta koma Zainab kallon juna suka yi sannan suka bi bayansh,i sai dai har yanzun Mamma ta kasa gamsuwa da sanyin da ta ga jikin Poul din yayi.

******

Nur ce durkushe ta na wanke kayan makantarta bayan ta gama ta dauraye, bayan gidan ta nufa domin shanyawa, hannunta ta daga sama da nufin shanya hijjabin islamiyyarta, cikin sauri ta saki hijjabin ya fadi kasa, tare da waigen falin da ita daya ce tsaye a gurin, diriricewa ta yi gaba daya tana kokarin fita hayyacinta, daker ta iya lalubo jarumta ta nufi windows din dakunnan dake bayan gidan na su, ahankali take bin sautin har ta isa bakin window da sautin ke tashi, wani dutse ta dauko tasa a gurin, sannan tahau kan dutsen ta leka, saidai labulen rufe ya ke

dan haka ta kasa kunne, tabass da ga nan sautin ke tashi, dan haka ta sauka akan dutsen a guje ta nufi cikin gidan tare da kwalawa Mamy kira.

Saukowa a gado Mamy ta yi da sauri tana dafe da kanta dake sara mata tun safe, jin kiran da Nur ke kwala mata hankalinta ya kara tashi domin tasan babu lafiya.

Aunty Saratu dake kicin ko fitowa ta yi tana cewa, "Nur mene ne haka, kin dai san bata jin dafi ko?" Zaman dirshen Nur ta yi a dakin tana maida numfashi, da ga Mamy har anuty Saratu afirgice suke tambayanta me ya ke faruwa?

Cikin tsananin haki take cewa, "Mamy, Aunty Saratu ku je dakin Yaya Abdallah ku gani..."

Anuty Saratu ce tace, "Meye a dakinsa? Me zamu gani acan din?"

"Mamy ku je ku gani wallahi ku yi sauri."

Mamy ce ta kalli Aunty Saratu sannan ta ce, "Saratu jeki gani"

"A'a, yanzun fa ya min sallama baya gidan nan, ina ga fa firgita take yi" juyawa ta yi ta kalli Nur ta ce, "Ke! ki nutsu dallah ki yi magana, mene ne kika gani a dakin?" Cikin numfarfashi Nur ta ce "Mace ce Yaya Abdallah ya shigo da ita cikin dakinshi...."

Hannu Mamy ta sa ta dafe kirjinta tare da runtse ido, cikin daga murya ta ce, "Mace! Acikin gidan nan?" Ganin in da ta runtse ido tana dafe da kirji Aunty Saratu tabita da kallo cike da fargaban kar ciwonta ya tashi, ganin Mamy na kokarin ficewa a dakin afusace Aunty Saratu tai saurin riketa tare da cewa, "Karki je, ki bari ya fito dan Allah."

Bige hannun Aunty Saratu Mamy ta yi tare da cewa, Bazan iya tsayawaba Saratu, wannan iskancin har ina, tun munajin waiwai ace har takai acikin gidan nan yake damar da zai mana haka."

"Koma mene ne karkiji dan Allah, kindai san baki da lafiya, ki bari ya fito, ko Kuma a kirashi a waya."

"Sakeni ina zuwa." Mamy ta fada tana kokarin zamewa daga rokon da Saratu tai mata. "Bazan sake kiba, ki yi hakuri bari na kirashi a waya"

"A dai dinga jin tsoron Allah, abin da baka son a maka kar bari amawa wani, ta yaya muna cikin gidan nan zamu bari haka na faruwa? Ina yar mu haka ta faru a kanta zamuji dadi? Saratu muna cikin gidan nan kuma kice wai in bari ya fito? Cikin sauri Saratu ta saki Mamy jikinta da sanyi sosai, afusace Mamy ta fice yayin da Aunty Saratu tabi bayanta.

CIWON'YA MACE

By

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 19-20

Afusace Mamy ta tura kofar dakin Abdallah tare da runtse idonta tsayon lokaci, Aunty dake bayantane tabi dakin da kallo, ganin babu kowa adakin yasa tabi Mamy da kallo tare da fadin, " Kinga Babu kowa a dakin fa?" Cikin sauri Mamy ta bude ido ta, ganin babu kowa ta shiga waige-waige, ko ina gyare ya ke tsaf, ban da tashin kamshi babu abin dake tashi a dakin, da sauri ta kalli kofar bayinsa da ke cikin dakin, ahankali ta fara takawa har ta isa wurin ta tura kofar, ko ina bushe ya ke, alama ce dake nuna anjima ba'a shigaba, juyowa Mamy ta yi cike da

mamaki, da ga gefen gadonsa Mamy ta hangi tarin littafansa na addini daya karanta wadda har yanzun baya rabo da karantasu, domin ta na yawan ganinshi yana bude dasu, ji ta yi kafafuwanta sun gaza daukanta dan haka ta tsinta kanta da zama bakin gadonshi tare da fadin, "Saratu abubuwan da suke faruwa kwana biyu cikin gidan nan suna daure min kai. Kindai ga yadda Nur take a rikice, ta ce dakin nan akwai mace Kuma gashi babu kowa adakin, ni Kuma basan Nur da karya ba." Nisawa Aunty Saratu ta yi sannan ta ce, "Tashi mu je Mamy, ni dama can bana zargin Abdallah, dan dai kuna cewa ba'a shaidan yaro yasa nai miki shiru kawai, amman ni aciki raina ina tantama, Abdallah fa ko daga kai ya kalli mace baya yi, kuma tuntuni ku ke cewa yayi aure amman sai ya ce shi ba aure bane a gabanshi, sanin kankine Abdallah ya tsana mace mara kamun kai, ko ita Nur kullum cikin mata nasiha yake karta yi wani abu dazai taba mutuncin gidan nan." Lumshe ido Mamy ta yi alamar nazari take, zuwa can ta ce, "Amman Nur bazata mishi sharri ba fa" Wani irin kallo Aunty Saratu tayiwa Mamy "Ni dai na fara zargin Nur tanason ta batawa Abdallah suna ne, tunda duk abin da take fada babu daya daya tabbata."

Ajiyan zuciya Mamy ta yi sannan suka fito a dakin, adaidai lokacin da suka fito falon, lokacin Abdallah ke shigowa falon, gani fitowan su da ga gefen sa ya ce, "Lafiya?"

Sauke ajiyan zuciya A unty ta yi sannan tace, "Lafiya lau" Kujera Mamy ta nema ta zauna dan haka itama Aunty Saratu zama ta yi jikinta a sanyaye. Ganin Mamy na share hawaye ya isa gabanta ya zauna tsakiyan kafarta tare da saurin rike hannunta ya ce, "Mamy wai mene ne?" Yana yin tambayan Mamy ta fashe da kuka, dan haka hankali Abdallah ya kara tashi. Cike da damuwa ya ce, "Aunty meye ya ke faruwa ne? Mamy me ya faru?"

Cikin kukan Mamy ta ce, " Duk abin da na ce ka yi ka na yi, abu daya ta taba umartanka da ka yi kaki yi, kuma shi ne babban abin dake sani damuwa a yazun, kullum bani da kwanciyar hankali na kasa sukuni...

"Me ye shi Mamy? Mamy tun kafin in ji meye na miki alkawarin duk abin da kike so shi za'ayi, ki fada min Mamy."

"Aure na ke son ka yi" Mamy ta fada cike da damuwa, dagowa ya yi da sauri ya kalli Mamy sannan ya ce, "Aure kuma Mamy?, yanzun akan auren kike irin wannan kukan?"

Dole ne in shiga damuwa, baka yi rashin ji tun farko ba dan haka banajin dadin ganinka a haka, idan ba aure na ga ka yi ba hankalina bazai kwanta ba." Hannu Abdallah ya mika ya na share hawayen Mamy tare da fadin, "Yanzun to ba maganar auren ake ba?, ai mun riga mun gama mganar da Abba komai ya kusa zuwa karshe in sha Allah ki kwantar da hankalin ki, ko ance miki na yi wani abinne Kuma?"

"Hankalina ne kawai ya kasa nutsuwa, aure nake son kayi kawai" Hannu Abdallah ya mika yana share mata hawaye tare da cewa, "Shikenan zanyi Mamy ki kwantaar da hankalin ki" Daker Abdallah ya samu kan Mamy sannan ya wuce dakinsa cike da damuwa, Mamy ko bayan ta koma daki samun Nur ta yi tana Bacci, dan haka itama ta kwanta gefen ta zuciyarta cike fal da tunani.

****

"Mairo! Mairo!" Wata tsuhuwa ce ke kwala kira tare da kotsuwa cikin falon tana sake cewa wai ina Mairon!? Can cikin baccinta ta jiyo muryan tsuwar dan haka ta diro a gadon ba tare da ta

shirya ba take cewa, "Oyoyo Hajiya!"
Itama Mamy da saurinta ta sauko a gadon ta biyo bayan Nur tana fadin, "To fa ko me ya kawo hajiya da tsakar ranar nan?" Ajikin Hajiya Mamy ta hangi Nur kwance cikkn tsananin murna, tsaye ta yi tana kallon su, muryan Aunty Saratu Mamy ta jiyo da ga bayanta tana cewa,  "Hajiya lafiya?" Sakin Nur Hajiya ta yi tare da rike hannunta ta karasa shigowa falon ta zauna tare da cewa, "Me kuke nufi ne? Jikata nazo gani, ko laifine dan na taho?"  Da ga Aunty Saratu har Mamy murmushi suka yi sannan suka karaso su ka zauna tare da hada baki wajen cewa, "Babu laifi, sannu da zuwa"
"Yauwa ku bani ruwa nasha kishi nake ji da kafa na taho na gaji sosai." Mikewa Aunty Saratu ta yi tana kokarin shiga kicin ta kula da Abdallah dake tsaye ya hade fuska babu abin da ya ke sai kallon Hajiya, murmushi Aunty ta yi sannan ta dan waiga ta kalli Hajiya, ganin bata San da Abdallah a gurin ba yasa ta yi murmushi tare da cewa, "Abdallah wannan kallon fa?" Kicin din ta shiga batare da tajira amsanshi ba, ita ko Hajiya tun da aka ambaci Abdallah ta bishi da kallo, ganin ya ki motsawa ta ce, "Kai kuma me aka maka ka tsaya anan? baki gaba kamar na biri yayin da ya so tsegumi" Kallon Hajiya yayi yana kokarin kawar da kai ya hangi Nur tana dariya kasa-kasa tare da boye fuskarta jikin hajiya, dan haka yai saurin tahowa gurin tare da nuna Nur da hannun sa ya na cewa, "Ke dan ubanki wa kike ma dariya? Ina wasa da ke?" Tun da ya fara maganar ta hade fuskarta, Hajiya ce ta kalli Abdallah sannan ta kalli Nur ta ce, "Ikon Allah, idan kai ba kayin dariyar ai baka hana wani yayi ba, haka kawai, yau na ga jaraba"
"Yanzu dai me ki ka zo yi? Ba su Abba sun hanaki yawon nan ba?"
"Ai duk fadin duniyar nan babu uwata babu ubana dan haka babu me saka min ta kunkume hana zirga-zirga, ko akwai me aurena fadin duniyar nan?" Karamin tsaki Abdallah ya ja, sannan ya nemi guri ya zauna tare da cewa, "Dan kiyaye lafiyan ki akace ki zauna wuri daya; ba wani abu ba, amman idan kinga za kiyi ta yi sai ki yi"
Ruwan da Aunty ta mika mata ta karba tasha bayan ta sauke ruwan ta ce, "Ni dan jikata na zo badan wani kato ba, karka dame ni da fada, ko iyayen ka basu isa ba bare kai, ledan dake gefenta ta dauko ta mikawa Nur, yayin da Nur ta shiga budewa cike da murna, kayan kwalliya ne cike da ledan, dubawa take tare da yiwa Hajiya godiya, Mamy ma godiya ta yiwa Hajiya, hakama Aunty Saratu, shiko Abdallah cewa yayi "Wato Hajiya kudin da su Abba ke bakine ki ke mata siyayya dashi ko?"
"Eh, idan banyi mata siyayayya ba me zan da su?" Tsaki Abdallah ya ja, sannan ya ce " Amma ai ana bakine dan ki dan dinga siyan wani abin kici badan mutum daya ba" Tabe baki Hajiya ta yi tare da cewa,  "Oho nifa duk abin da zaka fadi ka dade baka fadaba ita kenan guda daya tamkar tsuka daya amiya, idan ma bakin ciki kake Kai ka sani, lokacin danai wahala da ku ita batazo ma duniyar ba"
"Wanni wahala kika yi damu?" Abdallah ya fada yana kallo Hajiya, "Ka tambayi ubanka tun da ya ke ya taba siya maka hula?" Yar dariya Abdallah yayi sannan ya ce "Wannan danki kika sayawawa ni bani ba, kuma saina ce musu su daina baki kudi"
"Eh ka hanasu, ai ba kirki gareka ba, bansan in da ka samu wannan dabi'ar ba ta shirin son abin arzikiba" Mamy ce ta ce "Hajiya da gangan yake miki ai be isa ba ma."
Toh banda iskanci ni mahaukaciya da da zai dinga min da gangan, idan basu bani kudin ba waye zai bani?
"Ai shine Hajiya" Wasa ya ke miki. Aunty Saratu ta fada tana hararan Abdallah.

Hajiya ko cewa ta yi, "Ni bana wasa da jikoki, sabo da banson raini da rashin kunya, hawaye Hajiya ta share sannan taci gaba da cewa, ruwane ya daki babban zakara amman ba komai, ka hanasu subani ko bara naje na yi na karasa tara kudin dankunnen gwal din da na ke kokarin tarawa na sayawa Nur."

Ganin in da take share hawaye Abdallah ya ce, "Nifa wasa nake miki Hajiya, amman idan sun baki kibawa Tani ta din ga sawo miki abun dadi kici"

"Kayan kwalliyar da gwal da nake son sayawa Nur fa?" Murmushi Abdallah yayi sannan ya ce, "Ni zan din ga baki kina tarawa wannan" Murmushi Hajiya ta yi tare da cewa, To ai shikenan tashi muje ka kaini gida, nagaji sosai, haka kawai ina zaune kamar an mintsineni nace ni sainagano Mairo" Gudun karya ballo wata rigima ya mike tare da cewa, "Mu je to"

Mikewa ta yi cike da fara'a ta ce "Ko kaifa, dan albarka, na ji ance min ka kusa aure, ina ka samu yariyar?" Ficewa yayi afalon, su Mamy ma  sallama su ka ma hajiya, itako ta na rike da hannun Nur har suka zo  kusa da Abdallah dan haka Hajiya ta sake cewa "Ina ka samu mata?" Hannun Hajiya ya rike yana duba yadda fatarta duk ta yamushe alamar tsufa ya ce, Hajiya yar unguwar rimi ce, sati daya da ya wuce Allah ya hadani da ita, kallo daya nai mata na ji son ta ya kamani, bata da rawan kai, kuma bata surutu bare ta yi gulmace-gulmace, yar karamar yariya ce shekaranta goma sha bakawai danya ce sharaf, tana so na sosai, ko mutum zan datsa in binni a gabanta bazata fadawa kowa ba" Ciki da fara'a Hajiya tace, "Yo dama ai bata fada ba tun da tana kaunar ka, ai in kaji ana binciko aibu babu babu so" Lasan lebe Abdallah yayi sannan ya ce, "Yauwa Hajiya kin gane kenan, babu tarkon da zai kamani, duk in da aka dana min tarko ina tsallakewa, shiyasa ma Allah ya hadani da kyakyawar yariya" Lumshe Ido Nur ta yi domin ya na lissafin tana jin son yariyar na shiga ranta, kosawa ta yi sosai ya ambaci sunanta, ji tayi ya cigaba da cewa, "Hajiya mun hadu da itane a hanya lokacin da ta taso islamiyya, ta gama secondary bata tsaya yawon biyawa gidan kawaye ba, shi Abbanta daman tsarinsa da yariya ta gama secondary ya aurar da ita ya huta, sabo da bata da bakin kudiri acikin ranta Allah ya hadata dani, ni kuma sabo da Allah na sona ya hadani da ita, a lokacin da ake kokarin hadamin tuggu acikin gidan ubana, idan na yi aure sai munafuki ya cire idonshi a kaina aiko?"

Cike da murna Hajiya ta ce ai kuwa ai dama duk wadda yace tukunyar wani bazata tafasaba to tashi ko dumi baza ta yi ba, Allah ya tabbatar mana da alheri yasa zamu ga ranar, ya sunan yariyar?"

Adaidai lokacin da ya shiga motar ya zauna ya ce "Sunanta Bilkisu.

Da taimako Nur Hajiya ta zauna motar sannan Nur ta rofe motar, tana daga mata hannu fuskarta cike da murmushi, itama Hajiya cike da murmushi take dagawa Nur hannu, bayan sun wuce ta juya cikin gidan ta na me farin cikin da jin Yaya Abdallah ya na yabawa da yariyar da zai aura, kwanciyar hankali ta ji yana shiganta lokaci daya.

*****

Bayan kwana biyu, Nur ce tafe akan hanyarta ta zuwa islamiya, kasancewar yau asabar, ga wani irin sanyi da aka tashi da shi, tafe take akan hanyar cike da nishadi, da zaran ta tuna an tsaida ranar auren Yaya Abdallah take jin wani irin nishadi tun tasowanta ba'a taba yin biki aure a cikin dangin su ba, dan haka tafe take tana kirga sati biyu da aka tsaida, saidai ganinsu take kamar shakara, sabo da tsananin kosawa, bata ankaraba taga wata mota sha gabanta, nan ta

tsaya tana kallonta, duk gilashinta rufe ya ke, bata iya hango komai da ke ciki, bata wani ji tsoro ba, domin uguwar ta su lafiyar yiyiyar unguwa ce, dan haka ta fara kokarin kewaye motar ta wuce. Cak taji an dagata, kafin ta yi wani yunkuri ta ji an wurgata bayan motar tare da jin karan rofe motar, tashi ta yi zaune a rikice, wasu gamza gafzan maza biyu ta gani a gaban motar wadda bata taba ganin su cikin unguwar ba, figar motar suka yi sukabar unguwan aguje, tsoro da firgici ya sa Nur sakin kuka, tare da kokarin bude motar, duk da cewa gudu motar ke yi saidai duk kokarinta ta gaza budewa, dan haka ta shiga magiya, cikin kuka tare da firgici me tsanani akan fuskarta take fadin, "Na shiga uku, ina zaku kaini! Dan Allah ku yi hakuri ku rabo dani makaranta zani" Ko juyowa su kalleta ba su yi ba, zuwa wannan lokacin har sun fita daga unguwar su Nur sun haura sanmn titi, dan haka ta cigaba da kuka tare da magiya, "Ina zaku kaini? Me na yi muku.

07014197556
CIWON 'YA MACE
By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 21-22

Aguje su ke tafiya, duk irin magiyan da ta ke mu su basu juyo sun kalleta ba, dan haka ta daina bige bigen da ta ke ta zauna kawai tana kuka tare da magiyar su yi hakuri su sauketa.
Babu wadda ya juyo ya kalleta, tun ta na gane hanya har aka shiga in da bata ganewa, wannan ya sake daga hankalin Nur, tafiyan kusan awa daya sannan ta ga sun doshi wani katon get, wannan lokacin so tayi ta dauke numfashinta domin ta fara cire rai da duniya, gidane dandasheshen gaske, gani kawai ta yi get din ya bude batare da tasan waye ya bude ba, wannan lokacin raba ido kawai take da busheahen hawaye a idonta. Bayan motar ta faka a cikin harabar gidan matukin motar ne ya sauko da saurin sa, sannan ya bude bayan motar ya ce, "fito"
Jin hausarshi bata fita sosai ta da ga kanta ta kalleshi, baki ne katon gaske, damtsen hannunsa irin na masu da ga karfe, ga wani narkeken cross a wuyanshi, dauke kai ta yi da sauri ta waiga bayanta da take jin motsi, dayan ta sake gani a bayan ta shima da cross dinne a wuyansa, wannan ya tabbatar mata da su din ba musulmai bane, tafiya ta fara, ta na bin bayan daya kamar yadda ta lura abinda da suke so kenan, acikin zuciyarta ta shiga Kiran sunayen Allah.
Banda raba Ido babu abin da Nur ke yi, Cikin wani katun falo suka shiga, mutumin da ke zaune ya daura kafa daya kan daya tabi da kallo, waya ya ke dannanwa har suka durkusar da ita a gabanshi tare da cewa, "Gata" Da sauri ya dago kan shi ya kalleta tare da sauke kafar shi kamar zai taketa.
Ganin ya na kokarin sauke kafarshi tai saurin ja da baya, tare da dagowa ta kalleshi, "A fili ta ce, Innalilahi wa Inna ilaihir raju'un" Ido hudu suka yi da Poul dake tsaye a gabanta ya na mata

kallo me cike da tsana, sunkuyar da kanta ta yi kasa tare da nemo dalilinsa na sawa a dauko mishi ita, ko tantama ba ta yi akan su Mamma da Helen ne da suka musuluntа, nan ta ke hawaye ya fara zubo mata domin ta rasa abin yi, gaba daya jinta take a kidime.

Bata an kara ba ta ji an rike hijjabinta da karfe da alama shirin figeshi ya ke a jikinta, dan haka ta mike da sauri tare da cikuikuye hijjabin a jikinta tana fadin, "Duk abin da zaka min kamin da Hijjabina karka ciremin hijjabi."

Bece kala ba, ta bayanta ya miko hannun sa ya murde na ta duk biyun, cikin kankanin lokaci ya cire Hijjabin yai jifa dashi, bayan ta tabbatar da ya rabata da Hijjabin ne ta fashe da kuka tare da cewa, "Dan Allah ka bani hijjabina, ko kasheni zaka yi ka kasheni dashi a jikina." Tsaki ya ja sannan ya koma gurin zaman sa ya zauna tare da cewa, "Idan na kashe ki ma ai ban huce ba, aikin ku kenan hijjabi-hijjabi, can karshen naki zansa a yi fata fata dashi yanzunan, sai dai bakin ciki yasa ki mutu da kanki, kamar yadda ni ma kika dasa min bakin cikin da zai yi saurin hallakani."

"Babu ruwana, bani bace, su da kansu suka ka zabi hakan, ni ma daga sama na ji labarin." Mikewa ya sake yi a karo na biyu ya fara zagaye Nur tare da fadin, Koma mene ne ke kika sani wannan zai zama Jan kunne ne a gareki, dan da ga yau bazaki kara shiga gonata ba, ko ban shata miki layi ba."

"Wannan shine shata layin na ka ai, da ga yau bazan kara shiga gidan ka ba, dama Mamy ta dade ta na gaya min irin wannan."

Ba irin wannan take gaya miki ba, dan na tabbatar ita kanta da ace ta taba yin tunani irin abin da zai faru dake a yau zai iya faruwa ta dalin na da tuni ta rabaki da gidana, kamar yadda ni ma da ace nasan irin abin da kika min zai faru da tuni na rabaki gidan Koda ace binneki zan yi da ranki."

"Karka lalatamini rayuwa ka kasheni kawai"

"Ko na kasheki ban huceba, gara ki rayu da kunar zuciya, kamar yadda ni ma zan rayu da radadi acikin zuciyata."

"Allah bazai baka sa'a ba kan mugun nufinka akaina ba, Kuma Allah ya isa ciremin hijjabin da ka yi..."

Tun kafin ta rufe baki ya wanketa da Marin me zafin gaske, cikin sauri Nur tasa hannunta ta dafe gurin tare da runtse idonta, jin wann radadin Marin ya tuna mata zabar marin da Abdallah yayi mata kwanaki, yau ga kwatankwacin shi. Bayan zafin ya lafa mata ta bude idonta tare da kallon hannun da ta dafe kuncinta dashi, jini ta gani a hannun da haka ta Kara shafa kuncinta, jini ne wadda ke fitowa daga hancinta, dan haka ta mike a lokacin da Poul ke cewa "Kuje da ita."

Batare da wani bata lokaciba suka fara Jan Nur, ihu ta shiga kurmawa tare da cijewa, saidai duk da haka Saida suka yi nasaran shiga da ita wani daki me dauke da gado, kara rudewa Nur ta yi a lokacin da ta ga sun fara cire kayan dake jikin su, gaba daya su biyun suka cire, ya rage da ga su sai gajeren wando, ganin su manya-manya ta kara firgicewa, kayan makarantar da ke jikinta ta kalla riga da wando, kanta ta shafa dama hijjabi kawai ta sanya batare da ta daura dankwali ba. Hankalinta da maida gurin tika tikan maza dake shirin dufarota hawaye na tsiyaya a idonta take fadin, "Dan girma Allah ku yi hakuri, karku tabani, ko me kuke so mu je gurin Abbamu ya baku, dan Allah karku tabani" ganin suna daf da ita ta tsuguna akasa ta kurma ihu tare da sa hannunta ta kankame jikinta, sai dai duk da haka ji ta yi an dauktae cak, kamar an

dauki riga an yi jifa da ita zuwa gado, dan haka ta shiga fadin, "Allah karka basu dama, ka tai makeni ya Rabbi, ya Allah ka kawo min agaji, dan darajan mazon Allah" cikin karaji take kiran suna yin Allah da manzonsa, gani ta yi dayan ya rike kafafunta yayin da dayan ya kwanta ajikinta yana kokarin fincike rigarta, duk da haka bakinta be mutuba, ihu kawai take tana Kiran sunan Allah.

Duk ihun da Nur ta ke a kunnen Poul, har yanzun ya na zaune a falo kafa daya kan daya, a wannan lokacin duk tabi ta dame zuciyarshi, ba ihun bane ke damun shi, Allah da Annabin da take maimaitawa ne ke hanasa sukune, aduk lokacin da ta ambata sai gabanshi ya yi mummunan faduwa, a hankali ya sauke kafarshi tare da mikewa da sauri, wannan lokacin yaran nasa ne suke bashi haushi domin bega dalilin da zaisa su barta har tana magana ba, dakin ya nufa da saurin sa, ganin shigowansa wadda ke rike da kafar Nur ya waiga ya kalleshi, cike da tsawa Poul ya ce, "Mene ne haka? Wannan yar yariyar ce har zaku kasa make bakinta ku barta taita mana surutu?"

"Oga duk ihun da za ta yi babu me jinta anan ai" Tsaki Poul ya ja tare da yi ma su alama da hannu akan cewa su fita a dakin, cikin sauri wadda ya danne Nur ya sauka tare da daukan kayanshi, shima dayan nasa ya dauka ya fici a dakin, tura kofar Poul ya yi sannan ya fara takowa zuwa cikin dakin tare da balle butirin gaban rigarshi ya na fadin "Ki rufe min baki idan kika sake magana saina zubar miki da hakora."

"Cikin muryanta data fara dashewa sabo da kuka ta ce, "Dan girma Allah ka taimakeni ka barni in tafi agida za'aga na dade."

"Babu abin da ya dame ni" ya fada a lokacin da ya cire rigarshi ya fara kokarin cire agogon shi.

"Addu'a Nur ta cigaba da yi afili, duk da cewa Muryanta ya fara dashewa Amman Yana jinta dan haka alokacin da ya ke kokarin hawa gadon yake cewa, "Ki cigaba da kiran Allah har inzo gurin in same ki, karki daina kiran Allah ki gani."

Gadon ya hau tare fincikar rigarta da alama yage rigar yake son yi bawai cireta ba, yana rike da kafarta yake fincike rigar, tuni ta fara yagewa haka yayi ta farka rigar kaca kaca har har ya ficiketa ajikinta; ya rage daga ita sai bra sai dogon waddon maka ranta, kallo ya bita dashi sosai, har yanzun yana rike da kafarta har wannan lokacin bakinta be mutuba, duk wata addu'a da tazo bakinta yi ta ke, tare da kokarin fincike kafarta, tana cikin wannan halin taji karan barkewan dogon wandon dake jikinta, dan haka ta kara gigicewa tare da fita cikin hayyacinta, alokacin da hankalinta ya dawo jikinta daker ta iya bude idonta, ganinta har yanzu acikin wannan dakin ta furta "Innalilahi wa Inna ilaihir raju'un" jikinta ta kalla, ganinta tube tai saurin jawo bargon ta rufe jikinta tare da waigawa tana kallon dakin kota wanni kusurwa, ganin babu kowa a dakin ta yunkura da nufin tashCIWON 'YA MACE

By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Ido hudu suka yi da Poul yana zaune ya kureta da Ido, cikin sauri ta sake kallon jikinta tare da kara jawo barkon ta na rufe jikinta dashi.
Kallon shi ta kara yi har yanzun be cire idon shi a kanta ba, cikin sauri ta kalli kayan makarantar ta dake barbarke akasa, a cikin zuciyarta ta shiga tunanin tare da sauraran yanayin jikinta, babu wani canji baya ga makoronta da can cikin kirjinta dake mata zafi sosai, hankalinta ta mayar kan Poul ta na mai mishi kallon tuhuma, saidai shi ta rasa gane kallon me ya ke mata. Mikewan shi ya kara fadar mata da gaba, har yanzun dogon wando ne a cikinshi babu riga, rigar da ya cire ajikinsa ya jeho mata sannan ya juya ya sake dauko wani dogon waddon sa ya sake jehowa tare da fadin, "Kisa a mayar dake gida." Kallon kayan ta yi hawaye cike da idonta, sai dai bata jin zata iya saka kayan sam, domin da gani nashi ne, zama ta yi a haka tsayon lokaci, bayan kusan minti talatin ya turo kafar ya na sanye da manyan kaya na shadda kaikace cikakken bahaushe ne, kallonta yayi sannan ya ce, "Me kike jira baki saka kayan ba?"
Tun kafin ya rufe baki tace, "Hijjabina zaka bani."
Kallonta yayi sama da kasa, har yanzun tana zaune a kan gado sannan ya juya ya fita batare da ya ce komai ba. Be jimaba ya dawo tun daga bakin kofar ya jefeta da hijjabin sannan ya zuba ha nunsa cikin aljihu yana binta da kallo.
Ta na daga zaune ta sanya hijjabin sannan ta ture bargon ta gyara hijjabin tare da juyawa ta sauka agadon ta mike tsaye, har yanzu makoronta na mata zafi, shiko Poul ganin ta mike ya ce "Kisa kayan ki fito falo ki same ni." Bin bayanshi ta yi da kallo, duk da cewa ta ji yace tazo ya kaita gida bata wani ji farin ciki ba, domin bata gamsu cewa gidan zai kaitaba, duk da cewa bata ji alamar yayi abin da yayii niyya da ita ba, koda ace gidan zai kaita bawani abin dadi bane agaretadomin ya gana wulakantata bubu sutura ajikinta, kuma gashi yamma ta yi yanzu, dole an nemeta har an gaji, wannan kawai take iya sakawa bayan haka bata hango mafita. Harta taba kofar da zata fitar da ita daga cikin dakin ta ja ta tsaya, jimmm ta yi zuwa can ta juya babu yadda ta iya dole ta saka rigar da ya bata, wandon ta dago tana kokarin sakawa wani irin takaicine ya kamata wadda ya saka yin jifa da wandon, cikin kuka ta nufi bayin dake jikin dakin, tawul din wanka ta dauko ta daura a kugunta sannan ta fito falon. Har wannan lokacin Poul ya na tsaye a falon, gefensa gardawan mazan nan ne ke ta binta da kallo, sai dai tun kafin ta ksa wurin ya sallame su suka fice, tsaye ta yi afalon ganin ya fita ta rofa masa baya, har suka fito harabar gidan, bata wani tsaya kallon gidan ba, bayan motar ta nufa ta bude da hannunta ta shige bayan motar ta zauna, wannan karon da kanshi ya ke Jan motar, tafe su ke hawaye na cika idonta da tana matsewa suna tsiyayowa akan fuskarta, hannu tasa ta share hawayen sannan ta dago a hankali ta kalleshi, toki ya ke hankalinsa kwance, can kasan makoshi ta ce "Ina zaka kaini?" Nur ta yi tambayan tare da tsayar idonta waje guda hawaye na zubowa,
"Gida" Ya fada batare da ya waigo ba. Wannan karon cikin da ga murya ta ce, "Ka sauke ni a nan ma ya Isa."
"Me yasa zan sauke ki anan bayan ba anan aka dauko ki ba?"
"Babu ruwanka da in da aka dauko ni, ni dai na ce ka saukeni anan."
Wannan karon be tanka mata ba cigaba yayi da tafiya batare da ya sake waigowa ba, zuwa can Nur ta sake cewa, "Na ce ka saukeni a nan bana son komawa cikin unguwar nan har abada"
Lumshe Ido yayi batare da ya waigoba, sannan ya ce, "Kofar gidan ku zan sauke ki."
"Banaso, Tun safe nabar gida, gashi yanzun har yamma ta yi ban koma ba, bansan me zance

ba idan na koma gida, sannan jikina babu kaya ta Yaya zan iya shiga gida a haka? ta yaya zan bari su Mamy su ganni a haka, baza su fahimcini ba, ba ni da kalmar da zan gaya musu su gane, ni rayuwata bata da amfani, dama kaaheni ka yi kawai"

"Ke! Ke! Dakata, me aka miki dahar kike cewa rayuwarki bata da amfani, kofar gidan ku zan kaiki dan banga abin da aka miki ba, yariya dake sai ki dinga dagawa manya murya, waye dan ki anan?"

"Ka cimin mutunci kai dinan Poul, kamin tsirara ta hanyar yage suturar dake jikina da karfin tsiya, wallahi in sha Allahu Allah bazai barka ba sai Allah ya saka min bi izininlahi, tun aduniya kafin mu je lahira ya gana maka azabar sa, idan kacika sunanka ka kasheni yau karka barni darai, banza kawai wadda be san me ya ke ba. kuma idan har baka kasheni ba yau ka shiga uku, kuskuren da zaka sake yi a rayuwarka shine barina a raye"

Wani irin kallo yayi mata sannan ya ce, "Ya isa ka, ina nan zan jira abin da zai biyo baya" Duk da haka Nur tabar magana ba dan haka ya rabu da ita be sake kallon in da take ba.

Sosai ya ke jin zafin kalaman ta, saidai ya kasa tanka mata ko yi mata tsawa akan maganar tata, tukin sa kawai ya ke ko sau daya be waigo ya kalletaba, ya na jinta tana ta manganganu wani ya jiyota wani bayajin me take cewaba, dalilin muryanta da baya fita sosai, duk da cewa wani baji yake ba sosai ya kosa ya sauketa domin gaba daya tun da ya kwanta jikinta yaki jinshi cikin rashin nutsuwa me tsanani, kuma har yanzun nutsuwa taki zuwwar masa dan haka ya kosa sosai ya sauketa, misalin karfe hudu da rabi suka shigo cikin layin su ta saman layin ya biyo dalilin sauke Nur da zaiyi kofar gidan su, wannan karon ma sake daga ga murya ta yi ta ce, "Ka sauke ni a anan toh.

Lumshe Ido yayi batare da ya tankaba Kuma babu alamar tsayawa a tattare da shi, dan haka ta sake cewa, dan Allah na ce ka saukeni a nan karka kaini kofar gidanmu, kabarni anan in nemi in da zani bazan iya shiga gida ba a haka."

Tamkar bayajinta haka yayi dan haka Nur ta tsananta Kukanta tare da fadin "Allah ka kawo min mafita, Allah ka taimakeni, ta na addu'ar tana tunani cikin ranta ko meye dalilin sa da zai kaini har gida ahaka ko tsoron iayeyena bayaji" tuna yadda ya hankadata waccen karon gaban duk yan gidan su yasata ta nufi kofar motar iya karfinta take kokarin budewa saidai motar kulle take. Ganin motar a kulle ta daga kai ta hangi kofar gidan su, da alama baki aka yi acikin gidan, dan akwai motoci manya manya guda biyu a kofar, da Kuma maza da mata awurin yayin da wasu ke shiga motar sai dai bata iya gane ko su wanene, nesa da gidan Poul ya tsaya, dalilin ganin motocin da yayi a kofar gidan, waigowa yayi kadan ya ce "Sauka."

Nur kuwa idonta ta shiga rabawa domin son sanin su waye suke kokarin shiga gidan su yanzu, sai dai har suka shiga bata gane kowa ba, motar farkon ce tayo kwana, yayin da ta biyun ta miki layin, a daidai wannan lokacin Poul ya sako ya bude motar, saurin ficewa a motar ta yi tare da tsayawa wurin, kokarin ta domin ganin motar nan ta wuce wadda ke ciki be gantaba, saidai motar Sam taki wucewa har Poul ya zagaya ya shiga ya fiki motar sa a daidai lokacin da motar ta gama yin kawana ta fara tahowa cak motar ta tsaya, Nur ko kokarin boye fuskarta take ta hanyar durkusar da kanta, kafar mace ta gani fara sol ta fito daga motar, ko tantama babu wannan kafar Momy ce, dan haka ta dago kanta da sauri alokacin da Jamal ya ke saukowa da ga motar cikin fada ya ke fadin "Ina kikeje?" Jamil ne yayo kanta shima cikin fada ya ke cewa "Waye wancen ya sauke ki a mota?" Itako Ummy cikin sauri ta rungume Nur ajikinta ta na kokarin runtse idonta ta ji gabanta yayi mugun faduwa dalilin jin jikinta kamar babu kayan

kirki, hannu tasa ta bayanta ta shafa da kyau bra kawai take iya jiyowa dan haka ta dago ta kalli Nur, ganin fuskarta a kunbure ta fara janta zuwa mota, Jamal da Jamil kuwa basu bar Maimaita tambayan da su ke mata ba, Momy da Nur ne zaune a bayan motar, kallo take mata me cike da tuhuma zuwa can tace Nur garin yaya babu kaya a jikinki? Jin wannan yasa Jamal da Jimil juyowa kusan a tare suna kallon Nur a lokacin da hawaye ke zubo mata.

Jamal ne ya ce "Baza ki bude baki kiyi mgn ba?

Jamil ko fadi ya ke wai Ummy kina nufin da ga ita sai hijjabin?

Kasa amsa masa Momy take dalilin hawaye da ya fara zobo mata idonta akan Nur.

Jamal ne ya cije le lebensa sannan yace "idan baki bude baki kinyi mgn ba har nazo gurin nan jikinki zai gaya miki."

CIWON 'YA MACE

By

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 25-26

Ummy ce tai saurin takatar dashi da hannunta sannan ta juya ta kalli Nur ta ce, "Fyade aka miki ko? Cikin sauri ta girgiza kai tare da fashewa da kuka, itako Ummy ajiyan zuciya ta yi sannan ta ce, "Gaya min mene ne ya faru? Garin Yaya Nur? Jikin ki babu sutura kirki, haka kika fita dama? Cikin ma tsanancin kuka ta ce, "Ummy Poul ne, na fito zani makaranta ya turo aka daukeni, kuka ne ya kwace mata dan haka Ummy ta sake jawota jikinta ta rungome a lokacin da Jamal ya ke cewa, "Karyan banza kawai, yanzu nan aka sauke ki a mota sabo da kin rainawa mutane wayau kice wani an daukeki a mota, wadda bashi da gaskiyan ne ya dawo dake? Ko yasa aka dawo dake?, kinje yawon banzaki zakizo kinawa mutane karya." Wannan karon ma dakatar dashi Ummy ta yi ta hanyar cewa "Waye Poul din?"

Jamil ne ya ce, "Ummy ni abin da ya ke bani mamak,i me ya faru ta dawo gida daga ita sai hijjabi? Garin yaya hakan ta faru? Babu ruwanmu da wani can, ita tasanshi mu bamu sanshi ba, hankalin sa ya mayar kan Nur ya ce "Wallahi yau saina zaneki, saina farfasa miki jiki, da alama wannan ba sabon abu bane a wajen ki, tun da har kika iya dawa gida a haka, yar karama dake kin lalata rayuwarki" In da suke shiga shi da Jamal batan suke fita ba, dan haka Ummy ta daga waya ta kitmra Aunty Saratu, bayan ta daga ta mata bayanin a yadda suga Nur sannan ta sauke tana me dakarat da su Jamal daga fadan da suka rufe Nur din dashi.

Cikin kankanin lokaci Aunty Saratu ta fito da ga cikin gida, bude motar ta yi sannan ta kama hannun Nur tana fadin "Sai munyi waya." Binsu da kallo Ummy ta yi har suka shige gida sannan ta dauke idonta tare da share gutun hawayen ta.

*****

"Nur karki yadda Mamy ta ji wannan maganar bare kuma Abbanku, ki yi shiro da bakin ki zansan duk yadda zan yi wajen ganin ba a zargeki ba."

"Amman Aunty ki gayawa Abba yasa a kama Poul, ya cutar dani aunty, bansan yadda akai ya barni ba da kayan makaranta ajikina ya yayagasu ya ganni tsirara Aunty."

"Duk ki daina tuna wannan Nur, idan Abba ki ya kai mishi yan sanda kowa saiyaji wannan wulakancin da aka miki, ko kina sone kowa sai ya ji? Wani ma cewa zaiyi karya ne an miki fyade, sanin haka sai kiga mijin aure ma kin rasashi, Nur ke yariya ce shiyasa kike ganin fada dashi zain yi amfani, kowa cikin unguwar nan yasan  Poul yana da kudi, idan ya ga dama ma zaice sharri kikai mishi, ko ya kashe kudi maganar ta mutu batare da an hukuntashi ba, mu Kuma mun riga muntowa kanmu asiri shiko na mijine, asalima ba musulmi bane, ina abin da ya dameshi, da wannan ya ke gadara, shiyasa har zai kawoki har kofar gida, dan haka kada ki yadda kowa yaji wanna maganar, domin idan har Abdallah ko Bashir wani yaji kinsan zaman lafiya a unguwar nan ya kare."

Hawaye Nur ta share sannan ta ce "To yanzun Aunty shikenan barinshi za'ayi? Ni ko duk duniya ce zata taro nafison a kamashi Aunty, Koda ace yau zai kashe kudi maganar ta kare nafison haka Aunty"

"Nur ke yariya ce bazaki gane abin da nake nufi ba, ni zan nemo mafitar cikin hikima, amman kama Poul babu abinda zai haifar illa zubar da mutuncin gidan nan a karshe ki kasa aurowa"

"Dama Ni bani da burin aure Aunty, Ni ban damu ba, kawai a dauki mataki, in dai dan aure ne bazan yi auren ba" Daure fuska sosai Aunty ta yi domin tuni ranta ya kara baci cikin fada ta ce "Wallahi kiji na rantse idan har kika bari maganar nan ta fita cikin gidan nan sai ranki ya yi mugun baci"

Shishshekar kuka Nur ta cigaba da yi, yayin da Aunty ta ci gaba da cewa "Lokacin da aka dinga cewa ki bar zuwa  gidan baki kikayi ba, sai yanzun da komai ya dame zaki damu mutane"

"Aunty kayana fa ya yagesu a jikina ya min tsirara"

"Ki godema Allah da be lalata miki rayuwa ba sauran kibarwa Allah, shine kadai zai saka miki"

Kuka Nur ta cigaba dayi, sosai kukan ke damun Aunty, ga bakin cikin abin dake cin zuciyarta dan haka ta mike ta fita tare da neman mafita. Dakin Mamy Aunty Saratu ta shiga jiki a sanyaye, ganin shigowanta Mamy ta cire tagumi tare da cewa "Ta gaya miki da ga inda ta ke kuwa?"

Ajiyan zuciya Aunty ta yi sannan ta ce "Poul ne yasa a dauko masa ita, domin yana ganin itace taja ra'ayin yan gidan su suka musulunta."

"Inna ilaihir wa Inna ilaihir raju'un, be mata komai ba dai ko?" Mamy ta yi tambayan ta na gyara zamanta.

"Babu abin da yai mata, tana can ta na kuka wai ita aje a kamashi"

"Gaskiya gara aje ko kotu ne a yi mana iyaka dashi, wuni daya? sabo da ya raina mutane?"

Jimmm, Aunty ta yi sannan ta ce, "Ni kuma sai nake ganin gara a bishi a hankali, Kinga na farko yaron nan ya na da kudi, ga rashin mutunci, uwa uba kuma ba musulmi bane, kinga shi a gurinshi wannan ba abin kunya bane, mu kuwa ya na iya kawo mata matsala."

Jimmm Mamy ta yi Cikin yanayi irin na me nazari, zuwa can ta ce, "To yanzun me ye abin yi?"

"Ni dai abin da nake gani Mamy mu hana Nur fita ko makaranta, kafin mu ga yanayin abin, dan ni yanzun kaina a kulle ya ke, na tsorata ainun, saidai naki bari Nur din ta gane haka."

Ajiyan zuciya Mamy ta yi sannan ta ce "Ai abin tsoro ne Saratu, amma baki ganin kar nan gaba Alhaji yaji Kuma bayan yanzun mun boye masa?"

"In sha Allah komai zai wuce cikin sauki, tunda har ya dauketa ya kuma barta batare da yai mata wani abu ba, ni ina ganin kila ya fahimci babu sanintane."

Cike da damuwa Mamy ta ce "Allah yasa" Mikewa Aunty ta yi ta koma gurin Nur saidai ta

boyewa Mamy a yadda Nur ta dawo gida.

Tun da ga wannan ranar yanayin Nur ya canza, Bata da walwala kodayaushe. Abin da Poul yai mata ya kasa bace mata, kullum cikin kuka take, duk hali da take ciki aunty na sane da ita, saidai ta yi buris da ita, sannan duk wata hanya da zata kadaita da Abban su Aunty ta tausheshi, sabo da gudun karta gayawa Abba.

Aunty da Mamy ne zaune suna Hira, yayin da Mamy take korafi akan rashin sakin jikin Nur, Duk ta rame bata da walwala kamar da, Mamy ce tace, "Ina ganin ya kamata ta saki jikinta zuwa yanzun."

"Kin Santa da son makaranta, wata kila da ace tana zuwa makaranta ta ji saukin abin, na lura da Nur ma dai matsoraciyace."

"Dole ta ji tsoro Saratu, Kuma har yanzun babu matakin da aka dauka fa, Ni kaina banason ta fita a yanzun, ina ganin Dole mu gayawa Alhaji fa, domin a yi mana iyaka dashi, duk ranar da bamu ganta ba shine, ina nufin idan anje kai karar sa kawai muna zargin zai sacetane. Idan ba aka sake nemanta aka rasa ahine."

Cikin gamsuwa da maganar Mamy aunty tace "Kuma fa hakane, me yasa ma ba ai haka bane tuntuni, ni lokacin kaina kullewa yayi."

"Abin da yafi dacewa kenan idan har Nur zata ci gaba da karatu."

Shiru aunty ta yi tsawon lokaci, zuwa can ta ce, "Gashi yanzu bikin Abdallah sati daya ya rage, sai a bari bayan bikin sai a gaya mishi ko?"

"Amman sai dai mu toshe kunne, don zai yi fada da ace mun yi magana tun farko da yanzu an gama maganar"

Shigowan Abdallah ya sa duk suka maida hankalin su kanshi, Bashir ne a bayan shi, har suka zauna kallon su Aunty take tana kokarin ganu damuwarsu, ita ko Mamy su na zama ta ta ce, "Lafiyar ku?"

Bashir ne ya shafa kai sannan ya ce, "Munje wurin Abba ne akan maganar auren Abdallah...."

"Me ya faruwa akwai matsala ne?" Mamy da Aunty suka fada da saurin su"

Kawar da kai Abdallah yayi, yayin da Bashir ya ce "A'a ba matsala bace, kawai dai mun neme da adan Kara bikin ne zuwa gaba."

Wannan karon ma Katseshi Mamy ta yi da cewa, "Sabo da me?"

Cikin sauri Bashir ya kalli Abdallah ya ce "Ka mata bayani mana."

"Kawar da kai Abdallah ya sake yi dan haka Bashir ya ce "Mamy kinsan be wuce saura sati biyu ya wuce makarantar ba, Kuma karatun nan ya na da matukar mahimmancin, shine yake ganin gara a daga har ya dawo."

"Ya dawo Ina? Mamy ta tambaya tana kallon su daya bayan daya."

"Karatun mana Mamy, kinsan fa zai iya daukan shekara daya batare da ya dawo ba." Cikin sauri Mamy ta daga mishi hannu cikin fada ta ce, "Baza'a daga ba Baahir, ai yasan da maganar karatun ya fara neman auren, sai yanzun da aka gama magana biki ya rage sati biyu ka bijiro da wani salo?"

Kasa Abdallah ya yi da murya ya ce, "Mamy ba haka bane, acikin dangin yariyar ma akwai waddanda basa son a yi auren yanzu, Kuma ni tunani na yi, nauyin zai min yawa agarin da bansan kowa ba, ni ba wani karfene dani ba, ga yariya karama, nauyin zai min yawa Mamy

kilama in kasa karatun da ya Kaine, kamar fa mutum ne zai yi tafiyan kasa mai nisan gaske, sai kuma ya dauki buhun shinkafa ya goya, ya kamata ku duba wannan al'amarin.

Tun da ya fara maganar Mamy ke Kallon shi, zuwa can ta ce, "Me Abban ku ya ce?" Wannan karon Bashir ne ya ce ai yaki amincewa Mamy bema bari mun gama mai bayani ba."

"Nan din ma haka ne, baza'a daga ba, idan an daura auren kaga babu Inda zaka ajeta acan kana iya barinta anan, ka tafi abinka Kuma da kake cewa karama ce dacan bakasan da kankantar tata ba sai yanzu kasan dashi?, To gudun karka yarda karamin buhun shinkafa a hanya sai ka barshi agida, auren dai sai an daura"

Wannan karon ma kasa ya sake yi da murya ya ce, "Nifa Mamy abin da yasa na ce haka, ina ganin zata iya jirana ne har indawo sai a yi"

"Toh bazata jirakaba, ai mace bata jiran na miji sai dai namijj ya jira ta, tun da iyayenta sun baka banga dalilin wannan maganar ba."

"Shikenan Mamy sai ta zauna anan din har na dawo."

Aunty ce tace "In sha Allah  za'asan inda za'ayi ma ka tafi da ita."

Mikewa Abdallah yayi yana kokarin fita Yana cewa ta dai zauna anan din.

Bayan sunga ficewan shi Aunty tace "Wai meke damun Abdallah ne?"

Bashir Mamy ta kalla sannan ta ce "Me kuke shiryawa ne?"

"Ni fa Mamy babu ruwana, yanzu yaje har gida ya daukoni, ya ce mini ya tura Auwal wurin Abba da maganar amma sai Abba yace yazo da kanshi, shine fa ya ce nazo na rakashi."

"Sam ya Bata wayon shi, gaba daya ya siremin, a da nafi dayya dashi akan kowa a gidan nan, yanzu duk ya zama wani iri, bashi da gaskiya, shiyasa baya rawan jikin auren, idan aka barshi haka zai zauna tun da azuciyarshi babu Allah, afili ya ke mutum. Sabon Allah ya sa a gaba"

"Kashhh, Mamy dan Allah ki daina mishi irin wannan tunanin." Bashir ya fada tamkar zai fashe da kuka, itama Mamy cikin bacin rai taci gaba da cewa, "Ai gaskiya ne Bashir, ni ma ba farin cikin fadan nake ji ba, kafin kayi da na wani gara ka farayi da naka, neman mata ya ke yi, dake munafukine a haka bazakace ba, shiyasa baya daukin auren sam."

Tsaki aunty Saratu ta yi sannan ta ce "Wlh bana son kina irin wannan maganar, ba kowa bane ya hada wannan sai Nur, Kuma bata kyautaba sam, yanzu gashi da ga ya dan fadi ra'ayinshi kince neman mata ya ke, ni dan Allah ku goge wannan zargin akanshi, aure zai yi, kar matar tazo ta ji ana cewa neman mata ya ke, ta fara zarginshi kamar yadda Kuma kuke zarginshi, kai Kuma Bashir ka jawa Nur kunne dan aure zaiyi"

Mikewa Mamy ta yi tana kokarin barin falon take cewa "Baza dai a dagaba, tun da shi ya kawota da kanshi ba wanine ya nemo masa itaba bare ya ce dole aka mishi, kuma iyayen yariya basu kawo wata matsala ba dan haka duk gidan nan babu mai sauraron shi."

"Ai shima ba cewa ya yi  baya sonta ba, shawara ya kawo tun da kuma baku fahimcishi ba ya bar maganar"  Mamy tabata tsaya ta gama sauraron Aunty ba ta shige dakinta.

***

Nur ce kwnace tsakiyar gadon aunty tun daga ranar da abin ya faru Bata sake fita waje ba; bare ma taje makaranta, rashin karfin jikinta yasa akace ma Abba bata da lafiya dan haka ya sanar a islamiyya da boko, tun a ranar Abba ya bada kudi akaita asibiti, har yanzun a tunanin sa tana shan magani, ayanzun Nur ko son tunawa da Helen bata yi, sabo da abin da yayanta yai mata sosai takejin ciwon abin, tare da tunanin hanyar da zatabi a hukunta poul akan abin da yai

mata, tun da aunty ta hana ta agayawa Abba Nur bata fasa gayawa Allah ba, duk sallalolinta guda biyar saita ambaci sunan sa, tana mai zubar da hawayen dakaicin.Ajiyan zuciya Nur ta yi sannan ta tashi zaune zuciyarta cike da kuna, Aunty Saratu ce ta shigo dakin ganin yadda Nur ke cikin tunani ta ce, "Ke har yanzu bazaki saki rankiba ko, to ki je wani ciwon ya kamaki ke kika sani."

Ba tunani nake ba kaina ne ke ciwo, kallonta kawai Aunty ta yi ta kauda kai tare da fadin, "Mun yi magana da Mamy yanzun, bayan bikin Abdallah za'a gayawa Abban ku, don a yiwa tufkar hanci, sai kici gaba da zuwa makaranta abinki."

Ajiyan zuwa Nur ta yi tare da cewa "Yauwa Aunty, har naji dadi"

Wani irin kallo Aunty ta mata sannan ta ce "Wawiya kawai, wato ke koma menene zai faru a gayawa Abba."

Dan murmushi Nur ta yi sannan tace "Wallahi yafi Aunty, ko Yaya Bashir nasan bazai yadda ba"

"Hmmm Nur kenan, Ina gargadin ki karki bari mazan gidan nan suji, ta shi ki gayara gadon, Abdallah yamin waya gashinan zuwa shida amaryarshi"

"Nan gidan?"

"Eh" Aunty ta bata amsa, mikewa Nur ta yi tare da fadin "Haka ake yi aunty? Ai ba'a daura auren ba ko?

"Nace ya tambayo labar takalminta ya ce min gasunan zuwa, kedai tashi ki gyara gadon, zamani ne ai."

Cike da farin ciki Nur ta amsa take taji duk wata damuwarta ta yaye, jin amarya Yaya Abdallah zatazo yau dinan kuma gashi Za'a gayawa Abba abin da Poul ya mata.

Gadon ta gyara yayin da Aunty take fitowa da dakalma sabbi fil wadda Amarya zatazo ta duba, Sallama da sukaji bakin kofa yasa suka dago a tare suka kalli kofar, Helen ce tsaye abakin kofar, dan haka aunty tai saurin sakin ledan dake hannunta sannan ta taho cike da fada ta tare Helen tare da cewa, "Fice kibamu wuje, me ya kawoki?, Baki da labarin abin da Dan uwanki yaima Nur ne? Maza ki fice karki kara shigowa gidan nan."

Jikin Helen a sanyaye ta ce "Aunty nazo ganin Nur ne, kwana biyu bataje makaranta ba na gayawa Mamma ta ce inzo inga jikinta."

Lumshe Ido aunty ta yi domin da Alama Helen basan Abin da ya faru tsakanin yayanta da Nur ba, Nur dake bayan Aunty ne ta mike, tahowa ta yi wurin ta riko hannun Helen tana fadin "Shigo ciki."

"Bayan Nur tabi tana satan kallon Aunty, bakin gadon Aunty suka zauna yayin da Aunty ta juya ta bisu da kallo tare da mamakin Kaunar da ke tsakanin  Nur da Helen wadda a yanzun ta koma Zainab, ficewa Aunty ta yi ta basu guri saidai acikin zuciyarta Allah Allah take Helen din tazo ta fice a gidan.

Bayan Helen sun gaisa da Nur ta ciro waya a yar kamar jakar dake hannunta tare da cewa "Mamma ce tace idan nazo in kirata ku gaisa" cike da fara'a Nur tace to "Kirata to."

Dana wayar Helen ta yi sannan tasata a kunnenta tare da fadin "Gata"

Amsan wayar Nur ta yi tasa a kunnenta tare da Sallama, batare da ta jira an amsa sallaman ba ta shiga cewa, "Mamma kwana biyu bana fita, Kuma ko na fito bazan kara shigowa gidan ku ba, Poul ya zargeni akan komawar ku  addinina, Kuma har yasa an dauko masani yaci mun mutunci, Mamma fashewa Nur ta yi da kuka tsayon lokaci tana yi Cikin wayar, jin aba'ace komai

ba ta sake cewa, Mamma!

Gabantane yayi mummunan faduwa dalilin jin Muryan Poul da ta yi Cikin wayar....

CIWON YA MACE

By

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

PAGE 27-28

Cikin sauri ta dago wayar ta kalla sannan ta sake mayarwa kunnenta batare da tace komai ba.

Muryansa ta sakeji ya ce, "Me yasa bakya zuwa makaranta? ko kina tsorona ne? Kin fada a gida?"

Duk tambayan babu wadda ta amsa aciki, jin shirun yayi yawa ya sake ya cewa, "Ki fito kije makaranta abin ki, babu abin da zan miki, na gane cewa babu sa hannun ki, na gano bakin zaren, kuma komai zai dawo kamar baya, yanzun dai abin da nake so dake ki yafeni, kuma ki fito dan Allah, ina kofar gidanku, akwai abin da zan gaya miki..."

Mikewa Nur ta yi a fusace ta jefawa Zainab wayar tare da cewa, "Idan kin je kice mishi bazanzoba, bayan wancen karon ya daukeni a titi yanzu zaizo har gida ya daukeni sabo da yaga ba'a dauki matakiba?" Cikin sanyin murya Zainab tace, "Ba daukarki zai yi ba Nur, ya ce mini hakuri zai baki, ni abin ya fara daure min kai, kulum na dawo makaranta sai ya tambayeni mun hadu dake, idan nace bamu haduba ya fice, anjima ya sake tambayata, yanzu Kuma kawai ya ce mini inzo muje gidanku a baki hakuri."

"Ya gaya miki abin da ya mni?

"A'a Ni yace min ma ko kince zaki gaya min kar in saurareki, amman dai in baki hakuri."

Wanni irin kallo Nur taiwa Zainab sannan tace, "To yanzun in gaya miki ko baza ki saurareni ba?"

Jimmm Zainab ta yi sannan ta ce, "Karki gaya min tun da ya baki hakuri, yanzun kizo muje yana jiramu na ga kamar ma bashi da lafiya ne."

"Ai yanzu ya fara ciwo, aduk sanda na saka goshina akasa saina roki Allah ya saka min, idan kinje ki gaya mishi bazai warke ba ya dinga ciwo kenan daga nan har ranar mutuwanshi, kuma tunda kin goyi bayanshi karki sake zuwa gidanmu, ki gaya mishi ya shirya zuwa kotu bayan bikin Yaya Abdallah, sai anbi mini hakkina akan abin da ya yii mini...

Zainab bata cire idonta akan Nur ba saida ta ji wayar na ta sake daukan kara, ganin Poul ne ke kiran ta juya da nufin fitowa a gidan dan tasan ya gaji da jirane. Zainab na fita Aunty ta shigo dakin fuskarta dauke da murmushi, dakuwa taiwa Nur tare a fadin "Wai ni Nur waye ke koya miki magana haka? Wani maganar idan kika yi saina tsaya na kirga shekarun ki, me yasa zaki yi fada da kawarki tun ta kuruciya akan wani.?"

"Aunty ba wani bane yayan tane ai."

"Eh, be dace kiyi fada da ita ba..."

"Aunty cewa fa yayi wai yana kofar gida inzo kinga har a gidan ma zuwa zai ya daukeni sabo

da yaga ba a kamashi ba ranar..."

"A'a Nur bana tunanin haka, ai da kinje ba abin da zai miki."

"Aunty Poul din? Ni ko ganin shi banson na kara yi, itama Zainab din ba ruwana da ita har mamma"

Dariya Aunty ta sake yi tana kallon yadda Nur ke share hawaye. Bayan ta gama karewa Nur kallo ta tashi ta isa bakin window, labulen ta daga sannan ta leka har yanzun Motar poul na tsaye a kofar gidan, yayin da helen ke tsaye abakin motae tana magana. Dariya Aunty ta yi tare da sakin labulen sannan ta dawo daf da Nur ta zauna tana kokarin boye murmushinta.

****

"Kisan duk yadda za ki yi ki fito min da ita, ina son in gantane kawai."

"Bazata fito ba fa, maganganu take marasa dadi ta ke ta fada, kuma tace na fada maka"

"Karki gaya mini, amman ki koma ki bata hakuri tazo."

"Ta ce fa bayan bikin yayansu Abbanta zaikai ka kotu akan abin da kai mata." Shiru Poul ya yi tsayon lokaci, zuwa can ya shafa kanshi tare da fadin, "Ban mata komai ba, idan sun kaini kotu zan iya kwatan kaina, ni yanzun damuwata kawai kizo min da ita."

Juyawa Zainab ta yi domin ta rasa yadda zata yi ya hakura, dan ita bawani saba magana dashi ta yi ba, ko da ta koma nacin duniya taiwa Nur ta ki zuwa dan haka ko da ta koma kasa magana ta yi tai tsaye kawai tana wasa da yatsunta. Shima Poul kallo ya kare mata sannan ya figi motar sa ya wuce, ganin ba gida ya nufa ba Zainab tai a jiya zuwa sannan ta koma gida mamaki cike da zuciyarta.

Itako Nur shigowan Abdallah ne ya dauke mata damuwar maganar Poul, bayansa kawai take kallo domin ta masifar kosawa ta ga matar tashi, sai dai har wannan lokacin bata hango kowa ba domin Abdallah dogo ne sosai, mikewa ta yi da sauri ta nufi tahowa tare da leken bayanshi wata zarkadediyar budurwa ta hanga kanta sunkuye dan haka tai saurin zuwa ta rungumeta tare da fadin "Oyoyo." Cike da fara'a suka rungumi juna sannan suka taho zuwa cikin, tuni Abdallah ya zauna binsu da kallo kawai yake, sosai Nur ta bashi mamakin ganin in da take ta farin ciki da ganin yariyar da zai aura. Itama Nur bakin gadon ta koma tana kallon yariyar, Aunty taita bata takalmi tana gwadawa har ta debi wadda take so, tare da Yaya Abdallah suka zaba, da kanshi yake saita mata takalmin har ta gama, ga dukkan alamu yana son yariyar sosai, dan baya miti daya batare da ya kalleta ba, yayin da yake yawan kai bakinsa saitin kunnenta yai mata magana kasa kasa, idan zata bashi amsa kuwa kunnensa ya ke kaiwa gurin bakinta, bayan ya gama saurara yayi murmushi sannan ya koma gurin zaman shi. Har suka bar gidan Nur murmushi take domin sun matukar bata sha'awa, kuma sun dace da juna sosai, har mota ta raka su bayan sun tafi ta dawo gida cike da fara'a. Afalo ta samu aunty na bawa Mamy labarin Bilkisu, yayin da mama keta fara'a "Wlh bakiga yariyar ba kyakyawa da ita, kuma wallahi d'aya sharaf da ita, dan bata wuce Nur ba"

Cike da fara Mamy tace "Eh lallai karama ce tun da kika kwatanta ta da Nur"

"Wlh Mamy har dan jikin nasu ma, mama kawai Nur zata fita, sai Kuma dan haske kadan, gaskiya na yaba da yariyar ga tarbiya."

"Wannan karon ma Murmushi Mamy ta yi tare da cewa "Toh ai shikenan, Allah dai ya zaunar dasu lafiya."

"Amin" Aunty ta amsa, ita ko Nur tunda taji aunty ta ce wai tafita nono maganar da Abdallah yayi kwanaki ya shiga dawo mata, in da ya ke cewa ita da ga han hangota hanci ake fara gani

da wasu abubuwa, kawar da zanjen ta yi tare da fadin "I dan ma haka yake nufi Allah ya Isa."
Mamy da Aunty wuni ranar kayan akwatin sukaita hadawa dan gobe za'akai, kafin yamma sun gama zuba duk abin da ya dace. Misalin 10:37pm Abba da Abdallah ne tsaye a tsakar gidan, yayin da Abba kecewa, "Bana son in sakejin maganar daga biki, ai kaika nemo yariyar nan ba wani bane ya nemo maka, dan haka banga dalilin dagawaba, idan baka da wajen da zaka ajeta acan kana iya zuwa ka gano garin in yaso daga baya kazo ka sauki matarka."
Cike da gamsu Abdallah yace "Shikenan Abba, dama..." Kasa karawa yayi dalilin hango budurwar yariya tana shigowa gidan, ganin In da Abdallah ke kallo ya sa Abba kallon waje tare da fadin "Waye nan?"
Cak ta tsaya tare da cewa "Ni ce."
"Kece wa?!" Abba ya fada cikin tsawa tare da har gowa "Zainab ce Abba"
"Wacce Zainab din?!" Abba ya sake tambaya tambaya cikin kosawa, karasowa ta tayi tare da fadin, "Kawar Nur ce."
Kawar Nur? Cikin rashin fahimta Abba ke matsawa gabanta Yana mai jafa mata tambaya, ganin haka Abdallah ya ce, "Yariyar nan ce kawarta kanwar Poul" Dakatawa Abba yayi tare da cewa "To to na ji, lafiya dai ko?"
"Lafiya lau Abba."
"To me ya fito dake da dare haka" Abba ya fada yana duba agogo dake daure a hannunsa.
"Abba nazo wurin Nur ne zan amsa litrafina....
Batare da Abdallah ya bari ta rufe bakiba ya ce ta yi bacci ai yanzu, haba agogon hannun sa ya kalla sannan yaci gaba da cewa, "Shadaya ne take shirin yi fa.?"
Kawar da kai Abba yayi sannan ya ce "Ki daina fitowa da daddare haka, kai Abdallah rakata ciki, idan Nur din ta yi bacci ka bata jakar Nur din ta dauki abin da take so....
CIWON 'YA MACE
By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 29-30

Gaba Abdallah yayi badan ransa ya so ba, saidai suna zuwa afalo ya nufi hanyar dakinsa batare da ya ce da ita komaiba.
Aunty dake zaune ce ta kalli Zainab tace "Ke Kuma lafiya?"
Yadda ta gayawa Abba haka ta gayawa Aunty saidai ita Aunty bata yaddaba, dan haka ta ce "Kin ga Zainab Nur ta dade dayin bacci, ku yi hakuri sai da safe." Bayan tafiyar Helen Mamy ta kalli Aunty ta ce, "Yariyar nan fa inaga sai an rabasu da Nur Kinga dan uwanta ba kirkine dashi ba." Kin kula zancen Aunty ta yi da cewa "Ita ko tsoron daren ma bata ji kareke maganar ta yi tana kokarin mikewa tare da yiwa Mamy sallama ta shige daki.
Itako Mamy da abin ta kwana a kasan ranta, burinta kawai a gama bikin Abdallah a dauki matakin raba su da Zainab domin kada hakan ya jawo wata matsalar. Nur ma bata da burin da

ya wuce asanarwa Abba, domin zuwa gidan da yayi yasa ta sake tsorata, domin gani take tana fita za'a sake dauketa. Washegari da misalin karfe bakwai Zainab ta sake shigowa gidan, da Sallama abakinta, Aunty bataji mamakin ganinta ba, amman Mamy har Saida taji cikinta ya murda domin dai Zainab Bata saba musu irin wannan zuwan ba, bayan ta gaida su Mamy Aunty ta nuna mata dakinta da Nur din ke ciki dan haka ta nufi dakin, har ta shige bakin Mamy na bude sabo da mamakin da ta shiga, ajiyan zuciya ta yi sannan ta ce da Aunty "Ni fa Ina jin tsoron shigowan yariyar nan gidan nan."

"Karki wani ji tsoro, jiya da tazo na tsinci maganar su, Ina tunanin Poul din ke turota ta bawa Nur hakuri." Cike da mamaki Mamy ta ce, "A yaushe kikaji hakan? Bayan jiya sanda tazo Nur ta yi bacci" "Ai tazo da rana" aunty ta fada tana kallon fuskar Mamy. Shiru Mamy ta yi tsawon lokaci sannan tace "To me kika fahimta game da hakan?"

"Nifa Ina ganin kila yayi tunani ne ya ga be kyautaba tunda har ya sako kanwarsa acikin maganar." Har yanzun fuskar Mamy da mamaki tace, "To me Nur din tace?

"Ai yar taki ba baya bace Mamy, domin har kawar tata Bata bari ba jiyan, tatas ta mata..."

Katse Aunty Saratu Mamy ta yi da cewa,"Ta min daidai, wannan shine sanin ciwon kai, shiyasa a kullum Nur Kara shiga raina take, duk da karamar yariya ce ita, amman tasan abin da ya ke daidai da Wanda ba daidai ba, ko yayansu bazai nuna mata sanin ya kamataba, wautanta daya da nake ganin daukar da take yi zata iya canza komai."

"Hmmm Mamy kenan, dan dai tana kawo miki tsegumin ya sa zakice tafi Abdallah sanin ya kamata, a dai dinga tunawa da baya, dan mutun ya yi kuskure sau daya be kamata a manta da alherinsa na baya ba, dan ko ita Nur din ma dan ana mata uzurine amman itama itama ai da sai asa zargin kanta, Mamy batabi da kan zance aunty ba domin dama tasan bata cika son ana fadan laifin Abdallah ba.

****

"Jiya nazo da dare kina bacci"

Cikin kawar da kai Nur ta ce "Lafiya?"

"Lafiya lau." Juyowa Nur ta yi suka fuskanci juna sannan tace "Na ji kince jiya kinzo na yi bacci?"

"Eh na ga Abba da Yaya Abdallah a tsakar gida sukace kin yi bacci."

"Amman me kikazo yi a daren nasan dai baki taba zuwa gidan nan da daddare ba." Ajiyan zuciya Zainab ta yi sannan ta ce "Ai nima baki taba cewa babu ruwanki dani ba sai jiya, kasa bacci na yi shiyasa nazo in baki hakuri."

"Hmmm haushi kika bani, kinki tsayawa kiji abin da zan gaya miki akan dan uwanki, ni abin da yabani mamaki ma har yaushe kuka shirya da har zaki goyi bayan shi, alhalin kinfi kowa sanin bashi da kirki, na fita fa zani makaranta ya turo aka daukeni a mota, wasu dirka dirkan maza wallahi duk daukata garkuwa zasuyi dani,  amman muna zuwa gidan abin da ya yi mtatukar bani mamaki sai na ga Poul ne, yasa a dauko ni akan zargina da yake akan caza addinin ku."

Zaro Ido Zainab ta yi cike da mamaki ta ce, "Amman agida be nuna zai yi hakanba sam, ki yi hakuri Nur..."

Katseta Nur ta yi Cikin fashewa da kuka tana me cewa "Allah ne kawai ya kubutar dani don so yayi amin fyade... "

Zaro Ido Zainab ta yi a karo na biyu sannan ta tafi dogon tunani yayin da Nur ta cikaba da sanar mata duk abin da ya faru cikin kuka bayan ta gama raira Kukanta ta dago ta kalli Zainab

da idon ke cike da kwalla ta ce, "Kuma wallahi bazan yadda ba, bazan taba yafe mishi abin da ya min ba, in Allah ya yadda sai yaga sakamakon, hakkina bazai taba barinshi ya zauna lafiya ba"

Cikin yana yin irin na wadda yai nisa a tunani Zainab ta ce "Amma kinsan mene ne?, duk da cewa ni dai be gaya min abin da ya faru tsakanin ku ba amman kwana biyun nan cikin damuwa ya ke sosai Nur, kafin jiya yata zama a gida baya zuwa ko ina, yana gefen su, wallahi Nur irin masifar da ya ke mana saidai mu jiyo yana yima matar shi, itama cikin damuwa take tunda ta fita jiya har yanzun Bata dawoba, yau kuma sai gashi ya shigo gefenmu yana tambayana ke"
"Sabo da yata nemana ya kamani be ganni ba? Ai tun da ga ranar Ina cikin gida babu Inda nake zuwa, Allah bazai bashi nasara akainaba"
"Ba haka bane Nur, zuwan da na yi jiya da daddare wallahi har na yi bacci ya tasheni, wai in kai miki wayan, na ce ai darene yanzun amman ya ce muje ya rakani, tare mukazo har nan kofar gidan." Wannan karon Nur ji ta yi kamar an buga mata wani abu akai, dan haka ta tsaya tai shiru tsayon lokaci zuwa can ta ce "To me zai ce min? Idan ma hakuri ne karya bata bakinshi dan bazan hakuraba"

Cikin sanyin jiki zainab tace "Hakuri zai baki mana Nur"
"Wallahi Bazan hakura ba, tsirara fa ya mini, ya yayyaga kayan makarantar dake jikina duk suka fatantake, fyade kawai yaso yimin"

"Ai nace be yi daidai ba Nur, amman Koda ace bazaki hakura ba ki tsaya kiji mai yake son yace miki a cikin wayar nan, idan ya fada abin da ya ke son fada ba shikenan ba, ai ba lallai dan kinji ki yadda ba, kuma abin da kikace na fada mishi jiyama yaki bari na fada mishi, yanzun barin kirashi na baki dan ko yanzun fa shine ya turoni bazan boye miki ba, bakiga yadda ya rikeceba." Wanni irin kallo Nur taiwa Zainab sai dai a wannan karon ta fahimceta dan haka da taga Zainab ta fara danna waya tace "Inazuwa barin je na tambayo Aunty"

"Basai kin tambayeta ba Nur, ai ni Ina sonne mu ji menene zaice dahar ya damu haka, dan ni nafara yin wani tunani akanshi, Amma da kika gaya min abin da ya faru na shiga rudu, jin abin da zaice yanzun shine zaisa mu gane in da ya dosa." Karake maganar Zainab ta yi tare da mikawa Nur wayar, amsa Nur ta yi badan ranta yaso ba ahankali tasa wayar a kunnenta kamar jira ake aka amsa.

Gyaran murya ya fara yi tare da cewa cikin wayar "Helen ta amsa? Bazan Nur tayi dashi tsayon lokaci, ahankali ya sake cewa "Helen bakyajina?" Wannan karon ma bata ce komai ba dan haka ya kashe wayar, jin an kashe wayar Nur ta sauke tare da cewa "Har yanzun be daina ce miki Helen ba?"

"Ki daina sakashi a lissafi Nur, me ya ce?"
"Ni banyi magana ba kiran ki yaita yi ya gaji ya kashe" Nur ta fada cikin nuna ko in kula, Kiran da aka sake yima wayar ya yasa Zainab saurin dagawa tare da cewa "Na'am, eh itace ta dauki wayar ai" Zainab ta fada cikin wayar sannan ta sake mikawa Nur akaro na biyu.

Wannan karon tana sa wayar a kunnenta a jiyan zuciya ta ji yayi sannan yace "Nur!" Kara hade fuska ta yi batare da ta amsa ba, kasa ya yi da murya sannan ya ce "Ki yi hakuri kinji? Dan Allah ki yafeni." Wani irin haushine ta ji ya turniketa, tsintan kanta ta yi tana cewa "Bazan taba yafe maka ba, in sha Allah sai Allah ya saka min, tun a duniya zakaga sakamako."

"Nur kijini mana, tun da nake a duniya ban taba yin wani abu na yi dana sanin yinshi ba kamar yadda na yi akan wannan, da kinsan halin da nashiga akan wannan abin da nayi da kin

tausaya mini."
"Ni ko wuta a ka hura aka jefa ka aciki bazan tausaya maka ba."

Runtse ido Poul ya yi sannan ya ce "Ina son ki fahimci Ina cikin damuwa ne, maganar da kike fada kuma nasan zafin zuciyane ke saki fada, na yi kuskure kuma ina cikin lokacin nadama da damuwa"

"Allah ya karo maka ita." Nur ta fada cike da tsiwa. Wannan karon ma runtse Ido Poul yayi sannan ya ce "Ki yi hakuri, ki kuma fito ki je makaranta, zaman ya isa haka"

"Abin da Kuma ka min fa?"

Nafiki damuwa akan wannan, domin saka kaina nayi a cikin matsala batare da na sani ba, bana iya cin abinci bare na yi bacci, ke kuwa kinga kina bacci, dan Allah kibarni da wannan din ma kawai ya isheni."Shiru suka yi tsayon lokaci jin batace komai ba ya sake cewa "Nur kina jina?"

Jin yadda ya ke furta sunanta yasata lumshe ido tare da cewa "Kaika rada min sunan?"

Kamar bazaice komaiba zuwa can yace "A'a bani bane, yanzun dai kiyi hakuri."

Sauke wayar ta yi batare da tace komai ba, domin dai batajin zata iya amsawa cewa ta yafe duk da cewa Poul yayi matukar bata mamaki domin ko kadan babu alamar yaudara atare dashi yayi laushi sosai, da alama da gaskene yayi nadamar, dan haka sosai abun ya shiga bata mamaki, domin mutumin da yake magana da ker yau shine ya ke kwantar da murya, muryan Zainab ya dawo da Nur hankalinta wurin, inda taji tana cewa "Gata nan" jimmm ta yi sannan ta juyo ta mika Nur wayar saidai juyin duniya Nur taki amsa, dan haka ta maida wayar kunnenta tare da cewa "Taki amsa" sauke wayar Zainab ta yi Cikin yanayin damuwa ta kalli Nur da har yanzun fuskanta ya ke a daure, tsayon lokaci ta dauka tana kallonta zuwa can ta mike batare da ta ce komai ba ta nufi kofar fita, cikin sauri Nur tace "Tafiya zakiyi babu sallama? Kenan kinga laifina?"

"Cak Zainab ta tsaya tare da cewa to yaya kuke son na yi, shi yana ganin laifina ke kina ganin nawa bansan yadda Zan yi ba"

Ki rabu dashi ki daina kulashi, ko ya sake miki maganata kice mishi Abbamu ya hanaki shiga gidan mu." Kallon Nur Zainab ta yi sosai sannan ta dawo cikin dakin tace "Wallahi ko haka nace mishi bazai hakura ba, dan bakiga yadda ya damu bane, yanzun ma bakiji yadda ya rufeni da fada ba wai ai ke kawatace, me yasa zan kasa shawo kanki, ni kun sani a tsakiya."

Jimmm Nur ta yi zuwa can ta ce "Wai wanni irin Kaine ya ke son ki shawo, wai shi so ya ke sai nace na yafe?"

Jawo Nur Zainab ta yi suka koma suka zauna sannan tace, "Ni fa a tunanina ko kice kin hakura akwai saura, ni dai na shiga uku."

"Ban gane akwai saura ba?
"Toh Ni ai gani nake kamar Poul son ki ya ke yi."

Cikin sauri Nur ta zare idonta waje tare da dafe kirji tace "So?! Son lafiya"

"Eh mana, wallahi da alamar son ki ya ke, duk yabi ya damu, yanayin shi ya canza, wannan abin da yake ya wuce son ki yafe mishi, ni Ina tunani badan ya na sonkiba ko yayi nadama bazai baki hakuri ba."

"Innalilahi wa Inna ilaihir raju'un" Nur ta fada sannan ta ce "Ta Yaya hakan zai kasance alhalin Poul ba musulmi ba ne, Kuma ko da ace musulmine wallahi Bazan aureshi ba, ni bama shi ba gaba daya babu wata soyaya a raina karatuna zanyi, duk lokacin da na gama in samu koma waye in aura."

"Ni dai da ace zan baki shawarata Nur ki bari kiji mai zaice miki." Mikewa Nur ta yi tsaye tare da cewa, "Ai indai dan wannan ne gara ya barshi a ranshi, ko kasheshi zai yi gara ya kasheshi bazan taba bari mu haduba barema ya furta min."

"Wai Nur bakijin nauyin irin wannan maganar, abakin ki fa nake jin hakuri da yafiya abu ne me kyau."

Ai bazaki gane ba, kawai kije karma na sakejin maganar sa, ko yayinmiki maganata karki gaya mini, kuma idan ya turoki karkizo in dai ba zuwan kanki bane, idan ba hakaba wallahi zan gayawa Abbamu."

Kallonta sosai Zainab ta yi ganin babu wasa a idonta yasa ta miike batare da tace komai ba.

Haka Nur ta wuni da tunanin abin cikin ranta sai dai taki bari kowa ya fahimta tana cikin damuwa. Shiyer shiryen bakin Yaya Abdallah nata kankama wannan karon daka kalli Yaya Abdallah zaka gane yana cikin farin ciki.

Bayan kwana biyu Nur ta fara rage tsoron fita hakanan take jin nutsuwa na shigarta, dan haka yau tabi Aunty Saratu lalle da kitso, misalin biyar na yamma suka dawo, afalon suka samu Yaya da Abdallah da Yaya Bashir, Aunty na zama Yaya Abdallah yace "Kai Aunty lallen nan naki yayi kyau sosai, murmushi Aunty ta yi tare da cewa na Nur yafi nawa kyau Saida ta kwashewa me lallen karfenta sannan ni aka jagwalgawala min."

Dariya Yaya Bashir yayi sannan ya dubi Nur yace "Nur in gani." Tashi ta yi ta isa gabanshi tare da dage hijabinta tana nunawa Bashir, alokacin da yake cewa kai "Gaskiya yayi kyau" Jin haka Abdallah ya saci kallon Nur ta gefen idonsa, sannan ya kyabe fuska tare da jan tsakiya ya fice a falon.

Mamy ce tabi bayan shi da kallo, domin ta kula gaba ya ke da Nur, duk da cewa batasan meye ya sake haddasa abin ba tun bayan da taiwa tubkar hanci. Kwana biyu rak suka rage ayi bikin Abdallah, har wannan ranar Zainab Bata sake lekowa gidan ba, tana kallon su aunty suka tafi gidan da Yaya Abdallah zai zauna, yau akewa amarya Bilkisu jere amman Nur taki zuwa tai zamanta a gida.

Adaren ranar Auwal abokin Abdallah yazo gidan tare da wasu abokansu da alama agidan zasu kwana domin sun cika dakin, sai musun su kakeji wadda baka iya gane me suke cewa sai dai muryan Abdallah tafi tashi acikin su.

Duk juyin da Nur ta yi muryansa takeji, sosai ta shiga mamakin haka ya iya surutun tsiya, daker bacci ya kwasheta, washegari da safe Koda ta tashi tsit taji gidan dan haka ta yi tunanin kila tun da sukeje sallar asuba basu dawo ba, kitchen na nufa inda na samu bakin da suka zo jiya sunata tuyan kosai, Kula babba Aunty ta miko wa Nur tare da cewa "Yauwa Nur, mikawa su Abdallah adakin su."

Amsa ta yi sannan ta nufa dakin ta tura kofar tare da Sallama abakinki.

Wani Dake zaune kan kujeran Dake gefen gado ne ya amsa tare da dagowa yana kallon Nur, adaidai lokacin da Abdallah ya fito daga bayi yabi inda Nur ta aje kular da kallo. Mikewa ta yi tare dabin gadon da zagada zagadan mazan ke kwance da kallo, duk babu kaya ajikin su daga su sai gajeren wando, hakama Abdallah dake tsaye, acikin ranta tace, "Dan Allah dubesu manya-manya dasu" Ji ta yi mutumin Dake zaune yana cewa, "Kai! Ma sha Allah kunyi kama da yariyar nan sosai, dama kana da kanwa?"

Kallon Nur Abdallah yayi sannan ya kawar da kai tare da cewa, "Muna kama ko? Kanwata ce" mutumin ne ya sake kallon Nur tare da cewa, "Kai gaskiya tana da kyau, amma ba Mamy da

Abba ba ne suka haifeta? Dan ka taba cemin daga kai sai Bashir suka haifa" Riga Abdallah ya dauko yana kokarin sakawa ya ke cewa, "Daga baya aka haifeta karamar yariya ce fa, tsayon kafa ne.." ficewa Nur ta yi adakin ganin inda yake fakan idon abokin nashi yana zafga mata harara. Yau gidan kara cika yayi sosai, domin dangin su Abba dana Mamy duk suna gidan, ga abokan Abdallah da suke ta zuwa da ga gari gari dan haka gidan ya cika makil da jama'a.

Tun misalin hudu na yamma abokan Abdallah ke harabar gidan, da alama akwai wani abun da suka shirya zasu yi dan duk sun shirya cikin mayan kaya. Kafin karfe shida na yaddama du suka zare jiki batare da kowa yasan inda suka nufa ba.

Misalin karfe 8 na dare Nur na makale dakin Aunty dan yazon tafi zama cen, haka Kuma yanzun da ake biki yafi sauki jama'a, muryan Rahma taji tana kiranta, dan haka ta ji faduwan gaba, daker ta amsa tare da fargaban abin da yazo da ita gidan su a wannan daren.

Har cikin dakin Aunty ta shigo yayin Nur ta nuna mata Wurin zama tana cewa "Daga ina kike?"

"Da gida, ashe yau bikin Yayanku shine baki gayyaceni ba.?"

Ai ke kin wuce gayya Rahma, kawai kwana biyu bani da lafiya ne bana fita, amma bayau bane daurin aurem sai gobe

"Amma ai ko wayar Mamy Kya ara ki kirani, yanzun Umma ta gaya mini nace niko sainazo."Yar dariya Nur ta yi Jim ba wani matsalar bace ta kawota dan haka tace, "Lallai kin yi kokari da kika iya biyo lingunku a yanzun."

Karan motocin dake tsayawa a kofar gidan yasa Rahma mikewa tare da cewa, "Bari na wuce giben in sha zan dawo"

"Toh Rahma ki gaida gida na gode" Nur ta fada tana daga zaune.

Baki Rahma ta kama tare da cewa bazaki rakani ba? Sai naga kamar ma bakiso nazo ba?"

Mikewa Nur ta yi batare da ta sanyo hijjabi ba suna tafi suna hiran makaranta, abakin get Nur ta tsaya dalilin ganin su Yaya Abdallah a kofar gidan, cikin gidan na nufa komawa, saidai ga mamakinta sai taji an rike hannunta gam, dan haka ta fara kokarin fizzgewa tare da yar karamar gyara saidai hayaniyar dawowa su Abdallah da Karan motocin su baya bari a jita.

Can karshen bangon gidan aka jata, saketa taji Anya yayin da taga an mata runfa an zagayeta da hannun na mijine saidai sabo da babu wuta Bata iya ganin fuska bare ta gane waye.

Cikin daga murya tace "Waye? Meye haka?"

ba'a ce mata kalaba numfashi kawai ake saukewa me karfi.

Rawan jiki Nur keyi sai dai ganin har yanzun acikin gidan su take kuma su Yaya Abdallah na kofar gida yasata ganin saukin abin. Kamshin turaren dake tashi a wurin takejin kamar tasan shi saidai tsoro yaki Bari ta gane inda ta sanshi, bayan ya gama maida numfashi da ya ke ta tsinkayi wata murya na cewa "Ashe baki da tausayi Nur." Gabantane ya sake faduwa a karo na biyu domin ko acikin bacci zata iya zaida mai muryan nan...

CIWON 'YA MACE

By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Dan haka ta zare ido domin tabbatar da abin da kunnenta ya jiyo mata. Sai a yanzun tagane inda tasan kamshin turaren ko tantama babu Poul ne, tambayan kanta ta shiga yi Yaya aka yi ya shigo gidan nan, batare da ta gana nemo amsan ba taga Yana haskata ta da wayar dake hannunsa tare da fadin, "Ki nutsu, nazo ne kawai mu yi magana."

Batare da ta bari ya rufe bakiba ta ce, "Ana jirana agida acikin gida ne."

"Kafin ki shiga ina son zamu yi magana, idan kin bani hadin kai yanzun nan zaki shiga gidan, idan ki kaga kin dade a gurin nan to bansamu hadin kanki bane" Wannan karon Nur Bata iya cewa komai ba in banda kallon shi da take, duk da cewa bata iya ganin fuskarsa sosai amman hancinta na jiyo mata kamshin turaren sa, cikin rawar baki tace "Ka matsa mini in wuce."

"Bazan matsaba sai munyi magana, na aiko Helen kin ki sauraronta mai yasa? Numshi Nur ta maida sannan tace "Wace ce haka?"

"Kanwata Helen nake Magana."

"Zainab? Ita kadai na sani."

Kara matsota ya yi tare da cewa "Helen nake Magana Nur, bana son jin wannan sunan, dagowa Nur ta yi ta tsareshi da Ido, ganin in da yabita da Ido tai saurin sunkuyar da kanta tare da kokarin saka hannunta ta turashi baya, cikin kokarin Kai mishi doka tare da fashewa da kuka, dan haka yai saurin tareta ta hanyar matsaeta jikin bango, ganin duk hakan bazai mishiba ya dawo da ita jikinshi tare da matse mata baki yana fadi kasa-kasa "Ki yi shiri Nur ki tsaya ma yi magana ki wuce abinki"Jin numfashi ta na kokarin barin jikinta tai saurin yin shirun tare da kokarin daidaita numfashinta, har wannan lokacin tana kwance a jikinshi batare da ta sani ba. Jin da yayi ta lafa daga kuka da kokarin tureshi da take yi ya ce, "Haba Nur, menene haka? Na zauna sosai da masu addini irin naki, nasan wasu daga cikin hakayensu inajin suna cewa yafiya abu ne mai kyau, ban dauka zamu kawo har yanzun batare da kin yafe mini ba, Koko dan ni ba musulmi bane yasa bazaki yafe min ba?"

Sai a wannan lokacin Nur ta kula da in da take" Dan haka tafara kokarin tashi, saidai yaki barin hakan ta kasance, cikin kuka take cewa "Ka manta abin da kaimin ne? Saida ka wulakantani sannan zakace min in yi hakuri, duk da kake ganina karama Ina da wayauna, lokacin da nake baka hakuri me yasa baka hakuraba har Saida ka fatantaka min kayan jikina"

"Ai nasan kina da wayau Nur, nasan dole abin yai miki ciwo, shiyasa na ce da kaina zanzo na baki hakuri, duk da cewa ban miki komaiba, na gane ban yi daidai ba Mamma da Helen zansan yadda zanyi in canza su, ke Kuma kifito kije makaranta karatu na wuce ki, don Allah don Allah ki yi hakuri ki fito ki yi harkokin ki kamar da." Kuka Nur ta sake sakawa tare da kara hankadashi ganin haka ya saketa ta rabo daga jikinsa, saidai cikin sauri ya sake yi mata runfa a karo na biyu tare da cewa, kina nufin wucewa zakiyi batare da kince kin yafe ba?"

"Duk abin da zaka mini sai dai kamin wlh bazan yafe ba, haka kawai na riga na gayawa Abba na Kuma yana shirin daukan mataki karka kara shigo mana gida."

"Zan kara bazan daina ba Nur, dole in nemar ma zuciyata sauki akan abin da ta ke so."

"Ka matsamin na wuce ko na fasa maka kai."

"Ina jiranki na shirya daukan duk wani abun da kike takama dashi" Wanni irin kallo Nur tamai

sannan ta sake cewa,  "Matsa in wuce"
"Bazan matsa ba" ya fada yana kara matsota Dan haka ta kara mannewa da bango, ganin tana kokarin saka ihu yasa hannunsa ya toshe bakinta tare da cewa "Idan kina son in bar wurin nan sai kince min kin yafe."

Hannunta tasa tana kokarin banbare nashi tare da cewa "Na yafe." Hankali ya karasa sauke hannun sa tare da cewa "Yaushe zaki je makaranta?" Cikin zunbura baki ta ce "Nima ban sani ba."
"Kalla, gobe kuna biki, jibi lahadi, ranar Monday ki fito kije makaranta."
Wannan lokacin bata iya cewa komai ba kokarinta kawai ya cire hannu sa ta wuce, jinsa ta yi ya kuma cewa "Kin ji."

Daga kai ta yi alamar eh, sannan ya cire hannun cikin sauri Nur ta wuce, bayanta ya biyo, ita ko Nur sauri take har Saida taga tabi hanyar da zata sadata da cikin gida sannan ta juyo ta kalleshi a daidai lokacin da ya fice daga cikin gidan. Kai tsaye dakinta da shiga, rabon da ta kwana dakin ta jima, yau daya ta ji tana son kebewa, Sam bata son magana ko hayaniya, ko da ta shiga dakin gado ta fada sannan ta shiga tunani akan zuwa Poul gidan su, tashi ta sake yi acikin zuciyarta take cewa, "Yanxu shikena na yafe mishi?, Haka zamuci gaba da kallon juna alhalin ya kalleni tsirara" Innalilahi wa Inna ilaihir raju'un ta fadi a fili sannan ta sake komawa gadon ta kwanta, wani sabon yanayi taji a jikinta dan haka ta saurara domin tantace wanni irin Yana yi ne take ciki a yanzun, tunata kwance jikin Poul ya sa ta runtse Ido tare da sauke ajiyan zuciya kamar yanzun ne abin ke faruwa, gaba daya ta nemi nutsuwarta ta rasa duk da cewa bata ga fuskarsa ba ayau amman fuskarsa ta baya ke ta dawo mata, fari ne tass, dan gayen gaske maiji da nera, ajiyan zuciya ta sake ja sannan tace a fili "Su Yaya Bashir suna Ina Poul yayi kudi ya barsu alhalin zasu iya girman shi, duk da cewa suma suna da sana'a sai dai ko rabin-rabin shi Basu kai ba a kudi, dan ko Jamal da Jamil da suke takama da narai bzaasu nuna mishi komai ba" afili ta sake cewa "Watakila dan ya fisu kudi yasa ya fisu gaye" jin turo kofar da aka yi ya sata yin shiru tare da kallon Kofar, Aunty ta gani tana shigowa Dan haka ta fara kokarin sake fuskarta domin kada Aunty ta fahimci wani abu. "Nur ya kike dawo nan?" Aunty ta yi tambayan tana kokarin zama kusa da Nur"
"Na ga baki sun yi yawa acan ne." Nur ta fada tana kallon fuskar Aunty, kallonta Aunty ta yi sosai sannan tace "Ki ce min dai kin rage tsoron Paul toh ai shikenan" Mikewa ta yi tana kokarin fifita har ta kai kofa ta juyo ta sake kallon Nur tace "Kin yi sabon turere ne?" Gaban Nur ne ya fadi domun kamshin turaren Poul ne ya cika dakin a tunaninta ita kadai ke ji dan haka yanzun da Aunty ta yi maganar ta daburce, Daker ta iya cewa, "Eh" Ficewa Aunty ta yi, Nur ko na ganin fitan Aunty ta mike ta nufi bayinta dake cikin daki, kayan dake jikinta ta cire ta wanke su sannan tai wanka ta dawo ta kwanta, saidai Tunanin Poul ya hana mata runtsawa, tare da mamaki har lokacin da take wanke kayanta tanajin Kamshin turaren Poul na tashi a jikin su, daker bacci ya iya daukanta, washagari da safe jinta take cikin farin ciki da annashuwa musamman idan ta tuna yaune daura auren Abdallah duk da cewa har yanzun ba magana ya ke da ita ba. Alwala ta yi ta tada sallah saidai ta gaza natsuwa domin sosai Poul ke fado mata, duk da kukarin ganin ta kawar da tunanin shi dake yawan zuwa mata arai, bayan ta idar ta mike tana ninke dadumar acikin ranta take cewa Anya ma sallata ta yi kuwa ace ina sallah ina tunanin katon arne, tsaki taja tare da sake shinfida dardunar ta sake yin wata sallah, sannan ta mike ta shiga cikin gida. Ayau da ga kalli fukar Mamy zaka gane tana cikin farin ciki, hakama aunty da duk sauran

mutanen gidan, Shi kanshi Abdallah yana ta shiga da fice a cikin gidan fuskarshi babu yabo babu fallasa, misalin karfe daya gidan ya cika duk dangi sun hallara na kusa Dana nesa.

Nur zaune gaban Mamy sai danna wayar aunty da ke hannunta take, Umma dake zaune can gefe ne ta kalli Nur ta ce, "Gaskiya Hajiya Halima kin sangarta Nur da yawa, ji inda ta zauna tun tuni tana faman wasa da waya saikace wata karamar yariya."

Gefen da Nur take Mamy ta kalla sannan tace "Aiko duk wadda ya kalli Nur yasan babu alamar sangarta a tattare da ita."

"Idan ba lalacewa ba ko kamar Nur yanzun ai kamata yayi ace ta na can tsakar gida ta kama wani aikin Itama." Wannan karon Mamy fuskartar Umma tayi tare da cewa, "Ba aikin da zatayi yau, wannan aiki ai na manya ne" Wurin Nur ta juyar da kallonta tare da cewa tashi kije ki shirya" Mikewa Nur ta yi batare da ta ce komai ba ta nufi dakinta tura kofar, cike da mamake take kallon gadonta kaya maza ne farare kalla aje akan gadon, a gefe guda Kuma ga takalmi da agogo tare da turaroka, ajiyan zuciya ta yi domin ta tabbatar da babu wadda zai ajiye kayan nan sai Bashir, zama ta yi abakin gadon domin gudun karta shiga wanka Bashir ya shigo ya dauki kayansa batare da ya bata kudin da yace zai bataba, sai dai ga mamakin ta tazama taji motsin watsa ruwa a bayinta, dan haka ta saurara jin tabass wanka ake yasata mikewa ta nufi kofar tare da tambayan waye? Tsawon lokaci tana sauraro ba'ace komai ba, dan haka ta sake cewa waye aciki? Wannan karon ma abace komai ba, duk da haka Nur Bata hakura ba murya ta daga ta sake cewa Wai waye aciki ne? Awannan karon batare data rufe baki Bata ji ance Ubanki ne!" Da baya ta koma bakin gadon ta zauna tare da mamakin me ya kawo Abdallah wanka dakinta, bata gama mamaki ba ta mike da nufin fita dakin domin karma ya fito ya sameta aciki, saidai harta taba kofar ta tuna da sabulonta dan haka tai saurin komawa wurin kofar bayin tace "Yaya Abdallah karka taba min sabulona!" Saurarawa ta yi ko zaiyi magana, jin bece komai ba ta sake ce "Dan Allah karka taba min sabulo kaji" Wannan karon ma dai bece mata komai ba dan haka ta tsaya a wurin bayan tsayon wani lokaci ya bude kofar ya fito yana daure da towel daga kugunsa zuwa guiwa, kallo daya yai mata sannan yace, "Au dan Ubanki tsayawa kika yi anan? Sabolun naki na gwal ne da baza'ayi amfani dashi ba?" Kokarin kutsawa take ta gefen sa cikin turo baki gaba tace "Yaya Bashir ne ya saya min sau daya na yi amfani dashi"
"Toh ya kare dashi na yi amfani sai ki gaya mishi ya sake sawo miki wani" Kutsawa ta yi ta gefensa bata damu da gogan jikinshi da ta yi ba har sai da yai saurin rike towel dinsa tare da bin bayanta da kallo,
guntun sabolun ne rike a hannunta yayin da ta fara kuka tana fadin yau fa na bude, shine har ya kare haka? ta kare maganar tana kallon fuskar Abdallah, cike da mamaki yace "Zo ki fita kibani wuri na lura ma ba hankali ne da ke ba." Tsuganawa ta yi ta dauki soson wankanta ta kalla sannan ta fashe da kuka tare da kokarin ficewa a bayin adaidai lokacin da Abdallah ke cewa yau na gama masifa soson naki ma laifine dan na yi amfani dashi?

Cikin kuka ta ce "Ai babu wadda ke dauka soson wani agidan nan sai ni za'a dauki nawa?" Bata rufe bakiba ya dauketa da Marin tare da cewa "Fita kibani wuri." Fashewa ta yi da kuka sannan ta nufa kofar fita a dakin, bata dire ko Ina ba sai adakin Mamy, tun kafin ta shiga take cewa "Mamy Kinga Yaya Abdallah ko!" Duk mutanen dakin hankalin su dawowa yayi gareta, Mamy kuwa cike da fusata tace "Me ya faru?"
"Mari na yayi Mamy" Cikin kuka sosai Nur ke maganar har yanzun tana dafe da kumatunta"
"Kin mishi wani abun ne?" Daga yadda Mamy ke maganar zaka gane ranta a bace ya ke.

"Saboluna ya karar min Kuma jiya Yaya Bashir ya saya mim"
"Wato shi dai Abdallah matsala gareshi banda abinshi Ina ruwanshi da sabolon ki? Yana ina? Ni fa bana son mugunta, menene nashi da duka kuma? shi baya yin laifin ne me yasa ba a dukan shi? Mu je" Cike da fada Mamy ta fice a dakin, Aunty ce ta kalli Ummy Dake gefe tace "Kingani ko? in da kike ma Nur bata kalla ba, ita ta sabulon ta take, ita Kuma Mamy in dai kaji tana fada a gidan nan to akan Nur ne, dan ayanzun kam ita da Abdallah basa shiri sam, abin da ba'ayi da kuriciya ba shi ake yi yanzun." Murmushi Ummy ta yi tare da fadin "Allah ya shiryeta dai, banda abinta da yau daya har ta yi magana" Mikewa Aunty ta yi tare da cewa "Barin je, dan shima fa ba kanwan lasa bane, Mamy Kuma akan Nur Bata da dama" karake maganar ta yi tare da ficewa a dakin.

*****

Abdallah na daura agogo su Mamy suka shigo, be yi mamaki ba dan yasan dole Nur takai karanshi, kallo yabi Mamy dashi yayin da take fadin "Ya zaka daketa ka hanata kuka?" Cikin San yin murya sosai ya ce "Mamy kiyi hakuri, idan mutanen dake dakina sun fita taje ta kwashe duk sabolo dake dakina na bata."
"Ba ason sabolun naka, Kai kasan kana dashi me ya kawo ka nan wanka?" Wannan karon lebensa ya lasa alamar Yana cikin damuwa sannan yace, "Mutane sunyi yawa ne Mamy, kuma kowa wanka yake son yi"
"Idan hakane sai ka dauka sabulonka kazo dashi, Kai baka siya mata sabuloba baka da damar zuwa ka yi amfani da nata"
"Toh a yi hakuri Mamy baxan karaba" yana fada idonshi cike da farin ruwa.
"Dama neman magana kawai kake, da gangan ka yi, in ba hakaba wanka daya a karar sa sabolu haka?" Mamy ta fada tana nuna mishi sabulon da Nur tazo mata dashi. Satan kallon Nur ya yi ya gallara mata harara sannan ya kalli Mamy yace "Nawa ne sabulon in bata ta saya wani?
"Dukan Kuma da kamata fa? Nace idan ka biyata sabulu barin daka mata fa? Zaka hada duka ka biya ne?"
Shigowan Aunty ya sa duk duka juya suka kalleta Abdallah ko takalmi sa da kularsa ya dauka ahannu yana kokarin fita acikin dakin, cikkn sauri Aunty tace "Ina Kuma zaka? Ka tsaya ka gama shiryawa mana." Toh aunty bakya ganin abin da Mamy ke min ne" Ya fada cikin nuna bacin rai, da alama ya fara fusata, "Kibarahi gara ya fita din,idan ba neman rigima ba shida yazo cin arziki har ya daketa.?"
"A'a wallahi, ita dai kecin arziki" Aunty ta fada tare da amsan takalman Abdallah ta aje kasa tana fadin "Karasa shiryawa sannan ka fita."
"Au waton goya mishi baya kike har zakice haka? Ai ba'a canzawa tuwo suna, yadda zaiyi takama gidan ubanshine itama haka gidan ubantane, ba'a fimu tsumma ba bare ace za'a bada mana kwarkwata, kuma yazo ya fita tunda ba dakinshi bane"
Aunty kan Nur ta maida kallonta tana fadin "Wallahi Nur baki da kirki, yau daya kin kasa hakuri da dan'uwanki, yanzun ke wannan abin da ke faruwa dadi ya ke miki? Gida cike da mutane kika iya ratsasu kikai kara?
Batare da Abdallah yaji me Nur zatace ba ya fice a dakin, da alama yaji haushi sosai Dan ko kallon Inda Nur ta ke biyi ba, Aunty ma ficewa ta yi yayin da Mamy ta Kara rarrashin Nur sannan ta fita.

Har wannan lokacin Nur haushi take ji domin ita ta tsana a taba mata sabulo, daker tayo wankan sabo da haushi tana fitowa ta sake kwanciya a godo batare da shirya ba, wayar Aunty dake gefenta ta ji ta fara kara, dan haka ta mike tasa hijjabi domin ta mika mata, katsewa ta yi bayan ta saka hijjabin aka sake kira, wannan lokacin ne ta kalli wayar ganin Yaya Bashir ne tai saurin dagawa tare da cewa "Yaya!" Daga can cikin wayar yace "Na'am kanwata, Amman kin gama fushin dai ko?

"Yaya Abdallah ne ya karar min da sabulon daka kawo min."

"Yanzu Mamy ta gaya min, zan kawo miki wani amman ki saki ranki, Kuma kiyi maza ki shirya ganinan zuwa in dauke ki muje wurin dinner.

Cikin ranta taji farin ciki sai a yanzun ta tuna biki fa ake agidan cike da murna tace "An daura auren ne?"

"Eh yanzun dai za'a daura."

"Toh Yaya Bashir da an daura ka kirani ka Gaya min in ruga in yiwa Mamy albishir."

"Karki damu kanwata, idan ma kinason kiji kamar kina wurin sai in kira ki da zaran zara'a daura auren."

"Ina son Yaya Bashir dan Allah ka kirani."

"An gama kanwata, amman wai ni in tambayeki mana."

"Inajin ka."

"Ba yanzun kika gama fada da Abdallah ba amman Kuma kina murna da auren shi.?"

"Ai dan uwana ne Yaya, daman shine yake tsokana ta yanzun dai karka manta ka kirani, Kuma yanzun zan shirya karfa ka manta ka wuce dinner bakazo ka daukeni ba."

"Yaya za'ayi in manta? kiyi maza ki shirya dai."

Nur na sauke wayar ta mike, kayan da zata saka ta dauko, duk abin da zata bukata ta aje bakin gado, bayin ta nufa da nufin yin waka taji wayar na kara, dawowa ta yi ta zauna ganin Yaya Bashir ne ta zauna domin sauraron daurin auren...

CIWON YA MACE

By

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 33-34

Tana kara wayar a kunnenta ta ji muryan marokin cikin sifika ya ke maimaita abin da waliyan Amarya da ango ke fada, sosai Nur ta cika da farin ciki, dan haka ta mike a guje ta nufi dakin Mamy, tana cewa Mamy an fara daura auren Yaya Abdallah, ta na shiga dakin ta kara wayar a kunnen Mamy, yayin da mutanen da ke falon suka bita da kallo, itako Mamy cike da fara take kokarin zame wayar tare da fadin, "Naji Nur, jeki shirya" Nur kuwa kara dannawa Mamy wayar take, domin da alamu Mamy kunya ya kamata, dariya Nur ke yi da duk mutanen dake dakin, bata cire wayar a kunnen Mamy ba har Saida taji muryan Yaya Bashir yace, "Toh kindai ji da Kunnen ki sai ki yi maza ki gayawa Mamy" Mayar da wayar ta yi kunnenta tana cewa "Ai itama ma a kunnenta aka daura wallahi." Cike da fara'a Bashir yace, "Da gaske ko wasa? Amman kin

kyauta kanwata, Allah ya kaimu ranar namu ko?" Cikin sauri Nur ta fice a dakin, tare da cewa "Amin Yaya Bashir amman naka ni bandani"
"Me yasa banda ke? Bakya son mu yi aure rana daya?
"Ni bana so Yaya Bashir, karatu zanyi in zama likita, can gidan su Rahma yayarta ba tayi karatuba mijinta nayin kudi ya auro yar boko, yanzu tana nan agida ta girma tana kunyan komawa makaranta, sannan kigidan su Hajiya Tani..."
"Tsaya Nur, dakata mana, wannan shine hujarki?"
"Eh, tsaya kaji sauran"
"Bazan tsaya ba, indan wannan ne bari in koya miki yadda zaki dinga cewa, idan an yi miki maganar aure cewa zakiyi saina gama karatu amman kibar cewa bazakiyi aure ba" Nisawa Nur ta yi sannan tace, "Bari Kuma kaji ya Bashir, ni ko ban yi aure ba har na mutu babu komai wallahi, a gidan hajiya tani akawai wata mata, itama batai karatu ba mijinta har hira yake da yan mata agabanta da turanci tunda yasan baji take ba, da daddare ma yayi ta chart dinshi gabanta in tayi magana yace abokin kasuwancin shine daga chaina, har saida ya auro yariyar ta gane, yanzun duk tafiyan da zaiyi da amaryan yake zuwa, itiko uwar gidan duk ta zama abin tausayi ko kaya mai tsada tasa bata kyau."
"Oh Nur, wato da nace karki bani labarin shine saida kika san yadda kikayi kika gaya min, su wannan kaddaran su ce ahaka, ke ko Kinga ko yanzun kikayi auren duk matsalar nan da kika zaiyyano bazaki fuskanceshi ba in sha Allah, barema zaki kara karatu nan da shekara biyu zuwa uku sai kiyi aure, kinga lokacin kina da shekara 18 ko 19"
"Ya Bashir tsaya kaji..." Goshi Bashir ya dafe tare da kallon yadda Abdallah dake gefensa ya daure fuska tamau, dan haka yai saurin cewa, "Nur tashi ki shirya idan mun hadu ma karasa maganar yanzun Ina kan hanya ne, kuma ni ke tuka motar" Yana gama fadin haka ya sauke wayar, sannan ya saci kallon Abdallah tare da fadin, "Nur ce fa"
Cike da fada Abdallah yace, "Tunda muka taso Wurin daura auren nan kake waya da ita, Ni bansan me yasa kake bawa yariyar nan fahimcinba, naga har wani lallabata kake, baka son bacin ranta."
"Ba haka bane, idan bamu yi hira da itaba waye ne zaiyi da ita Abdallah, sannin kankane a family mu muna da karancin mata, babu wata mace wadda take sa'arta Kai ko wacce ta girmeta ma babu, ita kadai ce shiyasa gata nan kullum a firgice..."
"Wannan kuma ita taso, wanni kulawane a baya ban bata ba? Amman tarasa wadda zata zubarwa mutunci saini, ni daga yau babu ruwana da ita, bani acikin duk wani abu da ya shafeta" Shiru Abdallah yayi tunawa da yayi basu kadai bane a motar ya hanashi karasa abin da yaso fada, dan haka Bashir ma yayi ajiyan zuciya, daidai wannan lokacin suka Isa kofar gidan su Auwal.
Ita ko Nur tana sauke wayar tace "Kaji Yaya Bashir, nikam karatuna zanyi bani son wani zancen aure, idan lokacin yayi na yi amman yanzun nafi son naji ana maganar makaranta kawai."
Shiryawa ta yi, cikkn les din da Mamy ta dinka mata, dikin ne na mutunci wadda be takura jiki ba, dogowar riga, sannan ta yi daurin dankwalinta mara hayaniya, bayan ta saka dankunnenta wadda suka dace da kayan ta dauki dan karamin gyale ta daura a kafada, turaroka ta fesa sannnan ta zauna zaman jiran zuwan Bashir, agefe guda kuma ta na jiyo haniyar gidan sai dada karuwa yake, ta jima sosai ta na jiran Bashir harta fara gajiya, sannan ta ga wayar tayi kara,

cikin sauri ta dauka tare da cewa "Yaya Bashir na gaji da jira."
"Fito mu tafi kanwata" Sauke wayar Nur ta yi tare da mikewa, ganin gidan ciki ta nufi dakin Aunty, wayar ta mika mata sannan tai mata sallama ta fito kofar gida, motar Bashir ce kadai tsaye dan haka ta bude ta shiga yayin da Bashir ya juyo ya kalleta tare da cewa "Kinga inda wani haske ya lullube motar kuwa daga shigowanki, idonshi akanta yai maganar dan haka Nur tai dariya tare da cewa, "Na yi kyau ko?" Kara karkacewa Bashir yayi Yana mata kallo mai cike da tsokana ya ce, "Ba kadan ba Nur, Mamy ta ganki kuwa?" Cikin sauri Nur ta girgiza kai tare da cewa, "Banjeba, dakinta cike ya ke da mutane" Dauke Ido Bashir yayi akanta tare da kokarin tashin motar ya na cewa, "Ke kuma gaki mai tsoron mutane ko?" Girgiza Kai Nur ta yi tare da cewa, "A'a kawai dai na kosa na fitone, kuma idan na shiga bakina sai yayi zafi wajen gaishe da mutane, Mamy matsamin zata yi taita cewa mutane ga Nur nan, Nur ki gaishe su."
Dariya Bashir yayi bayan ya hau kantiti sosai tare da cewa "Wato abin da Mamy ke miki kenan?, Su kuma mutane su yi ta cewa lallai Nur ta girma ko?"
"Wallahi kuwa kamar ka sani, haka suke cewa sai su yi ta mamaki" Waigowa Bashir yayi ya kalleta tare da cewa "Ai dama na sani, dama dole za'ace kin zama budurwa, Yau dai Abdallah ya girma zai tafi ya barmu ni kuma in sha Allah kafata kafarki" Wani irin kallo Nur tawa Bashir tare da cewa zuwa Ina Yaya?"
Zuwa gidan miji Nur, Ina son mu yi aure rana daya"
"Tab, wallahi badani ba Yaya, ni fa wallahi na tsana maganar aure ma, dan Allah ka daina yi min"
Dariya Bashir yayi sosai Yana Satan kallon Nur sannan yace, "Lallai kince wani abu Nur, amman fa kina bani dariya"
"To wai kai Yaya mai yasa ka cika yin mgnr aure?" "Sabo da ina son Auren ne Nur" Tabe baki Nur ta yi sannan tace, "To dan Allah ka yi abinka karma kacewa Abba kana son mu yi rana daya kajamin." Dariya Bashir ya sake yi dan haka Nur ta sake cewa "Allah Yaya Bashir da gaske nake, ba cewa na yi Bazan yi kwata kwata ba, amman nan da shekara goma albarka." Wani irin kallo Bashir yai mata zuwa can Kuma ya daure fuska tare da jan tsaki sannan ya ce, "Amman baki da hankali ko? Tsaki ya sake ja sannan yace, Bari ma dai in daina wannan maganar dake" Kallon shi kawai Nur ta yi ta dauke kanta bayan sun yi tafiya Mai tsayo tace, Yaya Bashi kaga yadda Yaya Abdallah ya mayar min da sabulo daga yin wanka daya dashi, wallahi saura dan mitsi ya bari, ai kace zaka saya min wani ko?" Kawar da kai Abdallah ya yi can gefe sannan ya ce, "a'a" sosai Nur ta kalleshi tare da cewa "Sabo dame?"
"Bani da kudi" Bashir ya fada a gajarce, Kallon mamaki Nur tabishi dashi domin Bata tabajin irin wannan maganar daga bakinshi ba, can kasa tace Allah ya kawo"
"Amin" ya fada a hankali bayan sun yi tafiya Mai tsayo Nur ta sake kallon shi tare da cewa "To yanzun waye zai dauko Hajiya?" Wannan karon ma batare da Bashir ya kalleta ba yace "Ke" Da sauri Nur ta kalli Bashir tare da yin yar dariya sannan tace ai ni ganin anan, sai dai Abba ko Baffah wani ya daukota"
Wannan karon Bashir baice komai ba, har suka isa wurin Satan kallon Bashir Nur ke yi, suna sauka amotar Bashir yai ciki batare da yabi takan Nur ba, cikin gudu-gudu tabi bayanshi, cikin katon dakin taron da ya cika makil suka shiga, wadda ya kawatu iya kayatuwa, da alama a makare sukazo domin bikin ya riga da yayi nisa, a idon Abdallah Bashir ya wuce yayin da yaga Nur nabishin abaya, hade fuska yaso yi sabo da ganin Nur, amman tunawa da yayi duk

mutanen wurin nan suna farin cikine sabo dashi sai ya cigaba da Murmushi, sai dai har yanzun Idonshi a akansu, Yana kallo Nur ta tsaya a bayan Bashir, da alama neman inda zata sauna take domin taburin da Bashir ya zauna shine cikon mutum hudun kuma duk maza ne a wurin, gani yayi Bashir yayiwa Nur magana tai saurin kallon tebur din dake gefe sannan ta wuce ta zauna, wadda ya zama itama itace cikon mutum hudu sai dai duk maza ne, acikin zuciyarshi yake kwatanta abin da ke faruwa tsakanin Bashir da Nur da alama fada suka yi dan akwai bacin rai a fuskar Bashir, yana cikin wannan tunanin yaga Bashir yayiwa Nur magana yayin da tai saurin kallon can baya sannan ta make kafada, satan kallonsu Abdallah ya cigaba da yi zuwa can yaga Abdallah ya mike ya isa wurin da Nur ke zaune ya riko hannunta sannan suka nufa can baya suka zauna tare, Nur na zama ta kallo Inda Amarya da ango suke dan haka Abdallah yai saurin kawar da kanshi, itako Nur tana kallo Amarya da angon tana cewa "Dan nace sai nan da shekara goma kakejin haushina?, Nifa Yaya Bashir fada kawai na yi ba da gaske nake ba..." "Toh ki daina irin wannan, fatan tsiya ne kikewa kanki" Idonta akan fuskarshi tace "Nabari to" "Yafi kam" Idan kin gama Secondary kin fara makaranta ko a shekar farkon ne kika samu miji kiyi auren ki yafi,  ki kalli amarya Abdallah yar karama da ita, dan Allah bata burgekiba?" Kai kawai Nur ta daga domin burinta kawai ya bar maganar, Ji ta yi ya sake cewa "Nasan dan baki da saurayi kike fadan haka, Ina rokon Allah ya kawo miki miji na gari Mai hankali da nutsuwa kafin lokacin da iyayen Aisha zasuce in fito, dan ni bazan tafi in barkiba kafata kafarki" Wannan karon ma Amin Nur tace saidai bekar har zuciyartaba, hira ya cigaba da janta dashi kadan-kadan, yayin da ta maida hankalinta a wajen kallon ango da marya, zuwa can Bashir ya dauki Jakar Nur yasa kudi tare da cewa muje mu yi musu liki, gudun kartawa Yaya Bashir musu ta mike ta bishi, duk kudin da ya samata ta lika sannan ta koma wurin zamanta ta zauna tana kallon yadda Yaya Bashir yake ta watsar da kudinsa kamar besan darajarsu ba, Mai da hankalinta ta yi Wurin jama'a wurin, gani ta yi da yawa sannune jaruman finafinan hausane mata da maza ne wurin, kwalliya kuwa na waccen na wane wannan abin ba'a cewa komai, tunani ta shiga yi acikin zuciyarta wai menene alakar Abdallah da 'yan fim din Hausa, tunawa ta yi da hoton da ta taba gani a wayarshi da alama Yana cikin su dumo-dumo, tana cikin wannan tunanin taji ance "Gashi kije ki karayin likin, tunkafin Nur ta dago ta shaida Mai Muryan, yayin da kamshin turarensa ya kara tabbatar mata da hakan, dan haka tai saurin dago kanta ta kalleshi, Poul ne tsaye cikin shadda Mai tsananin sheki babba riga da yar ciki yayin da ya daura hula kalar aikin Dake gaban rigar shadda, sosai kayan ya haskashi, hasken fatarshi ya hade da bakin sajenshi ya bada kalla, daker ta iya sunkuyar da kanta domin tabar kallonshi, kokarin mikewa ta fara yayin da ya cigaba da Miko mata bandir din yan dubu-dubu dake hannun sa yana fadin "Amsa."

Cikin daure fuska sosai tace "Banso" kokarin wucewa take ya sha gabanta tare da cewa "Tsaya mana."

Cike da fada Nur tace "Ni ka wuce banso"

Tsaye yayi mata gaba yana kare mata kallo sama da kasa, itako Nur hankalinta ta raba kashi-kashi ko a jamar wurin bata son hankalin kowa ya dawo kanta bare kuma Yaya Bashir ya waigo ya gani, dan haka cike da karfin hali tacewa "Poul ka wuce ka rabu dani, idan ba hakaba zan hadaka da yayana." Kara matsowa Poul yayi yayin da yai saurin rike hannunta tare da cewa, "Na shirya tsayuwa a gabansu ai" Rawan jiki ta fara tare da kokarin kwacewa daga rokon da yai mata, janta ya fara yayin da ta shiga turjewa dan haka hankalin wasu mutanen ya fara

dawowa kansu, sai dai Poul ko a jikinshi janta yake har yai nasaran fita da ita daga cikin dakin taron, yayin da wajen ya kara kacamewa da kide-kide da hayaniyar mutane. Can bayan dakin taron Poul ya tsaya tare da yiwa Nur rumfa da faffadan kirjinsa, jajayen idonsa ya sa mata, Yana mata wani irin kallo, cike da tsana Nur take kallonshi saidai ta kasa cewa komai kallon shi kawai take.Tsayon lokaci suka dauka haka zuwa can Nur ta fashe da kuka wadda ita kanta batasan dalilin yinshi ba, ganin abin da take Poul ya hada goshinshi da nata tare da cewa "Kiyi hakuri na dameki ko? Kamar jira Nur ke yi ta tsuguna ta dauki wani dutse dake kasa cikin sauri ya cire hannunshi daya domin ya bata Tamar daga hannun nata kamar yadda yaga taso yi, daga dutsin ta yi cikin matsanancin kuka tare da cewa "Wallahi zan fasa maka kai, ka fita daga harka ta, na daina zuwa gidan ku, Helen dinma nabar kawance da ita, to me yasa zaka matsamin? Lumshe Ido yayi cikin sanyi jiki sosai sannan ya maida hannunshi tare da cewa "Idan akwai abin da yafi jifa kimin, duk abin da kike son kimin komenene shi bazan yi bakin ciki da faruwansa ba gani ki min.

Wannan karon kallonshi ta yi tare da sauke dutsen sabo da hannunta daya sage sabo da nauyin dutse, ki kwala min mana taji ya fada dan haka ta sake kallon shi cikin kuka tacigaba da cewa, "Wulakancin da ka min be ishaka bane har yanzu? wai menene? Me kake so? Me yasa kake bibiyata?

Cikin sauri ya sake hada goshinshi da nata tare da cewa "Yauwa Nur, zan gaya miki, tun da ga ranar da nasa aka daukoki kika tsaya min a zuciya, ko na yi kokarin share abin baya sharuwa, kin tsaya min a zuciya sosai kodayaushe sai in ji ina son na ganki, tunaninki yana hanani bacci, Koda ace na samu nayi Ina farkawa sai inji Ina tunanin ki, yana maganar ne yana goge hawayenta da fuskarshi zuwa koshinshi yayin da hannuwanta yake kan kirjinshi tana kokarin tureshi ta kasa, sosai yanayin da suke ciki ya rikita mata tunaninta tun daga lokacin ta kasa gane me ya ke cewa, ganinta kawai ta yi tana kokarin barin wajen shi Kuma yasa hannun shi ya riketa tare da tsugunawa yana kokarin dauko mayafinta dake kasa, bayan ya dauko daura mata a kafada tare da cewa "Kibani amsa kafin ki wuce."

Sunkuyar da kanta ta yi kasa tare da kokarin kwace hannunta, zagayowa Poul yayi Yana kokarin hada Ido da ita, ita Kuma taki barin hakan ya faru, "Nur ki amsa min saiki wace" Batare data waigoba tace "Banji abin da kace ba" idon shi a kanta ya ce "Na ce Mene ne wannan nake ji?" Sunkuyar dakai ta yi yayin da jikinta ke rawa dan haka ya sake cewa "So ne?" Cikin sauri Nur ta girgiza kai dan haka ya kara matsowa batare da ya saki hannunta ba yace "To mene ne shi?" Adaidai wannan lokacin taji muryan yaya Bashir yana kwala mata kira, dan haka ta zabura tare da kokarin kwace hannunta, saidai ya hana mata yin hakan tare da kara marairaicewa, kara rudewa ta yi domin har yanzun Yaya Bashir kwala mata kira yake har da muryan wasu mutanen daban

CIWON 'YA MACE

By

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Awannan karon zabura Nur ta yi mai karfi dan haka ta kufce batare da ya fargaba, aguje tabar wajen tana waiwayen shi, shikuwa Poul kansa ya dafa domin har yanzun beji hankalinshi ya kwanta ba.

"Ina kika je?" Ya Bashir ya jafawa Nur wannan tambayan yayin da ya tsareta da ido. Sunkuyar da kanta ta yi tana wasa da hannunta tare da motsa bakinta, sai dai ta gaza furta komai, Idon Bashir a kanta ya sake cewa "Nur bakyaji ne Ina managa?" Dagowa ta yi ta kalleshi can kasan makoshi ta ce, "Fitsarine ya matseni" Kallon sama da kasa yai mata sannan ya ce "Fitsarin kikaje kenan?" Wannan karon daga kai ta yi, kallonta Bashir ya sake yi sannan ya bi hanyar da ta fito dan haka gaban Nur ya fadi, kallo ta bishi dashi tana dafe ta kirji, zuwa can ya dawo ya wuceta batare da ya kalli Inda take ba, bayan shi tabi da alama be gamsu da abin da Nur din ta fadaba, yana shiga motar Nur ma ta shiga ta zauna, saidai ta kasa sakewa da ka kalleta zaka gane bata da nutsuwa sam domin gaba daya jin ta take a yamutse, dan haka ta fara hawaye duk da cewa tabawa Bashir baya Amman tanaji ajikinta kallonta yake saidai bece mata komai, karatun Alqur'ani ya kunna yanabi acikin motar dan haka tuni Nur taci gaba sa kuka.

Zuwa can taji ya tsaya tare da kashe karutun, waigawa tayi tare da zabura dalilin ganinsu a kofar gidansu, hawaye ta fara sharewa tare da kokarin sauka acikin motar batare da ta bari sun hada Ido ba, harta saka kafarta daya a waje taji yace, "Nur juyo mu gani" Ahankali ta juya ta kalleshi bayan ya kare mata kallo ya ce, "Kuka me kike yi?"
"Babu komai, ba kuka nake ba" Jinjina kai Bashir yayi sannan yace "Shikenan jeki" Sauka ta yi Cikin Sauri ta shige gida, dare ya riga yayi domin tun suna hanya aka Kira mangariba, Kai tsaye gefen Mamy ta shiga, wannan karon akwai saukin mutane, dafda Mamy ta zauna jikinta a sanyaye, cike da mamaki Mamy ta kalleta tare da cewa "Nur Yaya dai, na ga kin dawo jiki a sanyaye?" Kamar jira Nur take ta fashe da kuka dan haka Mamy ta saki baki, mamaki karara akan fuskarta tace, "Me yayi zafi haka?" Mikewa Nur ta yi nata kokarin fita batare da tace komai ba, dan haka Mamy ta mike ta biyo bayanta.

Bakin gadonta ta sameta zaune tana cigaba da kuka dan haka Mamy ta zauna a gefenta tare da cewa "Ke da wa? Abdallah ko?" Kai Nur ta girgiza dan haka Mamy tace "To waye? Girgiza kai Nur ta sake yi dan haka Mamy tace a'a bazai yiyuba Nur haka kawai mutum na kukane? Bana son irin wannan gaskiya, yau kowa gidan nan farinciki yake mene ne naki na kuka? Ganin Nur Bata da niyar magana Mamy ta mike ta fice, fitan Mamy ba jimawa Aunty Saratu ta shigo, kallon Nur ta yi cike da mamaki ta zauna gefenta tare da cewa, Wai maye haka Nur? Hannu Nur ta mika ta kara share hawaye, mene ne? Me aka miki? Aunty a fada bayan ta jawo Nur jikinta" Nur ta dauki tsayon lokaci ba tare da datace komaiba, zuwa can ta shiga bawa Aunty labarin abin da ya faru tsakaninta da Poul, bayan ta gama tace Aunty na gaji ya takura min. Fuskar Aunty Saratu cike da murmushi tace, "Nur dan wannan ki ke kuka? Wannan ai ba wani abin damuwa bane" Dagowa Nur ta yi ta kalli fuskar Aunty yayin da Aunty take cigaba da cewa, "Ni dama tun da naga irin zaryar da yar uwanshi take a gidan nan na zargi haka, Allah ne ya nuna mishi ikonshi, wannan shi zaisa ki sake agari batare da ya takura miki ba, ni dama bana wani son aje a yi kararsa, sabo da yana da kudi Nur, abin mu zaifi tabawa ya lalata mana suna, yaron yana takama da kudi Nur, yanzun abin da nake so dake ki kwantar da hankalinki ki daina sa

damuwa, yanzu bazai iya cutar dake ba, kuma ta sanadinki dabi'unshi suna iya canzawa ya zama mutumin kirki." Wuri daya Nur ta tsurawa Ido tare da cewa, "Aunty tsoro nake ji, Kuma ni na rikici, Inajin tsoro sosai kuma ni bansan yadda zanyi ba"

Kallon Nur Aunty ta yi sosai sannan tace, "Bari na fito miki a mutum, tun da naga kuruciya na dibanki, duk da ada Ina miki kallon wadda wayaunta ya wuce na shekarunta, amman yau duk kin daburce, idan baki fahimtaba ina son ki gane Poul son ki ya ke yi" Cike da mamaki Nur tace to Aunty ana yin haka ne dama? baya sallah fa" Nur ta fada tare da kallon cikin idon Aunty, "Cemin zakiyi ba fa musulmi bane, Ina sane Nur bakisan ta sanadinki konai na iya canzawa ba?" Wannan karon shiru Nur ta yi tana sake-sake cikin ranta, zuwa can ta dago ta kalli Aunty tace "Su Abba baza su yadda da wannan ba ai"

"In ji wa ya gaya miki? wuyarta ace be musuluntaba, iyayenku sunsan abin da suke yi, abu daya zan gargadeki akai karki yadda ko hannunki ya sake rikewa, ki gaya mishi wannan haramunne a addininku, sannan in dai ba a gidan nan ba karki tsaya hira dashi a titi, duk da nasan zai bukaci hakan, amman karki yadda, idan da gaske sonki yake yazo ya tunkare Abbanku ya nema izini tukuna...

Cikin sauri Nur ta katse Aunty da cewa "Ba musulmi bane fa" Wannan karon cikin tsayawa Aunty tacewa Nur "Ina ruwanki?" Sunkuyar da kai Nur ta yi yayin da Aunty taci gaba da cewa, "Kamar yadda kika saba haka zakici gaba dayi, duk ranar da ya bude baki yace son ki yake sai kice yaje ya gayawa Abbanku, ki sake jikinki ki daina tsoronshi ranar Monday idan zaki makaranta ki biyawa Zainab kamar yadda kuka saba."

Wannan karron Nur batace komaiba saidai ta samu nutsuwa sosai duk da cewa har yanzun tana tunani akan zancen Aunty, mikewa Aunty ta yi ta fita bayan ta Kara kwantar mata da hankali, Aunty tana fita Nur ta shiga bayin dake makale jikin dakinta, auwala tayo sannan ta yi sallah, bayan ta idar addu'oi ta yi wadda suka Kara samar mata da nutsuwa, bata tashi a wurin ba har saidai aka yi isha'i sannan ta koma gado, wannan lokacin wani irin nishadi ta tsunta kanta aciki musamman lokacin da ta jiyo gud'a tare da hayaniyar mutane afalo, durowa ta yi a gadon cikin sauri ta nufi falon tana cike da fara'a, abokan Yaya Abdallah ta gani zazzaune a kasa yayin data hangi Abdallah zaune saitin kamar Mamy, da alama neman Albarka yazo yi zai shiga dakin Amarya, yin wannan tunanin ya kara fadada murmushi Nur, zagayawa tayi can bayan kujeran da Mamy take ta zura hannunta ta dafa kadan Mamy tare da leken fuskar Abdallah fuskarta cike da murmushi, tun zuwanta Abdallah ya kula da ita, saidai be nuna ma yasan da zuwan nataba bare ya daga kai ya dubeta, 'yan uwan Mamy ne suka mishi nasiha daka karshe Mamy tasa albarka sannan suka mike zasu tafi, wannan karon ma farin cikene ya sake lullube Nur dan haka ta daga murya tace, "Yaya Abdallah!" Juyowa yayi ya kalleta tana wasa da hannunta akan kafadan Mamy, hannunta daya ta daga mishi tare da yar dariya tace "Allah ya sanya alheri" Azuciye Abdallah yayi kanta cikin tsawa yace "Ina wasa dake ne?" Baki Mamy ta bude tare da cewa daga addu'a? Abokansa ne su ka jashi Dan haka ya fice a  falon yayin da mutanen dakin suke dariya haka itama Nur dariya tayi domin ko kadan batajin haushin hargaginshi ba, afalon ta zauna akacigaba da hira da ita, washegari da wuri aka yi budankai kowa ya watse, duk bakin da suka kwana a gidan sunje gidan Amarya sun ganu gidan yayin da kowa idan ya dawo yake mamakin haduwan dakin Bilkisu, yayin da ake ta yabon amarya kowa cewa yake yariya karama Mai hankali ga sanin darajar mutane, washegari ma Aunty da Umma sukaje suma haka suka dawo suna yabawa, Washegari ya kama Monday dan haka Nur da wuri

ta shirya, bayan tawa su Mamy sallama ta nufi gidan su Poul gabanta na faduwa sosai.
Tura get din kawai ta yi ta shiga, Mai gadin gidan ne ya juyo ya kalleta sannan ya dauke kanshi, tundaga nesa ta hanga Poul zaune a farfajiyar gidan, Saida gabanta ya fadi ganin shi sannan Kuma batama taba ganinshi zaune a gurin ba. Wannan karon kasa kwalawa Zainab kira ta yi kamar yadda suka saba, tsaye ta yi ita bata shigaba ita bata koma ba, tun da ta shigo Poul din yake binta da kallo, zuwa can ya rufe jaridar hannun shi tare da mikewa tsaye ya fara takowa, ganin haka Nur ta fara ja da baya batare data daina kallonshi ba ta ke nufar kofar gidan. Ganin haka ya tsaya cak fuskarshi na dauke da murmushi yace "Yun da bazaki tsaya inzo ba to ki kira Helen din ku wuce." Wannan karon ma bata tanka ba komawa yayi ya zauna Yana cigaba da kallonta fara'ar fuskarshi Bata yanke ba har wannan lokacin, ganita jima tsaye Kuma da alama Bata da niyar kiran Helen din yasashi yace "Helen!" Amsawa ta yi da karfi yayin da ya sake daga murya yace "Ga kawarki, fitowa ta yi da Jakarta a hannunta tana kokarin goyawa ganin haka Nur tai saurin ficwa agidan, cike da mamaki Zainab ke kallonta domin Bata sa rai zata biyo mata ba. Misalin Uku ta dawo makaranta afalo ta samu Ummy zaune ita da Mamy, rungumarta tayi itama Ummy cike da Murmushi tace ke na yi ta jira ki dawo ki rakani gidan Abdallah" Batare da ta Nur ta Bari Ummy ta rufe bakiba tace "Ai bansan gidan ba Ummy." Mamy ce tace "Ita ta sani tashi ki shirya tun dazon take jiranki."
Karyar da kai Nur ta yi tare da yin kwalwal da Ido tace "Mamy ni baxani ba gaskiya."
"Au bazakiba?" Ummy ta fada tare da cigaba da cewa "Toni barin wuce ai bansaniba dan ban zauna na bata lokaciba ba."
Mikewa Nur tayi tare da amsar Jakar Ummy tace "Muje in rakaki mota ni sai in tare da Mamy ne zani."
"Toh Allah ya taimaka" Ummy ta fada tare da yiwa su Mamy sallama, Bayan dawowan Nur fada Mamy ta mata akan kin bin Ummy data yi kiri-kiri. Ranar da suka cika kwana na hudu da tarewa Bashir yazo daukan Nur zuwa gidan Abdallah, wannan karon ma kememe taki zuwa, dan haka Bashir ya tsareta da tambayan dalilinta nakin zuwa, ganin babu wasa a idonshi ta ce, "Kawai nafi son in je ne tare da Mamy kasan yanzu haushina yake ji yana iya dukana"
"Kizo muje bazan bari ya dukekiba" tashi Nur ta yi da ga kusa da Bashir ta koma can bayan Mamy tare da cewa "Ni gaskiya Yaya kaje abin ka ninafi son inje tare da Mamy, dan in da ita ko kallon banza bazai min ba" Mamy ce tai saurin cewa Ashe kuwa bazaki ba Nur, ni me zai kaini gidan su, ki tashi maza kina bata mishi lokaci dare na yi" Mikewa Nur ta yi tana me buga kafarta tare da kunkunai take cewa "Ni Mamy nace bazaniba, ko an hana shi ya dakeni idan ya yi ta hararata fa, saina dawo gida na ce ya harareni kuma kuce na yi hakuri ba gara banjeba" Karake maganar ta yi tana hawaye dan haka bayan Mamy ta gama kare mata kallo ta juya ta kalli Bashir da ke zubawa Nur harara tace "Jeka abinka" Kamar jira yake ya mike ya nufa kofa, cikin murya kuka Nur tace "Yaya ka gaida Aunty Bilkisun" Wani irin kallo Mamy ta sakewa Nur sannan ta kalli bayan Bashir da ya wuce ba tare da yace komai ba. Tun daga ranar babu wadda ya sake mata maganar zuwa gidan Bashir har suka cika kwana shida da tarewa wadda ya kama ranar ne Yaya Bashir zai wuce karatu, misalin karfe takwas na safe ta gama shirin makaranta, fitowa ta yi domin yiwa su Mamy sallama, tun kafin ta isa falon ta jiyo muryan Yaya Abdallah babu tsoron da taji domin dai tasan babu abin da zai mata, dan haka ta Isa falon tare da Sallama, duk mutanen dake falon amsawa suka yi Abdallah ne kawai be ma waigo bare ya amsa, karasawa ta yi kai tsaye ta nufa gurin amarya dake zaune daf da Yaya Abdallah cikin

katon hijjabi dan haka bakama iya hangen kayan dake jikinta, hannunta ta rike tare da cewa "Auntymu Ina kwana" cikin sakin fuska tare da yanayin jin kunya ta amsa yayin da Nur ta kalli Inda Yaya Abdallah yake tace "Yaya Ina kwana?" Tamkar besan da ita a wurin ba haka yayi, dan haka ta sake cewa "Yaya Abdallah Ina kwana?" Batare da ya kalli In da Nur take ba yace "Mamy in tafi zakiyi Mai bayani ko?" Cikin mamaki Mamy ta ce "Ban gane ka tafi ba?, Ko ba komai ai dai ka bari ku yi sallama ko?" Nur sakin hannun Bilkisu ta yi sannan ta juya tai ma Mamy da Aunty Saratu sallama ta fice abinta, gidan Poul ta nufa tana me ardu'ar Allah ya sa ya riga ya fita acikin zuciyarta, bayan ta tura kofar ta saki ajiyan zuciya ganin babu kowa sai Mai gadi, Amma da Alama Poul din yana nan danga motar shinan an sakko da ita, kira ta kwalawa Zainab ta amsa sannan ta fito daga bayanta ta hangi Poul tafe, dan haka ta ji gabanta ya fadi, kallo daya yawa gefenta sannan ya juya ya shiga motar, ita ko Zainab matsowa ta yi tace "Nur zo ga Yaya yace zai kaimu" gabanta ne ya sake faduwa Dan haka tai saurin nufar get din gidan tare da cewa "Ni bazan hau motar kowaba."
Muryanshi taji kamar daga sama yana bawa mai gadin umarnin ya rofe kofar gidan dan haka ta kara sauri, saidai ki kafin takai wajen mai gadin ya rufe kofar, dan haka ta tsaya cak tana kallon motar Poul din  dake tahowa zuwa get din gidan. Daidai saitinta suka tsaya, Zainab na gefensa, ganin haka ta yi kwalkwal da Ido, Poul din ne ya sakko ya bude bayan motar ta gefen da take tsaye yace "Shiga muje"
Kallon shi ta yi sannan ta kalli motar daya bude yake rike da murfinta, Nan take zancen Aunty ya shiga dawo mata...

CIWON 'YA MACE
By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 37-38

Kallon shi ta sata fuskarta daure sosai sannan ta daga kafa ta shiga motar ta zauna, rufewa Poul yayi sannan ya zagaya ya shiga alokacin da Zainab ke waiwayen Nur tana murmushi, shima kallonta yayi kadan sannan yaja motar, gaba daya hankalin Nur a tashe ya ke, dan haka ta sunkuyar da kanta kasa tana wasa da hannunta, daka ganta zaka fahimci tana cikin bacin rai.
Tafiya su ke acikin motar shiru sai wata wakar inyamuranci dake tashi a radio motar, zuwa can Nur ta dago kanta, gani ta yi Yana kallonta ta madubin dake gabanshi, dan haka ta karkace da sauri ta juya mashi kafada, murmushi Poul yayi, duk da cewa ta juyar da fuskarta amma ya kasa cire idonshi akanta, abakin makarantar ya tsaya, yana tsayawa Nur ta Bude motar ta fice, idon shi akanta ya ciro kudi ya mikawa Nur yana fadin ke da ita, itama Zainab idonta akanshi ta amsa kudin, mamakine ya kama Zainab ganin in da yake kallon Nur, bayan ta amsa ta kalli kudin sannan tace "Mun gode." Muryanta ne ya dawo da shi cikin hankalinnshi, kokarin tada motar yake batare da ya amsa ba, Saida ya ga shigansu makaranta tukuna ya wuce, sosai jikin Zainab yayi sanyi ganin wannan labari dake faruwa, tunani da yawa azuciyar Nur akan wannan abin, a yanzu ko tantama bata yi yayanta poul ya fada tarkon son, wurin Nur ta maida

hankalinta data shige ajinsu afusace.
Bayan sun zauna a ji ma zama Nur ta yi kamar kurma duk yadda Zainab ta so su yi magana ki ta yi, haka Kuma ko da aka tashi kafin ta farga Nur ta wuce, hanya ta kamo ita daya acikin ranta take sake sake, haka nan take jin tausayin Poul acikin zuciyarta.
Bayan Nur ta Isa gida sannu da gida tayiwa su Mamy sannan ta wuce dakinta, cak ta tsaya bakin kofar dalilin gani mutum kwance a kan gadonta, sai yanzu ta tuna da dazon tabar Abdallah da Amarya, kenan be wuce da ita ba, jakar makarantar ta ajiye sannan ta nufi falon, tun kafin ta isa take fadin Mamy Yaya Abdallah be wuce bane? Na dauka yaune tafiyarshi ai" Karake maganar ta yi tana kokarin zama kusa da aunty Saratu. Yayin da Mamy ke cewa, "Ya wuce Nur tun safe"
"Toh Kuma naga Aunty Amarya anan" Nur ta fada tana kallon fuskar Mamy, "Eh nan zata zauna"
"Har ya dawo?" Nur ta sake tambaya cike da mamaki, wannan karon Aunty Saratu ce tace, "Ya ce idan ya gama saita komai zai dawo ya dauketa."
Tabe baki Nur ta yi yayin da Aunty Saratu ta sake cewa "Ta tashi baccin kuwa?"
"A'a Bacci take" Nur ta bata amsa, Mamy ce tace "Kije ki cire kayan makaranta idan kin ta tashi kizo ki dauki abincinta. Mikewa Nur tayi bayan ta amsa sannan ta nufi dakin, kayan makaranta ta cire sannan ta nufi bayi, zuwa can ta fito ta sake bin Bilkisu da kallo, gani ta yi kamar idonta biyu dan haka tace Aunty Amarya! Bata amsa ba, ahankali Nur ta karasa bakin gadon ta zauna tare da leken fuskarta tana sake cewa "Auntymu!"
Wannan karon hannu Bilkisu ta sa ta share fuskarta sannan ta juyar da kanta dayan gefen tare da cewa "Kin dawo?"
"Eh na dawo" Nur ta fada na mai nazarin yanayin da Bilikisu ke ciki, kamar kuka take dan haka Nur ta sake cewa, "Aunty ashe kina jina to ki tashi su Mamy nata jira ki tashi kici abinci."
"Banci Nur, bana jin yunwa." Lumshe Ido Nur ta yi Jim yanayin muryanta sannan tace "Kinci wani abin ne to?"
"Eh kafin mu fito mun ci abinci." Wannan karon Murmushi Nur ta yi sannan tace "Ke dawa?"
"Cewa na yi kafin mu taho nan ni dashi mun karya" Dariya Nur ta yi afili tare da cewa "Ki fadi Sunanshi mana"
"Haba Aunty tun safe ne fa, kina son kice har yanzun bakyajin yunwa?"
"Bana ji Nur" Dariya Nur ta sake yi sannan tace "Kenan bazaki sake cin abinciba har sai ranar da Yaya Abdallah ya dawo?" Wannan karon yunkurawa Bilikisu ta yi ta tashi, bayi ta shiga ta wanko fuskarta sannan ta fito, batasan meye dalili ba tun da Nur ta fara magana taji ta samu nutsuwa tun bayan tafiyan Abdallah.
Nur kuwa har yanzun fuskarta cike take da dariya domin ta gane Bilikisu kewan mijinta take. Mikewa tayi ta fito falon, Aunty Saratu na ganinta tace yaya aka yi Nur da ganin ki akwai magana a bakin ki, kamar jira Nur take ta fashe da dariya tare da waiwayen bayanta cikin dariya tace "Ashe idonta biyu aunty kuka take Yaya Abdallah ya tafi ya barta, Karake magar tayi tana kyalkyata dariya, ita ko Aunty daure fuska ta yi sannan tace "Haka ta gaya miki?"
Kafin Nur ta yi magana Mamy ta ce, "Ai dole bazataji dadiba Saratu, dashi ta saba kwana shidda da rabota da yan uwanta wa ta saba dashi anan? Amman ya tsallaketa ya barta kuma tafiya ba kwana biyu ba ba uku ba wata da watanni, abin da nake nuna muku kenan, ki dauki abinci kije kuci kema aiki ya same ki" Mamy ta fada tana kallon Nur, tuni Nur ta tabar dariya

tunda taji ta bakin Mamy, dan haka koda ta shiga kicin tana deban abincin tana jinjina abin, har ta gama zuba abincin ta koma daki tunanin da take kenan, zaune ta samu Bilkisu ta yi tagumi, wannan lokacin tausayi tabawa Nur, dan haka ta zauna daf da ita tare da cewa, "Aunty kici abincin barin yi sallah inzo" Mikewa Nur tayi saidai har ta idar da sallah Nur bata taba abincinba dan haka Nur ta zuba masu tare sannan ta ce "Muci Aunty" Babu laifi Bilkisu ta danci kadan sannan tace ta koshi, a daidai wannan lokacin aka kira ta a waya, da sauri ta dauka yayin da Nur ta bita da kallo, wayar tasa a kunne tare da komawa bakin gado ta zauna, cikin shagwaba Bilkisu tayi sallama cikin wayar hawaye taga Bilkisu na cirewa a gefen idonta tsayon lokaci batace komaiba, da alama sauraron mgn take cikin wayar, zuwa can taji tace, "In je gida mana to" Shiru ta sake yi zuwa can ta sake cewa, "A'a" Murmushi taga ta yi sannan ta sauke wayar. Tunda ta fara wayar Nur Bata cire idonta akantaba dan haka da taga ta sauke wayar fuskarta sake tare da saurin mikewa tana Murmushi, tun da ga lokacin Bilkisu ta sake jikinta Hira suka yi da Nur tamkar Daman can sunsan juna, misalin takwas da rabi na dare Nur ce zaune adakin Mamy yayin da ke kokarin gyara kaya tana sakawa cikin sif, Waigowa ta yi ta kalli Nur tare da cewa "Taci abincin kuwa?"

"Eh taci Mamy harma sun yi waya da yaya."

"Yauwa ya kyauta yayan, yanzun wani abu kike so?"

"A'a" Nur tace tana kallon cikin idon Mamy. "To ki koma wurinta mana tafi jin dadin zama idan kina wurin ko?" Amsawa Nur ta yi ta fice badan ranta yaso ba, lokacin da ta shiga dakin kan gado ta samu Bilkisu tana danna wayarta tana murmushi da alama chart take, dan haka ta nema wuri daf da Bilkusun ta kwanta saidai ta kasa cire idonta akanta, murmushi take sosai zuwa can Nur taga ta saki wayar ta fashe da dariya cike da mamaki Nur ta kalleta tare da tashi zaune tana sake binta da kallo, ganin irin kallon da Nur ke mata yasata cewa "Nur kina ganin yayanki zai kasheni da dariya ko? Wallahi in dai zaka biye masa sai yasa cikin ka ciwo" Wayarta ta jawo tana fadin "Barin kashe data na kawai Saida safe."

Nur kasa cewa komai ta yi sabo da mamaki, sai take ganin kamar mafarkine take yi, wannan fuskar tashi har ta iya bada dariya, wani sashi na zuciyarta kuwa farin cikine ya kamata, tunda dai har Yana son matarshi har yana wasa da dariya da ita ai AlhamduLillahi, wayar Bilkisu ne ta sake daukan Kara, dauka ta yi tasa a kunnenta zuwa can tace "Bacci nake ji" shiru ta sake yi zuwa can ta sake fashewa da dariya tare da cewa "Ka bari karkasa cikina ciwo, gashi barin bawa Nur ku gaisa" shiru taga ta yi tare da ya mutsa fuska, harta sauke wayar fuskarta bata dawo daidai ba, ganin haka Nur ta juya mata baya domin tasan bazai wuce akan sunanta data Kira bane, ita Bilkusu kallon Nur ta yi sosai sannan ta kwanta cike da tunani, washegari da safe bayan Nur ta tafi makaranta Abdallah ya kira Bilkisu bayan sun gaisa ta ce, "Baby jiya daga cewa ga Nur ku gaisa sai ka hau fada" Lumshe Ido Abdallah yayi sannan yace "Banson maganar yariyar ne kawai, ko sunanta banson naji an kira" Cikin son taga ya sakko tace "To aini ban saniba dasai ka gaya min, jiya daker na yi bacci"

"Ki yi hakuri bansan lokacin dana fara fadan ba amman ba'a dakinta aka barkiba ko?" Jimmm Bilkisu ta yi zuwa can tace "Tare muke adakinta ne"

"Zanyi magana da Aunty a baki dakina ki zauna bana son alakanki da ita."

"Baby saboda me? Ni Inajin dadin zama da ita, tana da kirki"

"Eh, Nima ba cewa na yi bata da kirkiba, karkiga wai tana kusa da sa'arki ki saki jiki da ita, ba kowanni abu Zaki dinga bari tanaji ba, kuma idan na kiraki a waya ki daina amsawa a gabanta"

Cikin rashin fahimta Bilikisu tace "Amman in tambaye ka?"
"Ina jinki?"
"Wai Nur ba kanwarka bace?" Ajiyan zuciya Abdallah yayi sannan yace "Wacce irin tambaya ce Wannan kuma? so nawa zan gaya miki adadin 'yan gidanmu?" Cikin kwalwakl da Ido tace "Ai ce min ka yi Nur ce autarku" Cikin son kawar da baccin ranshi yace "Eh itace auta"
"Mamy ce ta haifeta?"
Cikin sauri yace "Eh, Bakiga suna kama ba?"
"Na gani, to kaifa?" Wannan karon dariya Abdallah yayi sannan yace "Ai na gaya miki nine na farko a wurin Mamy da Abba" Cike da gamsuwa tace "Na gane, to amma Nur ba Abba bane ya haifeta?"
"Waye to?" Abdallah ya jefa mata tambayar, jin haka yasa Bilikisu cewa "Aini kai nake tambaya"
"To Abba da Mamy sune iyayenmu gaba daya Baby, idan dan abin da kikaji na fada ne akanta kike tunanin ba kanwata bace akwai abin da tamin ne."
"Toh ka yi hakuri kaji"
"Ai na hakura, amman dai bana wasa da ita, kema kuma bana son ki sakar mata fuska"
Dole Bilikisu tabar mgnr badan ankai inda take son akai ba domin har yanzun zancen be shigeta ba.  Hira suka ci gaba dayi kafin su kare har ta manta da zancen Nur.

****

"Mai yasa zaki firgice haka" Poul ke fadin Haka alokacin da ya tare Nur adaidai kofar gidansa bayan sun rabo da Zainab. Kokarin gewayeshi take ta wuce saidai sai shan gabanta yake ya hana mata wucewa, kwalkwal Nur ta yi da Ido tare da cewa "Ni ka rabu dani banso" lumshe idon sa yayi tare da cewa magana zamu yi sai ki wuce.

Dagowa ta yi ta kalleshi cikin sauri tai kasa da kanta dama can bata iya hada Ido dashi domin sosai ya ke mata kwarjini, yau kuwa wani irin abu ne taji wadda ta rasa da wanni sunan zata kirashi, gaba daya ji ta yi kamar zazzabi na son rufeta dan haka ta tsaya ta kasa cewa komai, ita bata wuceba ita Kuma Bata dago ta kalleshi ba, zuwa can ya ce, "Nur yanxu bana iya bacci sosai kodayaushe sai inji Ina son kallonki, gashi kin min nisa ban isa inzo gidanku ba, ke Kuma ko kinzo nan bakya bani fuska." Sunkuyar da kai Nur ta yi bakinta zunbure batare da tace komai ba, zuwa can ya sake cewa "Ina son ki dinga bani ko minti goma ne kowacce Rana nayin magana dake" Can kasan makoshi ta ce "Sabo da me?" Lumshe Ido Poul yayi zuwa can ya sauke akanta tare da cewa "Sabo da ina son ki."
"Mu ba haka muke yi ba" Cikin Ido ya kalleta sannan yace "Yaya kuke yi to?"
"Gidanmu zakaje sai ka gayawa Abbanmu " Da sauri ya dago ya kalleta tare da kiran sunanta ahankali ta dago ta kalleshi, jawur taga idonshi cikin yanayin dake nuna yanajin tashin hankali, cike da muwa taga ya bude bakin sa idonsa cike da ruwan hawaye yace, "Amman kina ganin idan naje zai amince?" Tsintan kanta ta yi da cewa "A'a bazai aminta ba" Tsayon lokaci taji bece komaiba dan haka ta dago ta kalleshi, gani tayi yana kawar da fuskarshi duk Yana yinshi ya canza da ga ishashshe mai takama da naira ya koma kamar mai zama da damuwa, daker ya iya cewa "Amman ke kin amince dani?"

Cikin Sauri Nur ta girgiza kanta duk da cewa tana tuna zancen Aunty Saratu amman ta kasa yi kamar yadda tace. Bayan ya gama kare mata kallo yace "Mai yasa Nur?" Wannnan karon ma tsintan kanta ta yi da cewa "Bakeje gidanmu ka gayawa Abbanmu ba." Jimmm, yayi zuwa can

yace "Na gane, to ai kince bazai yadda ba ko? Kina da wadda zaki aura ne?" Wannan karon kai ta girgiza alamar a'a dan haka ya sake cewa to meye dalinlin? Sunkuyar dakai tayi tana mai takaicin yadda take kulashi har yanzun ta kasa wacewa ta barshi, idon shi akanta ya sake cewa "Ina jinki." Can kasan makoshi ta ce "Kai ba musulmi bane" Wannan karon shiru yayi tsayon lokaci, zuwa can ya ce, "Amman ai addinin ku be hana ba." Can kasan ta sake cewa A'a addinimu be yadda da mace ta auri na miji wadda ba musulmiba." Jimmm, yayi tare da sunkuyar da kanshi kasa, gani yayi Nur tana kokarin wucewa Dan haka yai saurin cewa "Dan tsaya" Tsayawa ta yi kamar yadda yace sannan ya ce, "Ni Kuma Gashi Ina son ki yaya kenan?" Wasa Nur ta shiga yi da hannunta tsayon lokaci batare da ta ce komai ba, bayan Poul ya gama kare mata kallo yace, "Ina jinki?" Dagowa Nur ta yi ta sata kallonshi sannan tace, "Hakan ba daidai bane" Kallonta Poul yayi sosai sannan yace, Na gane, shikenan amman yanzun kinsan mene ne?" Kai Nur ta girgiza tare da cewa A'a, Kara matsowa Poul yayi tare da cewa "Nasan kin sanni barin sani, ina neman wani taimakone a wajenki, idan bazakiyi dan niba inci albarkacin Helen."

Nur na wasa da hannunta tace "Mene ne shi?"

"Sai kin min alkawari tukuna in fada miki" Batare da Nur ta yi tunanin komai ba tace "Na yi"

"Na farkon shine kizo mu dan shiga daga cikin gida kin ga nan akwai idon mutane, na biyu kuma sai mun shiga zan gaya miki...

CIWON 'YA MACE 20

By

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 39- 40

Dagowa Nur ta yi ta kalleshi har yanzun ita ya ke kallo, cikin sauri ta sunkuyar da kanta kasa tana wasa da hannunta ganin haka Poul ya ce, " Ba cikin gidan zamu shigaba daga bakin get zamu tsaya in yi maganar da zanyi sauki wuce" Cikin Sauri Nur ta girgiza kai alamar a'a, kallonta yayi  ya sake cewa tsoron me kike ji? Bayan gidan ba bakonki bane, kuma da mutane a cikin gidan nan bakin get ma akwai mai gadi, idan cutar da ke zanyi ai ba anan zance mu shigaba ko? Wannan maganar da yayi yasa ta tuna waye shidin, hakika duk wadda yaganta tsaye da Poul abin zai bashi mamaki matuka, dagowa ta yi ta kalli layin nasu babu kowa, tsoro ne ya shigeta kar wani dan gidan su yazo ya ganta tare da Poul, yin wannan tunanin yasa ta nufi shiga gidan, biyo bayanta Poul yayi yana Mai sauke ajiyan zuciya, mai gadin dake can kofar dakinsa ne ya juyo ya kallesu sannan ya dauke kansa, in da Nur ke tsaye Poul ya tsaya tare da kureta da Ido, sosai kallon da yake mata ya ke sata shiga cikin damuwa domin a duk sanda yai mata irin kallon tana shiga cikin wani yanayi wadda take rasa gane kanshi, ganin bashi da niyyar magana ta ce, "Ka yi maganar sauri nake yi  a gida za'aga na dade" kanshi ya shafa tare da matsowa daf da ita, can kasan makoshi ya ce" Duba yadda na zama Nur, gaba daya banda nutsuwa, wata daya da ya wuce idan ance min zan zama haka bazan yaddaba, yau da kika tsaya muka yi magana bakiji yadda naji dadiba, yanzun abu daya nake son kimin dan

Allah karkice a'a, ki taimaka min in samu nutsuwa yau in yi bacci mai dadi" Dagowa Nur ta yi ta kalleshi, har yanzun a burkice ya ke, idon shi kawai ya isa ya tabbatar maka da hakan, cigaba yayi da cewa, "Zaki taimaka min?" Ahankali Nur ta daga kanta alamar eh, matsowa ya sake yi ganin haka Nur ta kara mannewa jikin get din kasa-kasa yace, "Dan Allah ki dan tsaya na rungumeki kona minti biyu ne" Cikin sauri Nur ta dago ta kalli jajayen idonsa tare da girgiza kanta, ganin haka ya kafeta da Ido tare da cewa mai yasa?" Kawar da kai Nur ta yi sannan tace Haramunne" Lumshe Ido yayi zuwa can ya bude su akanta tare da cewa, "Haram? Wannan karon ma kai ta daga mishi tare da cewa "Eh, babu kyau hakan ba daidai bane"
"Na gane, to hannun fa? Zaki bani hannunki mu gaisa?" Wannan karon ma kai ta girgiza alamar a'a, yawu Poul ya hadiye sannan yace "To shikenan amman zan iya baki waya anjima mu gaisa? Kai Nur ta sake girgizawa alamar a'a, cikin rashin jin Dadi yace "To shikenan, je ki na gode" kamar jira Nur take ta wuce tana daf da fita gidan ya sake kiranta, tsayawa ta yi, wani kati ya mika mata tare da cewa akwai number ta a jiki, anjima ki kirani" amsa kawai ta yi ta juya domin sosai ta kosa tabar wajen. A sanyaye ta isa gida, sannu taiwa Mamy sannan tai saurin wucewa dakinta domin gani take kamar mamy zata gane bata da gaskiya, a yadda ta shiga dakin yasa Saida Bilkisu ta bita da kallo, domin yanayinta ya nuna kamar batasan mai take ba, Daker ta iya cin abinci ta yi duk abin da zatayi sannan ta wuce islamiyya. Bayan sati daya Nur ce tsaye bakin makarantar tana jiran mashin, tun daga ranar da Poul ya tareta ta daina jerawa da Zainab, ana tashi take hawa mashin ta wuce gida abinta, yauma tsaye take tana jiran mashi taga motarsa ta tsaya gabanta, wani irin faduwa gabanta yayi, bude motar yayi ya fito, gabanta ya tsaya tare da cewa, "Sannu Hajiya" kawar dakai Nur ta yi kasa-kasa tace "Ina wuni"
" Lafiya" Ya fada idonshi a kanta, "Ya gida da karatu?" Wannan karon ma kasa-kasa Nur tace Lafiya lau" Zo muje mana in sauke ki? A'a mashin zan hau" Jimmm yayi zuwa can ya ce, "Shikenan, mai yasa baki kirani ba ranar dana baki kati na?" Na mance ne" Nur ta fada tana wasa da hannunta, shiko Poul cike da damuwa ya maimaita zancenta sannan ya ce to yanzun na tuna miki, dan Allah ki kirani.  Da kai anur ta amsa Motar ya koma ya shiga tare da cewa "Zaki kirani ko?" Wannan karon eh tace tare da tare mashin tahau, mashin din na shirin tashi ya taho da motar wurin ya daga murya ya ce, "Katin na nan ko?"
 "A'a ya bace" Wani katin ya sake cirowa ya mika mata, sannan ya figi motar kamar zai tashi sama ya bar wajen, ko da Nur ta isa gida ciro katin ta yi ta kalla kamar yadda ta yi ranar da ya bata wancen, bayan ta gama karewa katin kallo ta dauko Littafin da ta saka wancen tasa wannan, sannan ta maida Littafin ta ajiye, tsayon wata daya suke shafe a haka, idan yaga kwana biyu bata Kira ba sai ya sake aiko mata da wani katin, harsaidata tara koma sha tara batare da ta kiraba, yasha aiko Zainab ta kawo katin tare da rokon ta kira din, amman ko sau daya Bata taba kwatanta kiraba, sosai suka saba da Bilikisu a yanzun hira suke sosai ta saki jikinta dasu Mamy ma, yau kawar Bilkisun ce tazo, wannan shine zuwanta na biyu gidan, tun a zuwan farko suka saba da Nur, dan haka yauma har da ita ake hiran, labarin saurayinta take bayarwa, sunata dariya, zuwa can kawar Bilkisu Madina ta kalli Nur tace "Ke baki bamu labarin saurayin ki ba?" Tabe baki Nur ta yi tare da cewa "Ni bani da saurayi karatu nake son na yi sosai."
"Wallahi karyane kice baki da saurayi, mu ma ai duk karatun zamu yi Amman ai da samarin mu" Madina ta fada tana kallon Nur, "Niko bani dashi, ku gani kuke na girma ko?"
 "Eh mana to dame muka fiki" Bilkisu ta fada tana dukan kanwason Nur, dariya Nur ta yi sannan

tace to awurin Abba da Mamy har yanzu karamar yariya ce ni, kofa waya basu yadda na rike ba" Dariya Su Bilkisu suka kwashe dashi yayin da Madina tace "An barki a baya wallahi"
"Ba wani baya, ni haka yafi min, wayar ma mai zan da ita, duk wadda nake son nai waya dashi zan iya amsan wayar kowa a gidan nan nayi wayata banda matsala da waya" Domin karatu nake son na yi sosai." Bilikisu ce ta ce "Wai da gaske baki da saurayi? Maganarwa naji kuna yi ke da Zainab ranar ce?" Juya baya Nur ta yi tare da cewa "Wannan yayanta ne fa, waishi a dole sona yake, Kuma ba musulmi bane fa" Zaro Ido Bilkisu ta yi tare da cewa, "Kamar ya bamusulmi ba? Ba kince yayan Zainab bane?" Dan Waigowa Nur ta yi kadan sannan tace, "Eh yayantane amman ita da Mamman su ne masulmi shi arne ne, wai Kuma a hakan ya ke sona" Madina ce tace "Kuma idan Yana sonki fa saikiga ya musulunta."
"Hmm umm lallai, wannan mutumin ne zai musulunta? Bashi da kirki sam, shi a tunanin shi a hakane zan aureshi, kuma nasan Koda ace musulunta yayi Abba da Baffah bazasu yadda ba, ni shiyasa ma ban kulashi, baranma ya Bashir, tab" Nur ta kareke maganar tare da juyawa baya, Jimmm, Bilkisu ta yi yayin data shiga nazari jin Nur takira sunan mazan gidan bata kira na babban yayanta ba, share tunanin ta yi ta hanyar cewa, "Gaskiya ki yi saurayi soyayya da dad" Madina ce ta ce "Ke dallah rufe mana baki, keda kwana shidda da tarewa mijin ya bulaki ya tafi ya barki" Aunty dake kokarin shigowa dakin ce taja ta tsaya alokacin da taji Bilkisu na cewa "Wallahi yadda kike haka nima nake ba bulanin da aka yi" Madina ce tace "Wallahi karya ne, kwanaki shidda fa tare dashi a dakin kice ba abin da yayi miki har ya wuce?"
"Eh mana, alkawari muka yi bazai tabani ba sai ya dawo."
Madina ce ta sake cewa "Eh, ji ya zama dole, amma yadda kuwa ba dole bace, daga ke sai Abdallah adaki kice anyi kwana shidda be kusanceki ba?" Cikin da nishadi Bilkisu tace "a rantse da qur'anin Ubangiji har mukai kwana shiddan abin da kike tunani be shiga tsakanina dashi ba, kuma wuri daya muke kwana."
"Tabb lallai, amman na sarawa Abdallah da kokari, Juyawa Aunty ta yi rike da kular abincin, itako Nur bata saka musu bakiba saidai duk hiran tasu tana jinta cikin kunnenta.

*****

Gaban Mamy Aunty ta dire abincin tare da cewa, "Ikon Allah" Dagowa Mamy ta yi ta kalleta sannan ta kalli kular abincin tace "Lafiya kuwa?"
"Dawowa nayi na kira Nur ta dauka"
"Lafiya ko?" Mamy ta tambaya, hiran da ta juyo ta kwashe ta gayawa Mamy cike da damuwa Mamy tace "Ikon Allah, to Abdallah lafiya yake kuwa Saratu?"
"Nima dai abin ya daure min kai Mamy, sai dai fa kinsan yaso abar bikin har ya dawo watakila shiyasa yayi hakan kinsan yaran nan idan Basu suka yi niyyar abu ba babu wadda ya Isa ya sa su"
Jimmm Mamy ta yi tare dace "Niko da kinsani da baki Gaya min ba wallahi, yanzu zan shiga damuwa da zulkumi, meye ribarshi ta yin hakan to? Idan haka ne manene amfanin auren?"
"Yaran zamanin kenan ai Mamy, faface kawai wata rana zakiga ya dawo ya daukita dan ban tunanin zai iya hakuri har ya kammala batare da ya dawoba, suna waya da ita sosai, kuma kullum mukayi waya saiyace ya take, ta saki jikinta ko a'a, hankalinnshi Yana kanta."
"Ajiyan zuciya Mamy ta yi sannan ta ce, "Shikenan, Allah ya kara karkato da hankalinshi gareta,, Aunty ta amsa da Amin tare da kwalawa Nur kira. Bayan ta amsa tazo ta dauki abincin. Sai yamma Madina ta tafi, har kofar gida suka raka ta ita da Nur sannan suka dawo cikin gidan,

kitchen suka wuce domin yau Aunty tace su zasu yi kirkin ginan, cikin kankanin lokaci suka yi suka gama, suna yi suna kira, bayan sun gama ma jarashi sukayi kamar yadda aka saba, sannan suka koma daki suka yi wanka. Misalin karfe 8:30pm gaba dayansu suka zauna akan teburin cin abincin gidan Amman banda Bilkisu dan bata iya zama wurin har idan Abba na nan, dan haka adaki take cin nata, suna cikin cin abinci Bashir ya shigo, da ledoji niki Niki a hannunshi, afalon ya aje, sannan ya karasa wurin ya zauna, cike da Murna Nur ta gaidashi sannan shima ya gaidasu Abba, Aunty ce ta zuba mishi yaci kadan, sannan ya koma falon ya zauna tare da cewa Nur, "Ki sauri ki gama kizo" Cukalin ta aje tare da mikewa ta dawo kusa dashi, kallonsu Abba yayi sannan yace "Kaga ka hanata cin abincin" "Ta koshine Abba" Ledojin dake nesa dashi kadan ya nuna mata tare da cewa, "Ki dauki ledojincan ki ki kaiwa Amarya inji ango" dariya Nur ta yi sannan ta tsuguna ta deba ladojin, kudi ya ciro ya mikawa Nur ya ce "Kice injishi fa" Amsawa ta yi da to sannan ta juya, Abba da tunda Nur ta mike yake kallon su ne ya kira Nur a lokacin da take daf da shiga kofar da zata sadata da dakin, bayan ta dawo ta tsaya ya kalli Bashir ya ce, "Ita ina nata? Me yasa bazai tuna da kanwarshiba? Bayan ita take debewa matar tashi kewa?" Yar dariya Bashir yayi sannan ya nuna ledan dake hannunshi tare da cewa "Abba ga nata nan ai" Dauke fuska Abba yayi tare da cewa "Yauwa ya kyauta" Ita ko Nur juyawa ta yi takaiwa Bilkisu sannan ta dawo rike da jakar makarantarta tana cewa, Yaya Bashir mun fara jarabawa fa ka dade bakazo gidan nan ba"

"Da banzo ba ai ko a waya baki kirani ba" Bashir ya fada yana mika mata ledar, karba ta yi ta daura a jikinta tare da cewa "Dan wannan?" Wani irin kallo ya yi mata sannan ya kalli Abba, ganin baya kallon su yace, "Kinsan da yaya na saya miki wannan din? Sabulone kawai bani da kudi" Hannu yasa a aljihu ya ciro kudi ya mika mata tare da cewa "Amasa idan zan tafi kiban dubu uku ki rike biyu" Abba Nur ta kallah har yanzun abincin shi yake ci dan haka tace "Kai ka saya min sabulo amman kana son kacewa Abba shine kudin ma so kake suka kamar shi ya bani?"

"Eh mana, ko kinfi son suyita ganin laifinshi?" Ajikinta ya daura kudin sannan yace "Matso mu yi hoto tad'i zani, ta matsamin tana son ta ganki" Cike da zumudi Nur ta aje kayan hannunta a gefe ta matsa kusa dashi, wayar ya mika mata tare da cewa "Amsa ki dauke mu" Kin amsa Nur ta yi ganin inda yake kallonta tace "Kai ka daukemu mana, katuwa zanyi idan na rike wayar"

"Nima bana rike waya idan za'ayi hoto"

Juyawa Nur ta yi ta kalli Aunty Saratu tace "Aunty zoko daukemu, budurwar shi zai nunawa hotunmu Kuma wai saidai ni na rike wayar dan karyayi muni" Daure fuska Aunty ta yi tare da cewa "Nice marainiyar wawonku ko? ku ta hoto ma kuke yi" Karake maganar ta yi da Jan tsaki, batare da Abba yace komaiba ya mike yaje ya amsa wayar tare da cewa "Ni bari na musu" Cike da fara'a Bashir da Nur suka gyara zamansu, hoto daya Abba ya dauka ya mika wa Nur wayar tare da zama cikin falon, kallon hoton Nur ta yi ta kwashe da dariya tare da cewa "Be yi kyauba Abba, baka iya daukan hotoba, shima Abba cike da dariya yace "Kawo ingani" Mika mishi wayar ta yi ya kalla sannan yace "Maye beyi kyanba anan? hannunshi yasa ya nuna Bashir yace "Ga Bashir ga Kuma Maryam, to meye abin da beyin ba? Ko baku bane a jiki?"

"Mune Abba, Amma a karkace ka dauka, wurin mamy da Aunty Nur ta tafi da wayar suma dariya suke, yayin da Nur din ma keta dariya, idonta akan wayar ta nufa Yaya Bashir tare da cewa "Kallah hoton ya Bashir" Dagowa ta yi da nufin kallon sa, gabanta taji ya fadin dalilin ganisa yana tattara katin da Poul ke aiko mata dashi gaba daya suna watse a cinyanshi,

tattarawa yake tare da yi mata wani irin kallo dan haka gaba daya ta rude alamu rashin gaskiya ya bayyana a tattare da ita...

CIWON 'YA MACE 21

By

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 41-42

Ganin inda Nur ta rude ya tattara duk katin yasa a aljihunshi, sannan ya fara tattara littaffan Nur ya mayar cikin jakar ya mika mata, jikinta a sanyaye ta amsa sannan ta juya ta shiga dakin tana satan kallon fuskar Bashir, taso mai maganar saidai tana gudun kar su Abba suji, koda ta shiga dakin tagumi ta yi tana rike da jakar ta kasa ajewa, Bilkisu Dake waya a gefe ce ta kalleta zuwa can ta sauke wayar tare da cewa "Lafiya kuwa Nur?" Bude baki ta yi da nufin yin magana sukaga Yaya Bashir ya shigo, dan haka duk suka maida hankalinsu gare shi, yayin da idon Nur ya nuna zallar rashin gaskiya. Kokarin fita a dakin Bilkisu ke yi Bashir yace tai zamanta saidai duk da haka Saida ta fice.

Bashir kuwa kallo ya karewa Nur sannan yace "So nawa kikaje Ofishin Poul?" Dagowa ta yi ta kalleshi sannan tace "Yaya Bashir ban taba zuwa ba.."

"Karya kike yi? Bakyazuwa me kike da katinshi a jakar makarantarki?" Sunkuyar da kanta ta yi kasa tare da matso hawaye, ganin haka ya sake cewa "Ba magana nake Dake ba?" Wannan karon cikin kuka tace "Shine ya bani"

"Ya baki akan wani dalili?" Wannan karon ma Nur kasa cewa komai ta yi zuwa can yace Cikin fada "Zan mareki kuwa, ba mana nake miki ba?" Fashewa Nur ta yi da kuka tare da cewa "Yaya shi wai Sona yake" Dakowa Bashir yayi ya zauna dafda Nur tare da cewa "Inyamurin? Kintaba zuwa wurinshine?" Wannan karon dakai Nur ta bashi amsa dan haka ya kjreta da Ido tare da cewa "Gaskiya zaki gaya min fa"

"Yaya Bashir wallahi ban taba zuwa ba" Wannan karon ajiyan zuciya yayi sannan ya ce "Mai yasa baki Gaya min ba?"

"Ni ban dauki abin da mahimciba, so yake in kirashi a waya, ni kuma duk sanda ya bani cewa nake yabace amman sai ya Kuma vani wani" Ajiyan zuciya Abdallah ya sake yi tare da cewa zaici ubanshi kuwa, bazai yiyuba arnen banza da wofi kawai, bayan haka ma ai ba mutuncine dashi ba, dawa yake magana a unguwarna, dan ubanshi ko musulunta yayi yanzun waye zai bashi yar shi acikin unguwar na? Idan yace zai kawo mana iskanci sai mu rusa gidan yabar unguwar nan" Mikewa yayi a fusace tare da cewa "Zan kira Abdallah mu yi shawara sai munyi maganinshi."

Bayan fitanshi Nur kara rudewa ta yi dan haka taita kuka tare da tuna zancen Aunty da take cewa karta yarda kowa yaji maganarta da Poul, yanzun gahi ita ba ma kulashi ta yi ba amman abubuwan suna shirin jagulewa.

******

"Bashir naga kiranka dazon ina kan haya" Abdallah ya fada a lokacin da yake kokarin zama adan karamin falon da ya sauka, shafa kai Bashir yayi sannan yace "Eh yanzun zamu iya yin magana?"

"Ina jinka mai yake faruwa?"

"Ina wannan guy din Na gidansu wannan yariyar Helen kawar Nur?" Kafa daya Abdallah ya dauka ya daura akan daya, tare da cewa "Eh, naji, Poul kenan ko?"

"Yauwa, shi, wai shine yake bawa Nur katin Ofishinsa wai yana sonta" Shiru yaji Abdallah yayi tsayon lokaci dan haka ya sake cewa, "Abdallah kana jina?"

"Ina jinka mana kaci gaba Ina ji"

"Katinsa fa yafi ashirin a hannunta, ita kuma dake wawiyace tanata tarawa, yadda Allah dai ya taimaka Bata taba zuwa ba." Katsewa shi Abdallah yayi da cewa "To idan ma taje Ina ruwanka?"

"Ban gane ina ruwana ba?"

"Eh mana, meya dameka aciki? Yanzun dan ka ganta da wadda ba musulimiba shine abin da zaka tashi hankalinka, to Bari kaji, Ni ko da sarkin inyamurai zata yi mu'amala babu abin da ya dameni da ita, wani wahalane banyi da itaba abaya, amma saida ta nemi ta karar min da mutunci..."

Katseshi Bashir yayi da cewa "Amma Abdallah idan ya mata wayaufa ya cutar da ita, Ni dakai ne zamu hadu mu dakatar da abin domin ko musulunta yayi bazamu Bari ya auretaba."

Tsaki Abdallah yaja tare da cewa "Ai saikaje kayi tayi, nikam Ina nan idan sarkin arna zata aura banda matsala" Wacce irin magana ne kake yi haka Abdallah, ni ina maganar nanne har zuciyata matsayinta na yar uwata da bazan bari wani abu ya cucetaba, kaima kuma yadda zanji akanta haka ya kamata kaji sabo da ban fika kusa da ita ba"

Jimmm, Abdallah yayi zuwa can yace "Zaka min rashin kunya ne?"

"Ba haka bane, kawai dai inaganin be kamata ka yanke zumunci bane, naji tayi maka ba daidai ba, amma ai ita yatiyace, idan aka barta wayasan Mai zai faru da ita"

"Ai shi nace maka Bashir idan kaga zaka yi wani abu ka yi kabar jirana, karka sake min maganarta, ni ba abin da ya dameni da ita" katse wayar Abdallah yayi batare da ya jira cewar Bashir ba, Bashir ma wayar ya kalla sannan ya shiga cikin gidan cike da bacin rai.

Falo ya zauna tare da kwalawa Nur kira, nan danan ta fito jikinta a sanyaye, gefenshi ya nuna mata ta zauna sannan yace, "Kinsan mai nake so dake?" Kai Nur ta girgiza alamar a'a, "Karki kara yadda ya miki magana ki amsa, ke waima a ina kuke haduwa ?" Cikin kwalkwal da Ido Nur tace "Idan naje gidan biyawa Zainab makaranta..." Tun kan ta rufe baki yace karki kara biya mata makarantar, idan kuma ya tareki a hanya yayi miki mgn ki gaya mini, zanci ubanshi, wa yake kulawa duk cikin unguwarnan, zan tara mishi jama'a!" Yadda ya gada murya wannan lokacin yasa Mamy fitowa tana raba Ido tare da fadin "Lafiya kuwa Bashir?" Mikewa yayi a fusace yana cewa "Lafiya lau Mamy" Ficewa yayi dan haka Mamy ta maido da kallonta ga Nur dake hawaye tace "Mene ne ke faruwa" itama mikewa ta yi cike da rashin gaskiya tace "Bakomai" Daki ta shige dan haka Mamy ta tabe bakinta ta wuce abinta.

Koda Nur ta koma daki rufda ciki tayi tana hawaye sosai take jinta cikin damuwa, haka ta wuni babu walwala, bayan sun yi Shirin kwanciya Bilkisu ta dubi Nur tace "Wai ke baxaki saki jikinki bane, kodai kina son mutumin ne? Jin wannan tambayan yasa Nur ta tashi zaune, tare da cewa, Ni ba sonshi nake ba, yadda naga yaya Bashir ya tafi cikin fushi ne abin ke damuna,

Kuma nasan halinshi komai yana iya yi"
Kallonta Bilikisu ta yi soi sannan tace, "Karki kara bari yaji Koda ace ya miki magana karki gaya a gida, domin hakan zai iya haifar da rigima, na lura Bashir yafi Abdallah zafi, Wai dan Allah in tambayeki mana?" Dagowa Nur ta yi ta kalli Bilkisu sannan tace "Ina jinki."
"Wai da Yaya Bashir da Abdallah waye Babba?"
Cikin sauri Nur tace "Yaya Abdallah ne Babba kinga kusan kansu daya ne ko?"
"Eh, kansu daya, Bashir ma yafi Abdallah kiba kadan, amman shi Bashir Baffah ne Babanshi ko?"
Yar dariya Nur ta yi sannan tace "Eh ai dukkanmu Baffah ne Babanmu."
"Bangane ba Nur, karki kara sani cikin rudu, Bashir ne dai d'an Baffah ko?"
Wannan karon yar dariya Nur ta yi sannan tace "Wai ke baki sani ba da gaske? Yaya Bashir fa dan Mamy ne, kannin Yaya Abdallah ne duk su biyun Mamy ta haifesu."
Cike da mamiki Bilkisu tace "Ikon Allah, ni na dauka Umma ce maman Yaya Bashir ai"
"A'a umma yarta daya mace ce, da kadan ta girme ni, kuma ta rasu"
"Allah sarki, yanzun shi Baffah bashi da yara kenan shiyasa Bashir yake zaune agidan?"
Daga kai Nur ta yi tare da cewa "Ni daya ce yarshi yanxun." Wanni irin kallo Bilkisu tai wa Nur tare da cewa "Waike ma ba Mamy bace ta haifeki?"
"Mamatace, Amma ba ita ta haifeni ba, Yaya Abdallah be gaya miki ba?" Ciki da mamaki Bilkisu tace "A'a, nasha tambayanshi sai yace min Mamy ce ta haifeki ke dashi uwa daya uba daya."
Jimmm, Nur ta yi, zuwa can tace Ummy ce ta haifini, amman inajin Mamy sosai a zuciyata domin da ita na saba, na dade ban yadda wai Ummy bace ta haifeni, sabo da nafi samun kuwalawa da nuna kyauna daga Mamy". Cike da Mamaki Bilisu ta sake cewa "Ummy maman su Jamil kenan ko?" Da kai Nur tabawa Bilkisu amsa yayin da ta sake cewa "To Jamil da Jamal ma yaran Baffane kenan?"
"A'a bayan ta rabo da babansu ta auri Baffah da suka rabo Kuma ta sake komawa wurin babansu Yaya Jamal" Wannan karon ma cike da Mamaki Bilkisu tace "Na gane, kenan ke tunda ta fita ta barki wurin Mamy"
"Eh Ni dai na taso naganni wurin Mamy, amman dafari wurin Umma ta barni, soyayyar da Mamy ke min yasa ta daukoni ta rike tun a lokacin, dan haka yanzun na saba da ita fiya da kowa, domin tana nuna min soyayyar da bata nunawa yaranta na cikinta, tun tasowanta bazan iya cewa ga banbaci daya da ta nuna min ba, da ita da danginta sun rukeni kamar yadda zasu rike d'an daMamy ta haifa, sau daya Maman Mamy Kaka ta taba nuna min banbanci, Kuma akan Yaya Abdallah ne.
Dan Murmushi Bilikisu ta yi sannan tace "Ma dai kula keda yayan Abdallah nan naku bakwa shiri, wai mai yasa?"
"Bakomai, kinsanshi da son girma, Ni kuma na cika shishshige da yawan magana wannan yasa bama shiri sam"
Fashewa Bilkisu ta yi da dariya tare da cewa "Yanzun dan wannan yake jin haushinki, dariya ta cigaba da yi ganin haka Nur ma ta danyi dariya, yadda Bilkisu ke dariya tare da ceawa aiko saina shirya ku yasata kwarewa, nan ta shiga tari tare da hawaye, sannu Nur ke mata zuwa can ta tashi ta shiga bayi, amai taita kwarawa ganin tarin yaki tsayawa Nur taje ta Kira su Mamy, bayan zuwan su Mamy aka samu tarin ya tsaya, Aunty ta wanke mata fuska suka fito, nan Nur

ta basu labarin dariya take ta kware, sannu sukaita mata bayan tarin ya lafa suka fice adakin, tun daga lokacin Blikisu ta kwanta ta rufa, rawan sanyi taitayi zuwa can Kuma ta mike a guje ta koma bayin, amai Nur taji na yi dan haka tabi bayanta, kafin gari ya waye Saida ta yi amai sau biyar, dan haka Basu yi baccin kirkiba, da safe Nur na kwance taji Bilkisu na waya da Abdallah, tana gaya mishi amanta shidda cikin dare, sun dade suna waya daga baya suka yi sallama, Nur ko Shirin islamiyya ta yi sannan  ta karbo abin Kari, bayan sun karya ta wuce makaranta, misalin sha daya na safe ta taso, abakin makarantar taga Zainab tsaye sanye da hijjabi, karasawa wajenta tayi cikin  waige-waige, bayan ta tabbatar babu Yaya Bsmashir a kusa ta karasa tare da cewa "Daga ina, lafiya?"

"Daga asibiti nake Nur" Zainab ta fada cikin yanayin dake nuna tana cikin damuwa" waye babu lafiya?

"Poul ne, Nur a kwance kawai yake tun jiya baya iya cewa komai, kuma baya cin abinci" jimmm Nur ta yi sannan ta fara tafiya tare da cewa "Allah ya bashi lafiya" Ahankali Zainab ta sake cewa "Nur dan Allah kizo muje ki gaidashi nasan zaiji dadi"

"Tabb wallahi bazani  ba Zainab, bari kiji a gida ko ke an hanani magana dake bare kuma shi, gidan kuma an hanani shi shiga, Yaya Bashir din mu yace idan ya sake min maga sai kowa yajisu, sauri Nur ta Kara tana cewa "Ki tafi karya a gammu tare" A wurin Zainab ta tsaya cikin sanyin jiki sosai, har Nur tai nisa tana tsaye a wurin.

Bayan Nur ta Isa gida wannan karon ma cikin barko ta samu Bilkisu da alama jikin ya matsa mata har yanzun, da rana koda Nur ta amso abinci cewa ta yi bataci, abincin Nur ta fara ci da nufi taci ta barwa Bilkisu nata. Yadda Nur ke cakalar abincin yasa Bilkisu binta da kallo, gani ta yi ta kasa cin abincin ta tsurawa wuri daya Ido, dan haka tace "Nur!" Azabure Nur ta kalli Bilkisu tare da amsawa, "Tunanin me kike haka?" Bilkisu ta sake tambaya, babu komai Nur ta fada, sannan tacigaba da cin abincin, saidai Bilkusu ta lura Nur na cikin damuwa har dare haka Nur take, saita tsurawa wuri daya ido, abincinsu na dare kuwa cikinsu babu wadda ya taba, domin ita kanta Bilkisu yadda ta kwana amai shekaranjiya yauma hakan ce, washegari da safe Bilkisu ta kalli Nur tace "Ikon Allah, jiya cikinmu babu wadda yaci abinci, ni dai nasan lalurarace, tun kwarewan da na yi bandawo daidai ba, ke kuwa wani abu ke damunki Kuma kin kasa Gaya min, dagowa Nur ta yi ta kalli Aunty sannan tace, Ni fa ba abin da ke damuna, kawai jiya ne Zainab tace min Poul yana asibiti wai bashi da lafiya, bansan maiyasaba abin ya tsaya min a zuciya ba, na kasa kawar da tunanin araina hakanan sai naga Ina tuna fuskarshi"

"Tabb, kice kin kamo yariya, ashe kina son shi?" Bilkisu ta fada cike da Mamaki "A'a ba so bane, ko tausayinshi banayi, amman da gaski daga jiya zuwa yau Ina tuna fuskarshi."

"Hmmm Yariya ki zubar da makamanki ki nema mafita, kin kamo, mun yi waya da Abdallah yace "Bashir zaizo ya kaini asibiti, ki shirya daga can sai mu biya mu duba Poul din." Zaro Ido Nur ta yi tare da cewa "Kina son ya Bashir ya karyani kenan bazani ba."

"Shikenan" Bilkisu ta fada tana bin Nur da kallo, itako Nur tun da Bilkusu ta yi mgnr duba Poul zuciyarta ta fara nutsuwa, dan haka zuwa can tace "Aunty Bilikisu, amma sai dai idan bada Yaya Bashir zamu ba" Murmushi Bilikisu tayi tana daga kwance sannan tace "To ya kike ganin zamu yi mu zille mishi, ni kaina bason zuwa asibitin nake ba, Wai su Mamy ne suka matsa mishi akaini asibiti, wai sunce mishi ciki gareni." Yar dariya Nur ta yi tare da cewa ai gara adubaki aman yayi yawa kuma tun daga ranar baki kara cin wani abincin kirki ba, da gaskeyarsu kila na kusa samun yaro"

Yar dariya Bilikisu tayi tare da cewa, "Magani dai zasu bani, amma ni banda ciki, indai ba ana sha a ruwa ba"

Wannan karon ma dariya Nur ta yi tare da cewa Ni dai ba ruwana, wannan maganar manya ce,

"Kema babbace Nur, to yanzun ya kike ganin zakuyi mu zilewa Yaya Bashir din?"

Aunty kwanciya zakiyi ida yazo yaga baki shirya ba zai bamu kudin mota yace idan mun shirya mu wuce."

Cike da murmushina Bilkusu tace to haka za'ayi indai hakan zai Samar miki da kwanciyar hankali.

CIWON YA MACE

By

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 42-43

Murmushi Nur ta yi batare da ta sani ba, duk da cewa ta juyawa Bilkisu baya amma ta gane Nur murmushi take, dan haka ta shiga tunanin yadda al'amuran zasu kasance domin da alama Nur tana son Poul Bata kula zuciyarta ne sabo da ganin bazai yuwuba. Zuwa can Bilkisu ta ji tsayuwan mota, dan haka ta kalli Nur adaidai lokacin da Nur take cewa "Aunty rufe Ido gashi nan" Batare Da Bilkisu tace komaiba ta rufe idonta, Waigowa Nur ta yi taga idon Bilkisu a rufe, dan haka tai saurin shigewa bayi, tana turo kofar r Abdallah na buga kofar tare da Sallama a bakinshi, buguwa yayi tayi har ya gaji ya wuce, sannan Nur ta fito ta nufa kofar afalo, samunshi ta yi zaune afalon suna gaisawa dasu Mamy, bayan sun gaisa tace "Yaya ina bayine" Cikin sakin fuska yace "Nayi tunanin ma bakwa dakinne, Ina Aunty tamu ta shirya dai ko?" Karyar da kai Nur ta yi sannan tace "Bata tashiba in je in tasota?, Cike da mamaki yace "Kar dai Abdallah be sanar mata da maganar zuwa asibitin ba"

"Ya gaya mata, harma tace zan rakata, in tasota ta yi wanka?" Agogon dake daure a kan hannunsa ya kalla, sannan yace "Yanzun har saina jirata ta yi wanka? Zanyi latti ai" Mikewa yayi tare da saka hannu cikin aljihu ya ciro kudi ya mikawa Nur tare da cewa "Ki tasheta, in kunshirya sai ku wuce, amma kuna isa kimin waya, zan hadaku da likitan dazai dubata."

Cike da gamsuwa Nur tace "To" Saida ya fice sannan ta koma daki, inda ta samu Bilkisu ta gama shiryawa, dole suka dan tsaya suka bata lokaci sannan suka fito suka wuce, kamar yadda Bashir ya ce haka suka yi, bayan an gama mata gwajegwajen da za'a mata aka sallame su, Har zasu fita Bilkisu tacewa likitan "Ba wani magani da zaka rubuta mini?" Dagowa yayi ya kalleta sannan yace "Bashir zai taho dashi" Cike da gamsuwa suka fice, sannan suka wuce asibitin da Poul ke kwance.

Duk su biyun sanye suke cikin babban hijjabi har kasa, saidai ita Bilkusu tasa jibgigiyar rigar sanyi ta ciki, dan haka tayi katuwa, number Zainab tasa a wayar Bilkisu ta kira, bayan ta dauka ta sanar da ita gata a sibitin, nan danan kuwa Zainab ta fito cike da fara'a, Hannun Nur ta rike yayin da Nur Kuma tai saurin roko hannun Bilkisu duk da cewa bata jin karfin jikinta a haka suka

tafi, Mamma ce kadai a dakin, tana Zaune gefen Poul tana mishi fifita, ganin shigowan su Nur yasata dago tana musu sannu, Zainab ce tabawa Bilkisu kujerar da ta tashi, ita da Nur Kuma suka tsaya a tsaye, ciki da fara'a Zainab kecewa "Mamma ki gaya mishi ga Nur" kallon Mamma Nur ta yi, itama tana sanye da hijjabi ga carbi nade a hannunta,  sunkuyar da kai tana mamakin ganin mamma cikin damuwa, kenan duk da Wulakancin da Poul din yake mata tana sonshi a haka yanzun, muryan Mamma taji tace "Poul!" Batare da ya bude baki ba ya amsa, dan haka ta sake cewa "Ga Nur tazo dubaka" Cikin Sauri ya bude idon tare da rarraba su, zuwa can idonshi ya sauka akanta, tana tsaye ta dafa kujeran da aunty ke Kai, gaidashi Bilikisu ta yi ya dago mata hannu, Daker Nur ta iya yi mishi ya jiki, sannan ta sunkuyar da kanta kasa, nan Mamma ta fara basu labarin ciwon sh,i inda ta alakanta abin da rashin cin abinci ne, shiko Poul tun daga lokacin be sake rufe Ido ba, lokaci bayan lokaci Yana kallon Inda Nur take dan haka ta kasa sakin jiki a wurin, domin gani take ya hanata sakat da kallonshi da baya karewa, Zainab na Murmushi tamai ta yin cin abinci yace a'a. Shiru wurin yayi zuwa can Zainab ta nufa kofar fita tare da Kiran Mamma suka fice tare, ganin haka Bilkisu ma ta mike tare da cewa Nur "In kin gama ina waje kiyi sauri Amma." Kamar Jira Poul yake Yana ganin fitan Blikisu yayi ajiyan zuciya tare da waigowa ya kalleta, har yanzun tana rike da saman kujeran da aunty ke kai. Hannun sa ya miko mata tare da cewa "Rike ni in tashi" Yadda take haka take har yanzu bata bata motsaba, dan haka ya kara miko hannun tare da cewa "Dan Allah fa!"  Wannan karon dagowa ta yi ta kalleshi sannan ta sake sunkuyar da kanta kasa, ganin haka ya sa ya maida hannunshi tare da cewa "Washh" sannan ya dubeta yace "Haram ne ko? Babu kyau?"  Batare da ta dagoba ta daga kanta alamar eh, dan haka yayi murmushi sannan yace "Tam idan Helen ta dawo zata dagani" Wannan karon yi tayi kamar batajiba, zuwa can taji ya sake cewa "Ita ta gaya miki banda lafiya?" Wannan karon ma dai kai ta daga, dan haka ya sake yin mirmushi sannan yace "Ta gaya min abin da yayanki yace, amman yanzun ansan kinzo?" Bata saba karyaba dan haka ta girgiza kai alamar a'a, ajiyan zuciya yayi sannan yace "Na gode" Shiru suka sake yi zuwa can yace "Anjima in zakiyi waya dani? in kira number gidanku da wayar Helen? Tunda ke nace ki kirani kin ki" Can kasa makoshi tace "Wacece Helen?" Lumshe Ido yayi duk da cewa can kasa tayi maganar amman ya ji me tace sabo da Yana kallon bakinta, dan haka yace "Na manta ta canza suna ko? meye sunan ma?" Wannan karon kawar da kai Nur ta yi sannan tace "Zainab"  jinjina kai yayi sannan yace 'Baki amsa ba min tambayar da nayi mikiba, idan na Kira zakiyi magana dani?" Tsintan kanta ta yi da daga Kai, Dan haka ya lumshe Ido tare da cewa "Na gode,  kuje tunda kince ba'asan kinzoba, waccen wacece kuke tare?" Kawar dakai Nur ta yi sannan tace "Matar Yaya na ne0"
"Bashir?" Ya sake jeho mata tambayan, kaita girgiza tare da mamaki ta Yaya aka yi yasan sunan Bashir, bata rufe bakiba yace "Wadda aka yi baki kwanaki Abdallah ko?" Kai ta daga har yanzun da mamaki akan fuskarta, ganin wurin ya sake yin shiru ta juya tare da cewa "Allah ya sauwake" Saidai harta fita bataji ya amasa.
  Tare dasu Mamma ta samu aunty Bilkisu, sallama suka yi suka wuce, bayan sun dawo gidama Nur kadai taci abinci, Bilkisu ko kudundunewa tayi sabo da sanyin Dake damunta, Nur ko ta kasa cire fuskar Poul a zuciyarta, tun da ta dawo tunashi take a lokacin da yake miko mata hannu. Misalin 08:00pm Bashir yazo gidan, dan haka Nur tanajin sallaman sa ta fice, acikin dakin Mamy ta aameshi suna gaisawa da Mamy, zama ta yi bayan sun gama gaisawa da Mamy ya juya ya kalli Nur tare da cewa "Ya mai jikin?"

"Da sauki" Nur ta fada alokacin da Mamy ke cewa "Aikuwa ita za'a tambaya mai jiki, tunda sunce kwana take amai, ko dai yau zata koma dakin Auntyn ku ne?" Cikin Sauri Nur tace "A'a gaskiya, idan Kuma hakane saidai mu koma tare." Mamy ce tace "Ai saikuje taren, acan din zaifi, dan wani lokacin kila bazaki tashiba bare ko taimaketa."

Bashir ko tun da Nur tai maganar yabita da kallon mamaki tare da cewa, "Lallai Nur kina yaudaran kanki, wato bazata tafi ta barkiba, yanzun idan mijinta ya dawo fa?" Jimmm Nur ta yi zuwa can ta dago tace "Dama Abba yace su zauna anan"

Wannan karon dariya Bashir yayi adaidai lokacin da Aunty ta shigo, ganin Bashir nata kyalkyata dariya tace "Bashir ya samu mugunta kenan?" Mamy ce tace "Shi da Nur ne, abun da ya faru ta gaya mata itama dariya ta yi tare da cewa ai Nur babu komai cikin kanta sai kuruciya, lokaci kadan-kadan take da hankali, ai ranar da ya dawo ko kwana daya bazai karaba zai dauki matarshi, sai kinga yadda ya fitineni shekaranjiya da daddare, tsakar dare fa wai ya kirata bata dagaba" Bashir da Nur ne suka yi dariya yayin da Nur ta karashe dariyar da cewa "Allah yasa ya dade acan, walllahi gidan yanxun yafi Dadi" Itako Mamy kawar da kanta ta yi tare da cewa Bashir "Ka amso maganin dai ko? Sunce likitan yace Kai zaka taho dashi." Ledan dake gabanshi ya jawo ya mikawa Aunty, yayin da ta shiga dubawa, tana duba maganin ta dago cike da murmushi tace "Ina sakamakon to?, Hannun yasa a aljihu ya ciro takardar ya mikawa Aunty, budewa ta yi tare da cewa "Ma sha Allah, Alhamdulillah, ai ni dama nacewa mijinta cike gareta, yana min musu" Murmushin Bashir yayi tare da kawar da kai, itama Mamy godiya tawa Allah afili kuwa cewa ta yi "Allah ya rabasu lafiya, sannan ta mike ta ta fita adakin. Itako Nur sunkuyar da kanta ta yi fuskarta cike da murmushi, acikin zuciyarta take cewa "Lallai Aunty Bilkisu ta iya wayau, hiranta da kawarta Madina ne ya dawo mata, zuwa can ta yi dariya tare da mikewa, tana kokarin fita Bashir yace "Aunty ki bata maganin ta kaimata, ko wanni akwai yadda za'asha a jiki, laden aunty ta mikawa Nur har ta kusa kofa Aunty ta sake kiran Nur, takardan dake hannunta ta mika mata tare da cewa "Har takardan ma kai mata, yaran zamani kila har toho zata yi ta nuna mishi" dariya Nur ta yi sannan ta fice a dakin ko da Nur ta kaiwa Bilkisu tashi ta yi tasha magungunan sannan ta dauki takardan ta aje gefenta, kafin wani lokacin bacci ya dauketa, Nur ko tana ganin Bilikisu tayi bacci ta dauki wayarta sabo da yawan kallon Number Poul da take jikin katinsa tuni ta haddace number, bayan ta saka Number kasa dannawa ta yi domin wata zuciyar sosai take kwabarta, zuwa can ta tsincikanta da dannawa, saidai ta kasa sawa a kunnenta, muryansa tajiyo duk da cewa wayar na nesa da kunnenta, Jin yadda yake Kiran sunanta yasa ta nufa kunnenta da wayar, ji ta yi yana cewa "Nur bakya jina ne?" Can kasan makoshi tace "Ina ji" Ajiyan zuciya yayi mai karfi sannan yace "Na gode da kika kirani, tun dazon nake dakon kiranki, domin na kasa bacci sam, ni kadai nasan irin radadin da nake ji azuciyata, awannan karon ji tayi kalmar Bata mata dadiba, Wai zuciyarshi na mishi radadi, tsintan kanta ta yi da cewa "Dama zuciyar ce ke ciwo?" Lumshe Ido Poul yayi sannan yace "I ta tafi komai damuna Nur" juyawa ta yi ta kalli Bilkisu Dake bacci sannan tace "To asibitin baka gaya musu bane ai da sun baka magani" Ajiyan zuciya yayi sannan yace "Basu da maganin shi Nur, na riga na gama yankewa kaina hukunci, babu wani magani da zaiyi tasiri ajikina, domin kunar da zuciyata take min kece kadai maganinta, na tabbatar da hakanne bayan ganin ki da na yi dazon, tun daga lokacin naji na samu lafiya, yanzun haka Ina gida tun dazon nake kallon wayar, kiranki kawai nake jira, na gane kece maganin ciwona.

Wannan karon Nur batace komaiba, bayan tsawon lokaci yace "Bakice komaiba?" Can kasan

makoshi tace "Ai Gashi nakira." Cike da murmushi yace "Na gode, amman kinsan menene nakosa? Burina inga kinzama tawa, kuma jikina na bani hankalina bazai taba kwanciyaba sainaga na mallakeki, bana yin sekon daya batare da na tunaki ba, Nur kina ganin idan nazo gidanku za'abani auren ki?

Shiru ta yi batace komaiba, domin gabanta faduwa yake sosai, "Nur kinyi shiru bakice komaiba" Tsawon lokaci suka dauka batare da yaji tace kalaba, dan haka ya canza tambayan da cewa, "Nur in tambaye ki?" Can kasa-kasa tace "Umm" Ajiyan zuciya yayi sannan yace "Kina so na?" Shiru yaji tsawon lokaci, zuwa can Kuma yaji kamar tana kuka, dan haka yace "Kuka kike yi?" Wani abu Nur ta hadiye mai zafi awuyanta tare da share hawayen da ya fara zubo mata, Bayan shiru na wasu lokaci yace, "Gobe zanzo wurin Babanki kamar yadda kikace abaya..."

Katseshi Nur ta yi da cewa "Karkazo dan Allah"

Saboda me? Ina ce wancen ranar kece kikace min inje wurin Baban ki?"

"Yanzun nasan bazai yadda, kuma Yaya Bashir yamin gargadi sosai, bazasu yadda ba nasani."

Shiru yayi tsayon lokaci, zuwa can yace "Inda ace ni musumine kina gannin zasu amince su bani ke?"

Eh Nur ta fada a hankali, dan haka yace shikenan, ki kwanta kiyi bacci karki damu kinji?"

Ahankali ta amsa da "To" Jin yana Shirin kashe wayar tai saurin cewa "Karka kira wannan wayar na matan Yaya nane." Murmushi yayi tare da cewa "Bazan kiraba ai, amma dan Allah gobe ma ki kirani" Amsawa tayi sannan ta kashe wayar. Washegari tun da asuba Bilkisu ta fita neman abincin sabanin da da bata iya cin komai. Sannin lalurarta yasa aunty fitowa ta dama mata kunnum tsaniya, nan falon ta zauna tasha tai gyatsa, sannan ta iya yin sallah, da rana iyayen Aunty Bilkisu sukazo gidan duba jikinta, sosai tai murna da zuwan su, lokacin da zasu tafi gaba daya su suka fito rakasu har bakin mota, bayan sun zauna a motar ne kishiyar Maman Bilkisu tacewa Bilikisu "Toh Bilki ki dinga lura da cin abinci, Allah ya raba lafiya" Jimmm, Biliku ta yi kafin tace To kawai sannan tai saurin juyawa cikin gidan kamar zata yi kuka, Mamy, Aunty Saratu da Nur kuwa a tare suka dawo cikin gida, afalo Nur tabar su Mamy ta nufu daki, tana shiga ta samun Bilkisu ta yi zaune a bakin gado, kwalla cike daf da idonta, yayin da takardan da ta kawo mata jiya yake rike a hannunta, tsaye Nur ta yi tana kallonta, ganin kafufuwan Nur yasa Bilkisu dagowa ta kallli Nur a daidai lokacin da hawayen da suka cika idonta suka gangaro zuwa kumatunta, hannu tasa ta share sannan ta mike tsaye tare da cukurkude dakardan tana ya mutsata cikin hannunta, cikin yanayin dake nuna tana cikin tashin hankali...

CIWON 'YA MACE

By

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 44-45

Kallo Nur ta bita dashi cike da Mamaki, yanzu ta shigo cikin gidan tana murnan zuwan iyayenta,

ko mene ne yasata shiga cikin damuwa Kuma, karasowa Nur ta yi bakin gadon ta zauna, sannan ta sake kallon Bilkisu da har yanzun take share hawaye, wani tunani ne ya fado amta arai, dan haka ta kalli Bilkisu tace, "Aunty dan kinga 'yan gida kike kuka?" Dariya tasoyi Amman idonta na sauka akan takardan take hannun Bilkisu saita hade fuskar acikin zuciyarta tace, "Kamar Aunty Bilkisu nada damuwa da takardan nan, me yasa take matseta cikin hannunta?" Ganin babu mai Bata amsa ta mike tare da cewa "Aunty Bilkisu wai mene ne? batakai ga Bata amsa ba wayarta tai kara, saurin kallon wayar Bilkisu tayi sannan ta amsa kiran, daga yanayin amsa da take badawa Nur ta gane da Yaya Abdallah take wayar, bayan amsa ya jikin da ya mata sukaci gaba da hira, murmushi Nur taga ta yi kadan, dan haka ta fice domin ta bata wuri ta sake da mijinta. Tun daga wannan ranar Nur ta saba da waya da Poul, bayan Bilikisu tagama wayar da Abdallah ko wanne dare Nur zata Kira Poul susha hira, sosai Nur ke sakewa da Bilkisu bata boye mata komai, duk da cewa tun da Bilikisu ta samu cikin ta rage walwala, Mamy da aunty kuwa sai abin da Bilikisu keso ake dafawa a gidan, sosai suke bata kulawa, rashin walwalan Bilkusu be damu Nur sosai ba, domin tanaji ana cewa masu cikin sai a hankali dan haka idan taga ta kwanta ta yi shiru saidai ta dauki wayarta ta kira Poul, sosai suka saba, duk da cewa bata tunanin auren zai iya yuwa tsakanin su.

BAYAN WATA BIYAR

Tuni su Nur suka kammala jarabawa har sakamakon ya fito, dan haka Abba ya fara mata ciko cikon makarantar koyon aikin jinya kamar yadda take so, a yanzu burin Abba be wuce yaga ta fara zuwa makarantar ba, sabo da yanzu ya yadda da nutsuwarta, kuma ya tabbatar eh lallai karatun take so ganin bata taba kawo wani gida da sunan saurayiba, haka kuma bata da waya hakan be taba damunta ba, a yanzun islmiya kawai take zuwa, ita ko Bilikisu cikin ta ya fito sosai yayi girma, sai dai har yanzun bata da walwala ko waya suke da Abdallah hiran tasha banban da ta da.

*****

"Na rasa dalilin ki na kin yiwa Abdallah magana ya turo kudi yariyar nan ta fara zuwa awo, abin da fa baka son a maka karkawa dan wani, yanzun in da yarmu ce ai bazamu so ace ciki har yana dhirin shiga wata na takwas ba batare da an san lafiyarsa ba" Cikin rashin walwala Aunty Saratu tace, "Amman na ce miki kiyiwa Bashir magana ai yazo ya kaita, na mishi magana yace wai mijinta bai sanar dashiba dan haka bazashiba, in da kece kikamai magana ai bazai baki wannan amsan ba"

Wanni irin kallo Mamy taiwa Aunty sannan tace, "Ai ni bazance ya kaitaba haka kurumba, dole sai an bashi kudi tun da ba hidimarsa bace, ai be dace kawai ace yayi hidimar da ba tashiba, ko Abban su da nace ko zai bada cewa yayi yayi bashi da kudi sabo da yayi hidimar makarantar Nur bashi"

"To a yiwa Baffa magana mana" Aunty fada tana kallon Mamy, saida Mamy ta karewa Aunty kallo sannan tace, "Ikon Allah, to waishi Abdallah cewa yayi bashi da kudinne? Nifa banson iskanci, zan kirashi naci mishi mutunci wallahi"

"A'a Karki kirashi, ki bari zan kirashi" Aunty ta fada tare da mikewa ta nufi daki, Nur dake gafe Mamy tabi da kallo, ganin inda take huci tace "Mamy kiyi hakuri" Batare da tace komaiba ta mike ta shige daki, dan haka itama Nur ta mike ta koma daki inda ta samu Bilikisu na waya da

Abdallah, juyowa ta yi domin ta basu waje, wannan karon tana fitowa dakin autny ta nufa, saidai tana shiga ta samu anuty tana kaiwa da kawowa adakin, ganin shigowan Nur tai saurin daukan wayarta ta danna sannan tasa a kunnenta, zuwa can ya sauke tare da fadin "Busy" Nur ce tace "Yaya Abdallah yana waya da Aunty Bilikisu" Waigowa Aunty Saratu ta yi domin sai a yanzun ta gane ashe afili tai maganar ba azuciya ba, zama Aunty ta yi yayin da yanayinta ke nuna tana cikin damuwa, zuwa can wayarta ta fara kara dan haka ta kalli Nur tare da cewa Nur bani waje zanyi waya, mikewa Nur ta yi ta fita tare da jawo mata kofar, haka kawai taji tana son sanin mai aunty zata ce da Abdallah, har tayi nisa da kofar ta dawo a hankali ta tsaya, yayin da ta jiyo ayunty na cewa "Abdallah kwanaki da nai maka magana naga kamar kana nuna bakasan Bilkisu nada ciki ba?" Kara kasa Kunne Nur ta yi zuwa can taji ta sake cewa "Eh mana, tun lokacin datai rashin lafiya nan" A'a dakata mana Abdallah abin ba tashin hankali bane yarintane, nima harda laifina danasani tun lokacin na gaya maka tunda Bashir suna dawowa ni ya bawa sakamakon..." Shiru ta sake yi tsayon lokaci, da alama katseta yayi, zuwa can tace "Innalilahi wa innalaihir raju'un, Abdallah ka rufa mana asiri, tsaya kaji, ai shine nace ka saurareni" daganan Nur Bata sake jin komai ba dan haka da saurin tabar wajen, afalon ta zauna tai ajiyan zuciya, nan danan taji wani irin tashin hankali ya dirar mata, bata gama dawowa cikin hankalinta ba taga wucewar Aunty arikice  zuwa dakin Mamy, wannan lokacin bata da kwarin bin bayanta dan haka ta mike ta nufi dakinsu, Bilikisu ta gani rike da waya sai Kara take Amma taki dauka, cike da damuwa Nur tace Aunty ana kiranki awaya"

Cikin wani irin yanayi tace "Bazan iya daukaba Nur, domin gabana faduwa yake haka kawai." Leka wayar Nur ta yi tare da fadin, "Yaya Abdallah ne fa?" "Eh na gani gabana faduwa yake Nur yanzu maka gama waya dashi" Bilkisu ta fada tare da kwantawa a gefen wayar idonta cike taf da hawaye.

Haka Abdallah yaita kiran wayar Bilikisu har sau Babu adadi taki dauka, kwanciya ta yi cike da damuwa, hakama Nur take kiyasta abin da ke shirin faruwa cikin zuciyarta, saidai tana korewa domin ko a mafarki batason hakan ya kasance, haka gidan ya wani Babu wani walwala, adaren ranar Aunty Saratu ta shigo dakin Nur, bayan sun mata sannu ta ce da Nur ta jirasu a waje zasuyi magana da Bilikisu, mikewa ta yi ta fita, sai bayan kusan awa guda sannan Aunty ta fito, lokacin da Nur ta koma dakin samun Bilikisu ta yi Cikin kuka sosai, dan haka ta zauna a takure, daren ranar cikinsu babu wadda ya runtsa, lokaci bayan lokaci Nur na jiyo ajiyan zuciyar da Bilkisu take yi, yayin da hakan ke jefa Nur cikin damuwa, tare da kara yin nisa da tunaninta dan haka bacci ya gagareta saidai ta juya ta kalli Bilkisu sannan ta hadiyi yawo saboda makogoronta dake bushewa, abin da take tunanin yana shirin faruwa take ayyanawa akanta dan haka damuwarta gaba yake karawa ba baya, washegari bayan Nur ta gama shirin islamiyya ta fito domin yiwa su Mamy sallama, babu kowa acikin gidan dan haka ta nufi falon Abba, tukafin ta ksa taji muryan Baffah na cewa, "To ai wata takwas kenan da auran, wannan kawai so yake ya jawo mana kananan maganganu, sai ya bari ta haihu kafin yace wani abu, ai yanzun dama cikin be isa haihuwaba ko?" Muryan Abba taji yace "To ai shi cewa yayi ma gaba daya be kusanceta ba"

"Innalilahi wa innalaihir raju'un" Baffa ya fada yayin da taji Muryan Yaya Bashir yana cewa "Ba yace sati biyu ya rage ya dawo ba, ni inaganin a bari ya dawo" Adaidai wannan lokacin Nur taji kamar motsi a bayanta, dan haka ta karasa tare da sallama, amsan sallama suka yi cikin sakin fuska har ta gaidasu ta yi musu sallama bataji an cigaba da maganar ba, bayan ta dawo

gidan ma shiru tajishi, Bilikisu kuwa cikin tsananin tashin hankali ta sameta, kuma tana kula har yamma Yaya Abdallah be Kira Bilikisu cikin waya ba kamar yadda suka saba, a daren ranar Nur na zaune adakinsu wayar Bilikisu ta dauka da Nufin Kiran Poul domin jiya Bata samu sunyi waya ba, number ta saka tana kokarin kira taji muryan Kaka kamar daga sama, cikin daga murya take cewa, "Ina take tazo ta tafi gidan iyayenta, bazamu dauki kazanta da ba namu ba, yau na tabbatar da mutanen gidan nan basa kyaunar Abdallah, yariyar tashigo gidanshi da ciki kuce Wai yayi shiru? To idan shi kun Isa dashi ni baku isa daniba" a firgice Aunty Bilkisu ta mike tsaye cikin tsananin rudewa, ganin haka Nur ma ta mike tare da ajiye wayar hannunta, tuna irin masifar  da Kaka tai mata kwanaki akan Abdallah yasa tai saurin nunawa Bilkisu bayi tace "Kisha Bilikisu" batai musuba ta shige ciki yayin da Nur ta kulle bayan ta cire key jikin kofar sannan ta koma gadon ta kwanta, batajimaba taji an turo kofar, Kaka ce su Mamy na bayanta suna Bata hakuri, Amman sai masifa take yi, neme nema ta fara adakin tare da cewa "Ina tantiriyar take?"

Cikn nuna halin ko in kula Nur tace "Bata muku sallama ba? Yanzun Babanta yazon ya dauketa, ajiyan zuciya Kaka tayi tare da cewa "Yafi masu su je ce su karata, ashe sunsan yarsu lalatacciya ce suka lika mishi, Allah ya Isa tsakaninmu dasu, wato badan Allah ya dubi Abdallah ba dan wani zamu ma bauta acikin gidan nan, yanzun sai ku kara tabbatar da cewa gemon nan nashi bana banza bane, juyawa tayi kansu Mamy ta rufesu da fada ta inda take shiga batanan take fitaba, sannan ta fice adakin tana cigaba da tsinewa Bilikisu da iyayenta,, bin bayanta Many ta yi, Itako Nur suna fita ta bude Bilikisu cikin matsancin damuwa take zubar da hawaye, wannan karon harda shashshekar kuka ahaka su Mamy suka dawo suka sameta, lallashin Bilkisu suka kayi tare da kara kwantar mata da hankali, suna nuna mata rikicin tsofa ke damun Kaka amman ta bari Abdallah ya dawo za'a samu mafita cikin sauki, saidai duk kokarinsu nason su kwantar mata da hankali be gamsar da Bilkisu ba domin ko bayan fitansu kuka taita yi, Nur ma tun fitan Kaka take share hawayen tausayin Bilikisu domin idan har Abdallah yace cikin ba banshi bane to na waye? Juyawa ta yi ta kalli Bilkisu dake matsancin kuka, sam bata ta rawan kai ko kadan, tunda Abdallah yabarta agidan kuwa za'a iya kirga fitan da ta taba yi Kuma duk inda zasu tare suke zuwa, bata da rawankai ga kirkin dake gareta, kuka Nur take tsawon lokaci, zuwa can ta saurara tare da kallon Bilikisu tace "Ki yi hakuri ki daina kuka"

Kara rushewa ta yi da kuka tare da cewa "Ta Yaya zan daina kuka Nur? Ina mai bakin cikin iyayena suji wannan mummunan labarin, ina rokon Allah ya dauki raina kafin muyi ido biyu dasu ina cikin wannan halin, Nur Babana, ina tausayin shi, bansan me zanyi ba, narasa in da zansaka raina Nur, bani da bakin da zan wanke kaina, amman ni ba yar isa bace, sadai ba abin da na sani da zan fada ya wankeni, Nur zo ki taba kirjina kiji yadda yake yi, Nur bayan bugawa da yake inajin kamar zaiyi tsalle ya fito."

Kara fashe Nur tayi da kuka, haka suka raba dare suna abu daya, kafin safe gaba daya idonsu yayi luhu luhu ita da Bilikisu gaba daya, ciwon Kai ya hana Nur zuwa makaranta, halin da Namy da Aunty suga Nur aciki be basu Mamaki ba, domin suma cikin damuwa suke,  tunda ga ranar abincima saidai adancishi fan dole acikin gidan, Nur ko har tafi Bilkisu ramewa sabo da ta saka damuwar a ranta duk da cewa Bilkisu Koda Yaushe cikin kuka take Nur kuwa tsabar tunane tunen da nemo mafita tasa a azuciya dan haka duk ta fige, a daddafe aka cika sati biyun da Abdallah yace zai dawo, be dawo a ranar ba sai Washegari da tsakar rana, Bashir ne ya daukoshi kasancewar gidan babu yara masu oyayoto basusan da shigowanshi ba Saida

sukajiyo Muryanshi shida Bashir afalo, mikewa Nur ta yi ta fara kokarin fitowa domin gani take Yana dawowa komai zai warware, tana fitowa suka yi Ido Biyu dashi Yana zaune yayi wani irin fari tare da tara kasumba fiye da baya, kananan kaya ne ajikinshi dan haka sosai taga ya canza, kallo daya ya mata ya kauda kai, gefen Yaya Bashir Nur ta Isa sannan tace "Sannu da zuwa Yaya Abdallah" kanshi ya juyar wani gefen batare daya amsa ba, har sau biyu Nur ta Kara mishi asannu da zuwa be amsa ba, dan haka ta juya ta koma daki, Mamy na lura dashi saidai damuwan dake gabanta ya dame wannan, dan haka batabi takai ba, abincishi yaci sannan suka fita tare da Bashir, Misalin 8 na dare yana kwance a dakinshi na gidan Mamy Abba ya kirashi cikin waya, bayan dauka yace yazo falo suna jiranshi, mikewa yayi ya fito anan ya cika da mamaki ganin falon cike da mutane ciki har da Baban Bilkisu da kanninsa, zama yayi akasa wannan karon jikinshi yayi sanyi sosai, Baffa ne yace "To Abdallah mun hadu ne anan dominku ku biyu kaida Matarka, ga iyayenka anan, ga nata, sabo da muna son mu tabbatar da adalci, tun kana can kace Bilkisu ta tafi gida mukuma munga hakan ba daidai bane, dan mun tambayeta tace ciki naka ne, to yanzun gata gaka ga Kuma iyayenta ga naka, kace ba naka bane; tace naka ne"

Sunkuyar da kai Abdallah yayi tsayon lokaci, zuwa can yayi gyaran murya cike da nutsuwa ya ce, "Baffa ina son zan mata tambaya daya zuwa biyu."

Gaba daya falon aka hada baki wajen fadin "Kana da damar yin hakan."

Juyawa yayi ya kallin Bilkisu yace, "Bilkisu har muka cika kwana shidda na kusance ki?"

CIWON 'YA MACE

By

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 46-47

Shiru Bilkisu ta yi ttsayon lokaci, kowa ita yake kallo, ganin haka mahaifinta daya tsura mata Ido acike da damuwa ya ce, "Ba magana ake miki ba?"

Wannan karon dago kai tayi ciki da hawaye tace "A'a" idonta a kasa ta yi maganar yayin da hawaye ke gangaro mata masu tsananin zafi.

Cike da bacin rai Abdallah ya ce "To mai yasa zakice cikin nawa ne? Bayan kinsan babu wani abu daya taba shiga tsakaninmu" Wannan karon Bilkisu bata iya cewa komaiba illa hawayen dake zubo mata, tsayon lokaci ta dauka tana kuka zuwa can Babanta yace "Bilkisu mai na miki kika min haka? Banji dadin ganin wannan ranarba sam, wannan ranar ita rana mafi kunar zuciya a tarihin rayuwata, da ganin wannan ranar gara ace gawarki nagani agabana, tir dake Bilkusu" Kareke maganar yayi tare da fahewa da kuka dan haka Bilkisu ta kara rushewa da kuka, Abban ne ya shiga bawa mahaifin Bilikisu hakuri sai dai be saurari Abba ba mikewa yayi ya fice cikin tsananin damuwa tare da nuna tsananin bacin rai, ganin haka kanin mahaifin Bilkisu yace "Shikenan sai ki tashi muje muje gida, tun da haka kika zaba, Abdallah tun yana can ya sake ki, kuma banga laifinshi ba" Mikewa yayi afusace dan haka itama Bilkisu ta yunkura ta mike cikin matsanancin kuka, adaidai wannan lokacin Nur dake labe ta fashe da kuka, waigawa kowa ke yi yayin da wasu ke cewa "Wa ke kuka?" Bashir ne ya mike tare da cewa

"Nur ce"  hanyar dakin ya nufa inda ya sameta zaune dirshen akasa sai kuka take, hannunta ya rike ya dagota tare da cewa "Mene ne haka Nur?" Kokarin rarrashinta yake tana gocewa dan haka ya fara janta zuwa falon adaidai lokacin da su Bilkisu ke fita cikin falon itama tana matsanancin kuka, kwacewa Nur ke yi tana kokarin bin su Bilkisu yayin da Bashir ke janta cikin buga ganin haka Abba dake kokarin bin bayan Mahaifin Bilkisu yace ya saketa, sakinta yayi tabi bayan Abba, har bakin motar suka Isa bayan Bilkisu ta shiga motar cikin matsancin kuka Nur ke daga mata hannu, saidai ita Bilkisu da Ido kawai take kallon Nur bata iya daga mata hannu ba barema tace mata wani abu, har motar ta wuce jajayen idon Bilkisu suna kan Nur, bayan motar ta wuce Abba ya kalli Nur sosai sannan ya ruko hannunta suka dawo gida, daf shi ya zaunar da ita tare da nuna alhininsa akan abun da ya faru sam beji dadiba, daga karshe ya juyo ya kalli Nur yace "Ke kuma ki kwantar da hankalin ki, Baban ta mutumin kirkine, dan haka wannan bazai zama yankewar alakarmu ba, kuma wannan ya ishe ki ishara, kin zabi karatun dan haka kiyi taka tsankan karki yadda da ruden samarin zamani bare su kaiki su baro,  yanzun Kinga koma waye ya cuceta, Gashi tana son auren yafi karfinta, Nur batace komaiba hawaye take sharewa har wannan lokacin, Mamy da aunty Saratu ne suka mike suka bar wurin cike da jimami, itana Nur sallamanta Abba yayi dan haka ta mike da nufin wucewa, wanni irin kallo ta ga Abdallah ya yi mata dan haka tamai kallon sama da kasa sannan ta wuce, Koda ta koma dakinta Rufda ciki ta yi tare da cigaba da kuka, tare da tuna yadda zata yi rashin Bilkisu adaren yau da sauran lokotan da batan iya adadin su ba, dan haka ta kara fashewa da kuka, bayan kusan minti talatin Bashir ya shiga dakin tsaye yayi akan Nur yana kallonta tsayon lokaci zuwa can yace, "Ke wai Nur Ina runkine acikin wannan mgnr da zaki zauna kina ta kuke koke? bata motsaba bare ta tanka dan haka ya sake cewa "Kowa a gidan nan beji dadin abin da ya faruba amman babu mai wannan koke koken saike kuma wama yaceiki kizo ki labe kiji abin da ke cewa?"

Wannan karon ma bata tankaba, dan haka ya shafa kanshi tare da cewa "Shikenan, kiyi hakuri ki tashi mu yi magana" Kareke maganar yayi tare da zama a gefenta Yana kokarin dagata tare da cewa "Idan zaman gidan zai miki babu dadi kizo muje gidanmu" Hawaye ya shiga share mata, kamar jira Nur ke yi ta shiga cewa, Yaya Bashir dan Allah ku bashi hakuri Aunty Bilkisu ta dawo gidan nan, wallahi natsatstsiya ce, Idan ma cikin ba nashi bane to wallahi ba iskanci ta yi ba" Dan ya tsanshi yasa akan lebenta tare da cewa karki kara shiga cikin wannan maganar, ai ko ciki daya kuka fito bakya shaidaitaba bare wadda kika santa wata takwas baya, kuma nasan kina da ilimi idon kine ya rufe kawai amman ko be saketa ba basu da aure" Yana maganar yana share mata hawaye ganin wani na sake zubowa yace "Ya isa haka mana Nur, ki daina kuka dan Allah"

"To Yaya dan Allah ka taimaka ta dawo nan ta zauna"

Girkizata yayi tare da cewa "Ke ki nutsu Nur kiji abin da zan gaya miki" Lafawa ta yi da kukan tare da binshi da Ido ganin haka ya shiga cewa, "Zamanta anan bazai yuwuba, amman duk ranar da kika son zuwa ki gaya min sai in kaiki, amman sai in kin kwantar da hankalinki idan kina koke koke kamar wadda akawa mutuwa bazan kaikiba" Hannu tasa tana share hawayen tare da cewa "Na Bari" Yauwa ko ke fa? Karki sake kuka kinji ko? da ga yau babu ruwanki acikin wannan maganar, Abdallah ne ya kawo Bilkisu gidan nan, idan bata sanadinsa ba da bamu santaba, kuma yanzun rabuwa ya shiga tsakaninsu, shakuyar da kukayi ita zata sa na kaiki wajenta, dan haka ko kinje babu ruwanki da tattauna abin da ya shafi wannan matsalar,

bare kice zaki shiga tsakiya, ina son ki sani Abdallah shine dan uwan ki ba Bilkisu ba" Ciki rashin fahimta Nur tace "To amman Yaya Bashir dan shine dan uwana kuma ai ba'aza hananin tausayinta ba"

"Idan Kinga zakiji kije ki ta ji, kukan ne be ishekiba, idan kikace haka zakiyi bazan goyi bayanki ba, ashe baki da adalci?"

Fashewa Nur ta sake yi da kuka tare da cewa "Me na yi to Yaya"

"In da kina da adalci ai Abdallah ya dace kiji tausayi ba matar ba, domin yanzu badan Allah ya kiyayeba data kawo mana dan wani cikin gida."

Cikin turo baki tace "Aunty Bilkisu ba yar iska bace Yaya Bashir." Cike da fada Bashir yace "Ok kina nufin Abdallah ne dan iskan kenan? Shiyasa daman yace kin harareshi."

Zaro Ido Nur ta yi tare da kallon Yaya Bashir tace "Ni? Yaushe?" Ni ban harareshi ba saidai idan tsarguwa yayi"

"Zakiga tsarguwa idan ya fasa miki baki, dan ko yanzu nina hanashi shigowa, kiyi hankali da kanki tun da yace shi ba ruwanshi dake kema ki kama kanki ko da wasa karki shiga tsakaninshi da Bilkisu"

"Shike nan, kada Allah yasa yayi ruwa dani, ni bazan sake kallon inda yake bama, shima ya daina kallon in da nake, shikenan kowa yayi harkar gabanshi" Wani irin irin kallo Bashir yawa Nur mai cike zallar mamaki sannan yace, Nur ashe baki da kunya"

"To Yaya Bashir nifa ya isheni, ina gaidashi baya amsawa, darajarshi da nake gani bana iya ganinshi batare dana gaidashi ba duk da cewa nasan bazai amsaba, sai an yi magana yace ba ruwanshi dani, baruwanshi da ni kuma ya kalleni har yaga Ina hararanshi? tun da Babu ruwanshi dani ai sai ya daina kallon Inda nake."

"Ni kike gayawa magana?"

Kuka Nur ta sake sawa tare da cewa, "Ai dama ba dama mutum ya fada abin dake zuciyarshi sai ace bashi da kunya, Duk abin da yake min hakuri nake yi yasha cemin nan ba gidan ubana bane ko yace sai na koma gidan ubana, in da bani da kunya ai saina rama zagin da yake min, amma ban taba tanka mishi ba sabo da ina ganin girmanshi" Sunkuyar dakai Nur tayi tare da turo baki bayan ta gama rattafuwa, dan haka Bashir ya jinjina kai tare da cewa, "To kici gaba da hakuri wata rana sai labari, sabo da ko ni bazanso ki dinga gaya min magana ba bare Kuma shi Abdallah, duk da cewa yanzu nasan har da fushin wannan kila hada kuma shine abin da bana so din kuma na tabbatar da cewa Kowa ma agidan nan bazaiso ace wannan abin ya kara haddasa kiyayya a tsakanin ku ba, tun da Abdallah ya nuna beson kina shiga cikin lamarinshi to ki bari." Ganin ta sunkuyar da kanta tana hawaye yace "Kina jina ko?" Kai ta daga alamar eh, ajiyan zuciya Bashir yayi sannan yayi mata sallama ya wuce" Daren ranar Nur Bata iya runtsawa ba, da safe tana kwance ta dinga jiyo hiransu Yaya Abdallah da Bashir afalo, bayan wani lokacin taji shiru, hakan ya tabbatar mata da sun fita, sai wurin sha daya ta karya, shima daker taci kadan, sanin damuwarta yasa ba wadda yayi mata maganar makaranta, har aka cika sati da faruwan abin, yauma kwance take adakinta cikin tunanin Bilkisu tare da nemo mafita domin burinta kawai taga Bilkisu ta dawo amatsayin matar Abdallah domin tuni take hango hotonsu da yaransu acikin zuciyarta tare da auno irin zumunci mai dadi wadda zasuyi tare da ita, zuwanta gidan ta fara mancewa da kewan 'yan uwa mata da bata dasu jinta take tamkar yar uwanta ta jini, dan haka burinta kawai taga Nur ta dawo gidan, tana cikin wanna tunanin taji an turo kofar, Abba ta gani cikin Babba riga da hula, yake ta yi tare da kokarin tashi zaune, Bakin

gadon Abba ya zauna tare da cewa "Haba Nur, mai yayi zafi haka? Sati daya kenan bansaki a idona ba, hakama Bashir da Abdallah sunce suma tun wancen ranar basu sake ganinkiba, Mamynki ma tace kin daina magana da kowa, abincima ba sosai kike ci ba" Wasa da hannu Nur take, yayin da Abba yaci gaba da cewa "Makaranta ma bakya zuwa ko?"

Wannan karon Kai ta daga alamar "Eh" Dan haka Abba yace "To kuncin ya isa haka, gobe asabar ki shirya kije makaranta" ta kardun dake hannunsa ya mika mata, tare da ceawa " Ga albishir na zo miki dashi, maganar makarantar ki ya kammala, i dan Allah ya kaimu ranar Monday zakije."

Fuskarta babu walwala ta amsa takardan hannun Abba tare da motsa bakinta, dan haka Abba yace "Ko kina da magana ne?"

Kai Nur ta daga da sauri dan haka Abba ya kureta da idon tare da cewa, "To Ina jinki?"

Motsi tai tayi da baki ta gaza furta komai, dan haka Abba ya sake cewa "Ina jinki."

"Abba baza iya canza min ba?"

Cike da rashin fahimta Abba yace "Ban fahimceki ba?" Wannan karon ma magana ta kasa har Saida Abba ya sake cewa "Ina jinki Nur?"

"Abba ina son na yi makarantar horas da lauyoyi domin na karanci shari'a yanzun nabar sha'awan jinya."

Wannan karon cike da bacin rai Abba ya kalli Nur sannan yace, "Amma Nur kina da matsala" shiru yayi tsayon lokaci yana bin yadda idonta ya cika da waye da kallo sannan yace "Me yasa tunanin ki be tsayawa da wuri daya? Saida na gama shan wahala sannan kice min bakya so Nur? Kinsan nawa na kashe akan neman makarantar nan, shike nan," Abba ya fada tare da fizagar tagardan a hannun Nur ya fice, Gannin haka Nur ta mike tare da cewa Abba ka yi hakuri to zamyi, ficewa yayi batare da ya saurareta. Da daddare Nur ce zaune adakinta tun da Abba ya fita dazon take cikin damuwa, agogo ta kalla karfe Tara, hakan ya tabbatar mata da an gama cin abinci a gidan, afili tace "Abba na fushi dani, tunda besa an kirani ba, Kuma har tara ba'ace inzo in daiki abinci ba" Mikewa ta yi da nufin zuwa ta bashi ha kuri, falonshi ta shiga shinkadai ta samu yana ta lissafi, yana ganinta ya dago cike da murmushi tare da cewa "Nur!"

Karasawa ta yi ta zauna tare da tace "Sannu Abba" Cikin sakin Fuska yace "Yauwa sannu Nur ya gidan"

"Lafiya lau Abba nazo ne na baka hakuri, kayi hakuri ranar Monday zanje makarantar."

Murmushi Abba yayi tare da cewa "Bakomai Nur karki damu, na fara maganar akan sabon zabin naki, matsalar dai ta kudi ce, amman na tambayi Abdallah be dai amsa ba amman yace gashinan zuwa."

Idon Nur cike da Kwallah tace Abba abarshi kawai zanyi wadda aka samu di"

"Hmmm, Nur matsalar ki bakya tsayawa wuri daya, yau kice wancen gibe kice wannan, amman duk da haka Ina da burin faranta miki, akwai akwai wani abu da iyaye suka dauramu akai, shi ne duk wani zabi na yaro in dai ba ya sabawa addini ba to karka hanashi kace lallai abin ka kake so shi za'ayi domin abin da yaro yake da sha'awa kai yafi maida hankali, fatana kawai wannan yazama zabinki na karshe" Idon Nur cike da Kwallah tace, "Na gode Abba, tunanin zancen Abba ta shiga yi Cikin zuciyarta tare da Jinjina irin kyaunar da Abba ke mata, hawaye taji ya zobo mata adaidai lokacin da Abdallah yayi sallama ya shigo, yana zama ya gaida Abba, sannan ya bude jakar dake hannunshi ya fito da bakar leda ya Isa gaban Abba ya aje tare da cewa "Abba gashi dari biyar kace ko?" Cike da fara Abba yace "Eh an samu kenan?"

"Eh Abba, idan kana son kidi kawai kace min idan Ina da kudi in kawo, ka daina ce min bashi"
Dagowa Abbba yayi ya kalleshi tare da cewa "To ajiya na baka?" Gyara zama Abdallah yayi sannan ya ce "Abba ni dai kyauta na baka ba bashi ba, godiya Abba yayi masa tare da saka mishi albarka, Hira sukaci gaba dayi Nur na sauraron su zuwa can Abba ya bude kudin ya cire wasu sannan ya turawa Abdallah ledar tare da cewa "Dauki wannan, idan Allah ya kaimu gobe da duku-duku ka kaiwa Alhaji Ibrahim." Dauka Abdallah yayi tare da cewa "Gidansa ko office?"
"Gidan sa dai, shiyasa nace da safe ai, duba can, ga takardu can ka dauko" In da Abba ya nuna masa ya nufa, daukowa yayi yayin da Abba yaci gaba da cewa, "Takardun Nur ne, ka hada da kudin ka bashi duk abin da ya dace yayi."
Cikin rashin fahimta Abdallah yace "Abba ba ance an samu makarantar nata ba, wannan Kuma na me ye to?"



"Kasan Nur da tunane-tunane, shari'a take son ta karanta yanzun kuma" Cikin sauri Abdallah ya juya ya kalli Nur sannan ya kalli takardun tare da kudin ya kada kai ya fice batare da yace komaiba.
Bayan fitan Abdallah Nur tawa Abba sallama ta fito, dakinta da koma, tun bayan da Bilkisu ta tafi gidan su sai yau Nur ta samu dan nutsuwa, sai dai har yanzu tausayin Bilikisu yana makale da zuciyarta, a gefe guda kuma a kawai tarin Haushin Abdallah azuciyarta, musamman da taga ko ajikinshi, be nuna damuwa ba, so da yawa takan kwatanta abin da kanta, domin har yanzun tana kewan Bilkisu, tare da tuna halayenta nagari, mai yasa shi Abdallah be nuna jimami ko kewanshi ba, wata zuciyar ce tace "Kila kuma yana yin kewan gabanmu ne baya nunawa" Share tunanin tayi sannan ta mike taje dakin Aunty, gani ta yi ta fara bacci dan haka ta dauki wayarta ta fito a dakin. Duk abin da ya zamar mata jiki kafin kwanciya ta yi, sannan ta rufe kofa ta kwanta tare da saka number Poul acikin wayar Aunty, tana fara ringing ya dauka tamkar mai jira, "Nur!" Poul ya fada a hankali, amsa ta yi kasa kasa "Lafiya kuwa kwana biyu? Nata jiran Kiran ki har nagaji na kasa hakuri na kiran layin da kike kirana dashi" Cikin lumshe Ido Nur tace "An dauka?"
"Eh, an dauka, amma ba ace komai ba, kira yafi sau goma, sannan wata ta dauka tace mai wayar bata da lafiya."
Jimmm Nur ta yi sannan tace "Mai ke damunta?"
"Haka dai akace bakwa, tare ne?"
"Eh tana gidan su"
"Mijinta ya dawo kenan?" Cikin wani irin yanayi Nur tace "Eh ya dawo, amma basa tare sun dan samu matsala." Sosai Poul ya nuna rashin jin dadinshi, sannan ya shiga fada mata halin da ya shiga da baya samun kiranta. Nur kuwa nuna mai ta yi bata da lafiya ne, dan haka ya tambayeta jiki, bayan ta amsa yayi ajiyan zuciya tare da cewa, "Ina son in yi wata magana

dake." Nur na daga kwance tace ina jinka" Kara jawo bargo yayi ya rufe jikinshi tare da cewa "Ina son in nuna kaina a matsayin wadda ya ke son auren ki a gidanku." Jimm, Nur ta yi zuwa can tace "Ai na ce maka gidan mu bazasu yadda ba" Cikin wani irin yanayi ya ce, "Kenan bazamu yi aure ba? Idan baza mu yi aure ba meye amfanin wayan da muke yi? Kullum zuciyata kara nisa take a son ki, na shirya in karbi musulunci a yanzun dan haka kawai dama nake jira daga gareki in zo wurin Abban ku." Wannan lokacin cike da damuwa Nur tace "To idan har ka shirya ka musulunta mai yasa zakaje wurin Abba tun yanzu, ai gara kaje kana musulmi."

Jmmm Poul yayi sannan yace "Haka ne, amman ina son insan ta bangarenki banda matsala ko?" Can kasan mokoshi Nur tace "Eh"

Ajiyan zuciya Poul yayi sannan yace "Shikenan amma banson aja lokaci, cikin kankanin lokaci nake son a yi komai a gama." Wannan lokacin cike da gamsu Nur tace "Haka ne" Domin burinta kawai ya musulunta din, har sunyi sallama zai kashe wayar tai saurin cewa "Wurin Malam Zubairu zakaje ko?"

"Wurin shi kike son naje?" Poul ya jefa mata tambayar, can kasan makoshi tace "Eh"

"To Zanje" Tsintan muryarta yayi ta sake cewa "To yaushe zaka je?"

"Yaushe ki ke son naje?"

"Gobe" Nur ta fada a hankali, "Shikenan karki damu, amma ki bani shawara akan sabon sunan da zan zaba?" Shiru Nur ta yi tsawon lokaci zuwa can tace " Kai baka da zabi ne?"

"Inadashi amman zanso inji naki ko yafi nawa dadi" Wannan karon ma shiru Nur ta sake yi alamar nazari take yi, zuwa can tace "Kana son suna Abubakar?"

"Eh, sunan yana da dadi Nur, mai zai hanani so idan har kina so?" Dan murmushi Nur ta yi sannan ta ce "To ka gaya min wadda ka ke so da?" Shima Poul Murmushi yayi sannan ya ce "Ni ina son suna Aliyu ne amman tun da kina son Abubakar din shima yayi" Lumshe Ido Nur ta yi tana maijin tsananin farinciki na lullabeta, zuciyarta fari kal tace "Zabinka suna ne mai daraja shima, ni ma nafi son Aliyun to" Dan murmushi Poul yayi, cike da farin ciki sukawa juna sallama. Washagari ta kama alhamis babu makaranta dan haka Mamy tace "Nur ta je ta gaida su Baffah, badan ranta yasoba ta fice, domin tasan yanzun Baffah baya gida, Umma kadai ta samu a gidan bayan ta gaisheta dakin Bashir ta shiga ta yi bincike-bincikenta tare da daukan duk wani abin da take so tasa a lada, sannan ta fito ta yiwa Umma sallama, ledan Umma tabi da kallo alokacin da Nur ke daf da barin gidan tace "Ji in da ta kwashe mishi kaya saikace ta bashi ajiya, ko da yake laifinshi ne, dan ba yau ta fara ba, shike barin ta." Karfe daya ta dawo gida, tana shiga falon Mamy tace, "Kin hadu da Bashir a waje? Girgiza kai Nur ta yi tare alamar a'a, "Kin mishi wani abu ne?" Mamy ta sake fada bayan ta tsare Nur da ido. "A'a Mamy ni mun dade ma bamu haduba." Zama tayi a hannun kujera yayin Aunty Saratu tace "Sai kikaji Poul ya Musulunta, wani irin faduwan gaba taji, dan haka tasa hannunta ta dafe kirjinta, adaidai lokacin da taji sallaman Bashir, waigawa ta yi ta kalleshi tare da saurin kawar da kant,a duk yadda yaso su hada ido taki yadda har ya wuce ya zauna, shiko Bashir kokarin hada Ido yayi ta yi da ita taki kallon shi, zuwa can ya mike ya nufa kofar fita tare da cewa "Nur zo"

Mikewa ta yi tabi bayanshi, motar shi suka shiga suka zauna, sannan ya dubi Nur yace, "Har yanzun kuna tare da Poul ne?

Batare da ta kalleshiba a ta girgiza kai, idonshi akanta yace "Me kika kasani geme da musuluntar sa?" Tana wasa da hannunta tace "Bansan komai ba."

"Karki min karya, gaskiya nake son ki gaya min, yana miki magana har yanzun ko?" Girgiza kai

ta yi tare da cewa "A'a"
"Amman kina da labarin ya musulunta?" Wannan karon ma kai ta girkiza tare da cewa aunty ce ta gaya min yanzu" Shiru yayi tsayon lokaci yana binta da kallo, zuwa can yace, dazon ina wurin aiki akamin waya wai ya musulunta nace badai sabo dake ba ko?" Kawar dakai ta yi tare da cewa "Ni bana magana da shi."

"Ya yi kyau kanwata" Duk nacin shi bazai aure ki ba, mu na haukane dan kawai ya musulunta sai dauke ki abashi? Ai ba a garin gaba-gaba muke ba, idan shi ya musulunta mammanshi da kanwarshi sun musulunta sauran dangin nashi fa? Irin shine sai kiga azo a haifi yara wasu musulmi wasu ba musulmiba, dan haka karkiga wai ya musulunta ki ce zaki saurareshi, idan ma musulmar ya ke son aure yaje can ya nemo a wata unguwa" Cikin sanyin jiki Nur tace, "Ni bana ma magana da shi" Ajiyan zuciya Bashir yayi sannan yayi sallama da ita ya koma gida. Sai dai ita Nur cike da damuwa take, dan haka ta shige daki, hawaye ta fara domin har ga Allah tana son Poul, sai dai kamar yadda Yaya Bashir ya fada itama akwai irin tunanin aranta, saidai tana ganin tunda ya musulunta ai tana iya aurenshi tunda da shi zata zauna bada yan uwanshi ba, irin wannan tunanin taita yi har tsawon wani lokaci, sai dare ta samu tai waya da Poul, cikin farin cikin yake bata labarin zuwansa wajen Malam Zubairu da yadda jama'ar unguwan sukayi farinciki da komawarshi addinin Musulunci, a karshe ya sanar mata da cewa Abbanta ma yaxo har gida da daddare nan yayi Murna, har ya kawo masa kyautar sallaya mai man sha'awa,, sosai wannan labarin yasa Nur farinci mara misaltu, so ta yi ta tambayeshi labarin matarshi, amman ta kasa, domin koda wasa be taba mata maganar matarshi ba, tuni Nur ta watsar da zancen Bashir sukasha soyayyarsu da Poul, sai da safe ta mayarwa Aunty wayarta.

****

Cikin wata biyu aka gama maganar makarantar Nur, dan haka ta fara zuwa, shigar mutunci take, ko da gyale zata saka to riga mai mutunci zata saka sannan ta tafi, hankali ta mayar akan karaton sosai, duk da cewa tunanin Bilkisu da na Aliyu suna adabar zuciyarta, kullum Nur jira take an ce mata Bilkisu ta haihu, ganin har an shafe wata hudu da faruwan abun ta zauna gaban Mamy tare da cewa "Mamy wai har yanzun Aunty Bilkisu bata haihu ba?

Cikin nuna halin ko in kula Mamy tace "Ta haihu mana" Cike da mamaki Nur tace "Yaushe?"
"Yanzu ina jin za'ayi wata biyu."
"Mamy shine baki gaya min ba?"
"Nur ni da nasan halinki ai bana fada miki ba, duka-duka Yaushe kika dawo hayyacinki."

Jimmm Nur ta yi idonta cike da kwalla zuwa can tace "Me ta haifa?"

"Mace akace" Shigowan Abdallah yasa suka daga Kai suka kalleshi, bayan ya zauna ya gaida Mamy ta amsa sannan Nur taci gaba da cewa, "Mamy babu wadda yaje ne daga nan gidan?"
"Aunty ku da Bashir sunje" Hawaye Nur ta matso sannan tace "Shine akaki gayamin barema aje dani, kuma bayan an min alkawarin za'a dinga kaini wajenta, ni ma gobe zani."

"Babu in da zaki, yariyar da akace ma bata maga me zakije kiyo?" Jin haka jikin Nur ya kara sanyi, mikewa tayi ta fita batare da takalli inda Abdallah yake ba, shiko Abdallah ta gefen ido yake Satan kallonta, bayan ta fice yace, "Wai mene ne Mamy?"
Nan Mamy ta gaya mishi abin da takewa fushi, tabe baki yayi tare da kawar da zancen. Adaren ranar tajewa Abba da zancen son zuwa gidan su Bilkisu, hakuri ya bata tare da nuna mata Bilkisu bata da lafiya, bama ta gidan yanzun haka. Kuka sosai Nur taci, domin abun sai ya dawo mata sabo, haka taci gaba da karatunta bata da walwala sosai, wata rana ta taso makaranta

wata zuciyar ta bata shawaran ta biya gidan su Bilkisu, karkacewa ta yi ta nufi hanyan gidan nasu, duk da cewa bata taba zuwa ba, mashin tahau ta sauka a daidai kofar gidan, sannan ta shiga, bayan ta shiga cikin gidan ta  ne ta iske mace daya a tsakar gidan kishiyar Maman Bilkisu ce Kawai a tsakar gida, bayan sun gaisa ta Gaya mata Bilkisu take nema, kallonta ta yi daga sama har kasa sannan ta tabe baki tare da nuna mata wani daki da baki, hanyar dakin Nur ta nufa nan ta hangi Bilkisu zaune da goyo a bayanta, wanni irin kallon Bilikisu tai mata mai cike da Mamaki, itako Nur da gudu ta fada jikin ta suka rungume juna sannan tai saurin sa hannunta ta kwanto yariya ta koma bakin gadon ta zauna tare da zubawa yariyar Ido, cikin zubar da hawaye take cewa "Allah sarki Aunty Bilkisu, ji yariyar mai kyau da ita, rungume yariyar ta kara yi sannan tace "Yaya sunan ta?"
Jin Bilkisu batace komaiba Nur ta dago ta kalli fuskar Bilkisu, gani ta yi tana hawaye dan haka ta sake cewa "Aunty Bilkisu Yaya sunanta?"
  Wannan karon ma batace komaiba illa Murmushi da take ga Kuma hawaye a gefen kumatunta, tunawa tayi da zancen Abba da yake cewa Bata da lafiya bata magana dan haka sake kallonta tare da cewa "Baki da lafiya Aunty Bilkisu da gaske bakya magana?" Zama Bilkisu ta yi abakin gadon dan haka Nur ta kara fashewa da kuka ta kalli Bilkisu ta kuma kalli yariyar, tana cikin wannan yanayin ta ga matar data hado da ita a tsakar gidan ta turo kofar tare da cewa "Idan kinga dama kizo ki dauki abincin" Mikewa Bilkisu ta yi ta fita, zuwa can ta dawo da kular abinci ta aje gaban Nur, sannan ta koma ta zauna, kallonta Nur ta yi tare da cewa "Kici Aunty ni akoshe nake, dauka ta yi ta fara ci Nur kuwa wasa takewa yariyar tare da kuka lokaci guda,  tas Bilkisu ta cinye abincin, sannan Nur ta Bata yariyar tare da cewa Zan tafi Aunty, sai na sake zuwa, Allah ya baki lafiya, ya Kuma saka miki koma waye yake da sa hannu a shigar ki cikin wannan masifar, wannan karon kai Bilkisu ta jinjija, cike matsancin kuka Nur tabar gidan, har Nur ta isa gida kuka take, dakinta ta wuce, kafin wani lokaci kanta ya dauki ciwo, acikin zuciyarta take cin alwashin in Allah ya yarda sai hukunci ya hau kan wadda ya yaudari Aunty Bilkisu, saiya amsa 'yarsa, sannan ita Kuma da yardan Allah saita dawo gidan Yaya Abdallah. Insha Allah wannan bazai zama karshen auren su, duk kokarin da take kada su Mamy su gane tana cikin damuwa saida su ka fahimta, Washegari fito tawa Mamy sallama zata wuce makaranta Mamy ta kalleta ta ce "Kukan me kikayi Ido duk suka kunbura haka?" Cikin kawar ta Kai tace "Ba kuka nayi ba, tashi kawai nayi na ganshi a haka" Kai kawai Mamy ta daga badan ta gamsu ba, itako Nur ficewa ta yi tun daga lokacin bata hada sati biyu ba tare da taje gidan su Bilkisu ba, yawan zuwan da take ta fahimci iyayen Bilkisu suna nuna mata halin ko in kula, wadda hakan ke sosa ranta, wannan dalilin yasa ta fara yiwa Bilikisu sayya tana kaimata, karutun da ta fara ya fara tasiri ajikinta ko da wasa bata taba barin wani ya gane tana zuwa gidansu Aunty Bilkisu ba, tsayon shekara ta dauka tana zuwa gidan, wata rana tana zuwa akace mata kanwar mamanta tazo ta tafi da ita, cikin rashin jin dadi Nur ta fito daga gidan Gashi babu sakin fuskan da zata tambayi inda aka kaita, wannan yasa Nur ta dawo gida ta bakin ciki da ta jima bata dawo cikin walwalaba, kullum dare suna waya da Poul da wayar Aunty, dan haka ta maida hankali kan karatunta sosai, yayin da soyayya mai karfi ke dadashigarsu.

BAYAN SHEKARA SHIDDA

Abuwa da dama sun faru zuwa wannan lokacin, sati biyu ya rage Nur ta kammala karatunta, sosai ta kara gogewa tare da waye da wayau baki daya, duk inda ake neman kyayawan mace

Nur ta kai, domin komai nata ya gama bayyana, ayanzu shekaranta 21, tuni Bashir ya saya mata waya tare da nuna mata lokaci yayi da ya kamata ace ta yi aure, sai dai har yanzu nunawa take tafi son karatu sama da auren, Tsakaninta da Aliyu kuwa soyayya ce mai karfi, sun aminta da juna bayan waya da suke kuman lokaci bayan lokaci suna haduwa a makaranta, hakanne yasa duk wanni wadda yasan Nur amakaranta ya san Aliyu, kuma tunda ya ke zuwa babu wadda ya taba gane musulunta yayi domin akwai Hausa radam abakinshi, a daddafe ya bari a ka kawo wannan lokacin a kullum bashi da magana sama tada aure, sai dai har yanzun duk wata kofar da zata saka agane tana tare da Aliyu Nur ta tosheta, Abdallah kuwa sauda yawa saidai ta jiyo muryansa domin tuni ya koma gidanshi can yake rayuwarsa sun jima sosai basuyi gaba da gaba ba saidai taji Muryanshi ko ta hango gilmawarshi.

Yauma kamar kodayaushe bayan Nur ta dawo makaranta tana kwance adaki Aliyu ya kira wayarta, bayan sun gaisa yace "Ya maganar da muka yi jiya?" jimmm Nur ta yi zuwa can "Tace nace kadan Kara hakuri ai"

"Haba Nur? mai yasa bakyajin tausayina, bakya gajiya da kiran hakuri, gaskiya na yi hakuri iya wadda zan iya, na lura laifinki ne, ke ce bakyason auren ba iyayen ki" Kasa ta yi da murya tare da cewa "Ba haka bane fa"

"To Yaya ne? tsayon shekara shidda kenan kina gaya min hakuri, har yanzun a gidanku ba'asan Ina yi ba, kince sai kin gama karatu, mai yasa bazaki bari akai maganar gida ba? amman shikenan tunda haka kike so" Katse wayar yayi batare da ya bari sunyi sallamaba, dan haka Nur ta kalli wayar tare da ya mutsa fuska, sam bata son bacin ranshi, duk da cewa ta sani yayi hakuri, afili ta ce "Ni fargaba nake, bansan mai Abba zaice ba, aduk ranar da yaganshi a gidan nan, wayar ta dago ta sake kiranshi saidai harta katse bai dauka ba, dadadre ma sake kira ta yi nan ma be dauka ba, wannan karon Murmushi Nur ta yi tare da fadi afili tace "Yayi fushi" kwanciya ta yi a gado ta rubuta sakon ban hakuri, nan ma koda ta tura bece komai ba, dan haka washegari da safe bayan ta yi shirin islamiyya ta biya gidan, tana tura get din ya juyo ya kalleta fuskarshi dauke da murmushi, ahankali ta karasa wajen ta tsaya tare da wasa da yatsunta, kallonta yayi sama da kasa yayi murmushi sannan yace "Kin tashi lafiya? Cankasan makoshi tace "Ai baka damu da lafiyataba"

"Mai yasa kikace haka.?"

Karya kai Nur ta yi sannan tace "Tun jiya nake kiranka baka dauka ba, na turo sako ma baka nuna ka gani ba" idonshi akanta yace "Na gani."

"To mai yasa baka dauka ba.." Kamar jira yake ta rufe baki yace "Saboda ba bukatata in tajin muryanki kina daga min hankali ba, a yanzu nafi bukatar in ganki kusa dani a matsayin matata, nagaji da hakuri Nur" Shiru Nur ta yi tsayon lokaci zuwa can tace "Kayi hakuri to"

"Ni ba wani hakurin da zanyi, jeki abinki"

Tsayon lokaci Nur ta dauka tsaye zuwa can tace "To yanzun Yaya kake son ayi.?" Batare da ya kalletaba yace "Dama nake son ki bani in tura gidan ku" Shuru Nur ta yi tsayon lokaci sannan tace "Ai na ce maka ka kara hakuri kadan."

"Shikenan na ji kije makaranta karki makara" ganin ya dauke kansa tabishi da kallo acikin zuciyarta take cewa "Bani da jarumtar da zan iya turashi wurin Abba, ina shakkar Abba sosai akan wannan, Juyawa ta yi ta fara tafiya har ta fice a get din be kirata ba, haka Kuma ko juyowa ya kalleta be yi ba wannan ya tabbatar da lallai ya yi fushi.

Koda taje islamiyya rasa walwala ta yi, bayan an taso gida ta wuce cike da damuwa, har dare

tana cikin damuwa, Misalin karfe takwas na dare taji Mamy ta kwala mata Kira, mikewa tayi ta fice, Abba ta samu zaune Yaya Bashir a gefen shi, gefe daya Kuma Aunty da Mamy ne, hira akaci gaba dayi zuwa can Abba yace "Nur bani hankalin ki" Cikin Sauri Nur ta mike ta dawo kusa da Abba, kallonta yayi kadan tare da cewa "Wai ni kwana nawa ya rage ki kammala karatunki?

Kamar jira take ya dire tace "Sati biyu ne Abba"

"Ma sha Allah, burin Nur dina yana daf da cika."

Yar dariya Nur ta yi tare da cewa, "Abba saima ka ganni a gaban Alkali." Bashir ne yayi dariya tare da cewa dallah saikace zata iya, ke kinsan aikin kuwa?masoraciya kawai ko karfi bakidashi"

"Yaya Bashir ai abin ba fada bane ko kai yanzu nan saina kure ka ka kasa cewa uffan."

"Haba? Dan Allah fa? Ta yaya zaki kure ni?"

"Sabo da na karanta Yaya, yanzu ba da bane, duk wadda yayi irin karatummu dole ya zama mai kaifin kwakwalwa da tunani, da iya hadda saboda low course ne da yake da bukatar haddace abubuwa da dama, kuma sai ka zama mara tsoro mai karfin hali da juriya, ya zama koda mutanen duniya aka tara maka zaka iya tashi ka gabatar da hujjojinka a gabansu batare da kaji wani dar ba." Baki Bashir ya bude cike da mamaki, Abba kuwa cewa yayi "Yauwa Nur gara ki gaya mishi ba lokacin banza kika bata ba" Jin haka Bashir da har yanzun be cire idonshi akan Nur ba yace "Tun da hakane tashi ki kare kanki da tarin hujjojinki da yasa kika kasa kawo mijin aure har zuwa wannan lokacin" Ya mutsa fuska Nur ta yi idonta akan Bashir, sannan ta waiga ta kalli kowa na falon, da alama sunji dadin abin da yayi, domin gani tayi duk ita suke jira suji mai zata ce, sunkuyar dakai ta yi tare da cewa, "Ai aure lokaci ne" Dariya Bashir yayi tare da cewa dole kice haka tunda kinki sauraron kowa ba" Mikewa Nur ta yi tare da cewa, "Ni dai abar mganar idan lokaci yayi ai zanyi" Tana kokarin barin falon "Abba ya ce dawo Nur ki zauna ai magana zan yi dake" dawowa ta yi ta zauna kanta a kasa, yayin da Abba ya shiga cewa, Nur ina ganin duk abin da ya kamata nai miki na adalci na yi, banso ace har ki kammala wannan karatu batare da kinyi aure ba, kullum cikin jiran tsammani nake amman har yanzun shiru, yanzun idan kin kammala kina nufin zakici gaba da zama a gida ne babu aure?"

Kasa dago kai Nur ta yi bare ta kalli Abba, ganin taki dago kai yace, "To dan Allah zan rokeki yadda na cika miki burinki ni ma kiyi kokari ki cika min burina, ki kawo min mijin da zaki aura, kafin ranar da zaki kammala karatun ki, a takaice dai, banson ki kara wata daya gaba batare da kinyi aure ba"

"Abba idan bata da saurayi akwai wani abokina dazan hadata dashi" Bashir ya fada cike da tsokana, Dagowa Nur ta yi ta kalli Bashir kadan ta sunkuyar dakai tana matso hawaye daya cika idonta, adaidai lokacin da Abba yaci gaba da cewa "Kina dashi ko ya kawo miki abokin nashi?"

Cikin sauri Nur ta juya baya tana mai turo baki tace "Ina dashi Abba"

Yar dariya Bashir yayi, shiko Abba cike da farinciki yace "Da gaske ko wasa?"

"Da gaske" Nur ta fada kanta akasa duk kuwa da cewa ta Juyawa Abba baya" Cikin murya irin ma me lallashi yace "To ku daidaita kijin ko? Ku nake jira dazan kin amince dashi sai kice mishi ya turo.

Amsawa Nur ta yi dakai tare da mikewa ta shige daki, cike da mamaki Bashir dasu Mamy suka bita da kallo domin babu wadda yasan tana da saurayi.

Bayan Nur ta shiga daki bakin gadon ta zauna tare da kirga kwanakin da taji Abba ya yanka

mata, tsintan kanta ta yi dason kiran Aliyu dan haka ta dauki waya ta kirashi, bayan ya dauka ta sanar mishi da halin da ake ciki, shima cike da tashin hankali yace 'Ai kinga irin abin da nake fada miki kenan, kina son ki samu cikin matsala, ni a shirye nake, gobe zan tura" Lumshe Ido Nur tayi tare da cewa, A'a kafin ka turo ka fara zuwa gidanmu tukuna ina ganin hakan zaifi"

Batare da wani tunaniba Aliyu yace "Shikenan goben zanzo."

Hakance ta kasance Washegari da daddare Aliyu ya aiko Kiran Nur, yayin da hakan ya faranta ran su Mamy, bayan Nur ta fice addu'a Mamy tai mata akan Allah ya daidaitasu ya kuma sa abokin zamanta ne nagari.

Fitan Nur ba jimawa Bashir ya shigo, kokarin zama yake tare da cewa "Mamy baki kuka yi ne naga mota a kofar gida.?"

Aunty ce tace "Ina jin bakon Nur ne" Shiru Bashir yayi zuwa can "Ya ce to acikin motar zatayi Hira? Mai yasa bazata shigo dashi cikin gida ba, ai wannan be dace ba" Ganin su Mamy basuce komaiba ya daga waya yakira Nur tare da bata Umarnin ta shiga da bakonta falon Abba, amsawa Nur ta yi sannan ta sanar mishi, farin ciki sosai yaji tare da addu'ar Allah yasa komai yazo mishi da sauki Kamar hakan.

Shiko Bashir jira yaitayi Nur ta shigo ganin dare na kara yi bata shigoba yayi sallama ya fita, ita ko Nur sai kusan sha daya ta shiga gidan, dan haka Mamy ta dubeta tace "Nur kalli agogo, daga Kai ta yi ta kallah tare da yin raurau da ido, sannan ta sunkuyar da kai, Mamy ce ta sake cewa Daga zuwa mutum yau-yau sai ki saki jiki har kiyo dare haka? Idon Nur akasa tace ban kulla bane Mamy, kallo Mamy ta kare mata sannan tace "To ina miki fatan alheri amman ki kiyaye da irin wannan, kin dai san halin mazan gidan nan, musamman Bashir.

Can kasan makoshi tace "Bazan kara ba" Hira suka dan taba, sannan Nur ta wuce daki cike da farinciki wadda ta jima bataji irinshiba, acikin zuciyarta tace ashe haka tadi yake da dadi, sai naji kamar karya tafi, yau daya naji kamar ankara min sonshi, cike da farin ciki ta kwanta, dan haka ko a bacin ta mafarkinshi taitayi har gari ya waye.

Washegari ma Aliyu yazo da daddare, falon Abba suka zauna hirar yau ma, hira suke mai cike da kyauna, yayin da Nur ke sanye cikin hijjabi, gaba dayansu murmushi suke domin sosai suke jin dadin haduwar tasu ta biyu, wadda suke ganin daren na masifar zura gudu, agogon dake wayarta taita kallo, domin karta sha'afa ta kuma yin dare, karfe goma na bugawa Aliyu ya mike tare da cewa ki je gida sai gobe, kar a sake miki fada.

Cikin kwalkwal da Ido Nur tace "Ka bari sai da darabi ta yi mana."

Cikin wani irin yanayi dake nuna jarumta kawai yake yace "Kije gida gobe zanzo da wuri."

"To ka bari saida kwata to" Cike da murmushi Aliyu ya kalli agogo tare da cewa "Ai da kwatar ma yanzun zata yi, nifa banki in kwana anan ba, kawai Ina lallabawa ne kar mu samu matsala da gidan ku, ko zamu canza lokacin haduwa ne domin cikin kwana biyun nan na fahimci dare jaren lokacine, Adaidai wannan lokacin aka ji an turo kofar, dan haka Nur tayi saurin waigawa afirgice

CIWON 'YA MACE
By
Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Bashir suka gani tsaye dan haka Nur ta yamutse tare da neman abin yi, shikowa Bashir cike da mamaki ya kara shigowa dakin yana kallon fuskar Aliyu ganin haka Aliyu ya mika mishi hannu, Kamar Bashir bazai bashi hannu ba zuwa can sai ya mika suka gaisa sannan ya juya ya fice tare da kallon Nur yace, "Nur zo" Bayan Bashir Nur tabi batare da ta baru sunyi sallama da Aliyu dan haka shi ya dada mata hannu tare da biyo bayansu.

Bashir na gaba Nur na binshi abaya har suka shiga cikin gida, daga bakin falon Bashir ya tsaya ganin hakan da yayi Nur ta tsaya ta kasa garasawa, kallo ya tsareta dashi sannan ya fara takowa yana kokarin zuwa inda take. Ganin tahowan Bashir Nur ta fara kokarin komawa da baya, dan haka yace, "Ina zaki?" Cike da tsiro Nur ta tsaya tana kallon shi, shima kallo ya kare mata sannnsn ya juya tare da cewa "Ki shigo ciki"

Ganin ya shige ta waiwaya bayanta ganin babu kowa yasata fara tafiya a hankali zuwa cikin falon, bataga kowa ba kamar yadda ta yi zato, Bashir ne kawai zaune afalon ya daura kafa daya kan daya sai fama shafa gemon shi yake, jikin Nur a asanyaye ta tsaya a saitin kanshi. Bayan tsayon wani lokaci ya juyo ya kalleta tare da cewa "Ki zagayo mana kin tsaya min akai" Zagayawa ta yi ta tsaya tare da kallon yatsunta tana ya mutsawa, tsayon loaci ya dauka yana kallon ta sannan yace, "Dama jiya wannan ne yazo wurin ki?" Batare da Nur ta dagoba ta daga kai a lamar eh" Kallo Bashir ya kare mata tsawon lokaci sannan yace "Tun yaushe ya fara zuwa?" Can kasa-kasa Nur tace jiya ne kawai" Kai ya jinjina zuwa can yace "Tun lokacin da nace miki ki rabu dashi kuna tare kenan?" Wannan karon kasa amsawa Nur ta yi dan haka daya gaji da tsammanin jiran amasanta yace, "Ba magana nake miki ba?"
Wasa kawai take da hannunta batare da tace komai ba, wani irin kallo Bashir ya mata sannan ya mike ya fice a gidan, batare da ya sake waiwayen inda take ba, Nur ma cike da damuwa ta wuce dakinta, washari da da safe cikin sanyin ciki tai sallama ta wuce makaranta, Bashir kuwa Daker bacci ya iya daukanshi sabo da tunani, dan haka washegari yana tashi aiki ya wuce gida domin ya dan kwanta, msalin karfe biyar ya shirya fitowa zuwa gidan Abba domin ya tabbatar ma kanshi ta dawo makaranta yanzun, adakinta ya sameta, Nur na ganshi gabanta ya fadi, daga tsaye ya tsaya Yana binta da kallo, cikin sanyin jiki ta gaidashi, jiran amsawarshi taitayi saidai har aka dauki tsawon lokaci be amsa ba, dan haka ta dago ta kalleshi. "Kar na kara ganinki da mutumin nan, idan Kuma har kika kara bari yazo gidan nan duk abin da ya biyo baya ki kuka da kanki, juyawa yayi batare da ya jira amsa daga garetaba dan haka Nur ta matso guntun hawayen da ya zubo mata ya sauka a kan kumatunta afili tace "Abin da nake ta gudu kenan, ni yanzun ya zanyi? Bazan iya kiranshi in ce ance ya daina zuwa ba, nasan bazaiji dadiba, kamar yadda nima bazanji dadiba, komawa tayi bakin gadon ta zauna, tunanin aunty Bilikisu fal zuciyarta, kasa Kiran Aliyu ta yi ta gaya mishi har aka kira magariba, babu abin da zuciyarta ke nuna mata sai Aliyu, ganinsa take yana Shirin zuwa wurinta, yayin da take tuna murmushinsa, bata ankaraba aka kira isha'i, alwala ta yi sannan ta tada Sallah, tsintan kanta ta yi ta idar da sallah batare da ta tuna maita karantaba dole ta mike ta sake kawo wata sallah tare da tattaro nutsuwa tasawa zuciyarta, bayan ta idar hannunta ta daga tana addu'a Allah yasa Aliyu yazama miji a gareta, karo na farko data fara addu'a akan aure, domin ada tafi yin addu'ar

Allah ya cika mata burinta akan karatu, yau sai gashi tana rokon Allah yasa Aliyu shine mijinta, kiransa ne ya shigo wayarta, batare data tashi akan sallayar ba, yana sanar da ita gashi a kofar gidansu, kirji Nur ta tafe tare da mikewa tsaye, tana ninke sallayar tare da cewa fili, "To ni Yaya zanyi? Inje ne ko kar in je? Amman Yaya Bashir ba a gidan nan yake ba, kilama yau bazai zo ba" Karfi guiwa taji, dan haka ta shirya ta fita tare da yiwa su Mamy sallama, Hira sukayi da Aliyu sosai, saidai bata da walwala, kuma karfe tara da wani abu tayi sallama dashi ta shiga gida, bayan ta shiga daki ajiyan zuciya ta yi, ganin Yaya Bashir bezo gidan ba, yau da wuri ta yi bacci saboda bashin baccin jiya,  dan haka washegari ma wuri ta tashi ta yi shirin makaranta, bayan ta gama shiryawa tana kokarin fita wayarta ta yi kara, dauka ta yi ta duba, Abba ta gani, dan haka tayi saurin fita ta nufa dakin Abbba, shikadai ta samu aciki bayan ta zauna ta gaidashi tare da cewa "Abba na ga ka kiran ni." Dagowa yayi ya kalleta sannan yace, "Eh naso in shigo tun safe nayi baki, kina jina? Gyara zama Nur tayi sannan tace "Eh Abba. Waishin wani yaro ne ya ke zuwa wajen ki?

Faduwan gaba Nur taji nan danan yanayinta ya canza tare da kasa cewa uffam. "Ina jinki Nur?"

Wannan karon ma batace komai ba bare ta dago Ido ta kalli Abba, kawar dakai Abba yayi sannan yace "Dole ki kasa magana Nur, abun yabani mamaki, kuma ya daure min kai, a unguwar nan idan akwai wadda yasan halin yaron nan a bayanki yake, acire maganar Addini tun da ya musulunta, bana manta ranar da kika zauna anan wurin kina rokona in rike uwarshi, sabo da ya gaza rike ta, Nur irin wannan mutumin zaki kawo min ya zama surukina? To ki shiga hankalin ki, karki sake bawa wani dama ya shigo min gida, ban amince dashiba kuma bazan amince ba." Zuwa wannan lokacin Nur ta fara kuka, idonta akasa, bayan Abba ya gama magana yace tashi ki bani wuri" Kasa tashi Nur ta yi tsawon lokaci dan haka Abba yace ko kina da mana ne?" Idonta na zubar da hawaye tace "Abba duk abin da yake da ya bari wallahi" Kallo Abba ya kare mata sannan yace, "Wannan zaton kine ai baki zauna dashi ba"

Hannu Nur tasa ta share hawaye sannan ta sake cewa, "Abba kayi hakuri mun yi alkawarin aure tun da dadewa dashi" Kallon mamaki Abba ya bi Nur dashi bayan tsayon wani lokaci yace, "Maganar da aka gaya min gaskiya ne kenan, dama an gaya min ina ganin kamar ba hakaba, tun kina secondary kike tare dashi, hakika kin yaudari kanki ni ma kuma kin yaudareni, sam banzaci zaki aikata hakanba, wato makarantar da na baki dama kiyi yasa kike ganin kina da 'yancin bada kanki ga wani? Kin gama yankewa shi zaki aura sabo da kin riga?" Wannan karon ma sunkuyar dakai Nur ta yi cikin matsanancin kuka, yayin da taji Abba ya ci gaba da cewa, "Baki Isa ba Nur kije acikin manemanki ki kawo min wani, tun da ke yar boko ce kuma kin iya munafunci" Kara roshewa Nur ta yi da kuka tare da cewa, "Abba wallahi shi kadaine, kuma shima ta waya ne kawai muke magana"

"Ke kika san wannan Nur sai kuma Allah daya hallicemu, Ni dai abin da nake gaya miki ki kawo min wani kafin sati biyun su cika"Jajayen Idonta ta dago ta kalli Abba tare da cewa "To ka Kara min lokaci Abba"

"Babu wani lokaci dazan kara miki Nur, in dai ba kina son ki nuna min iyakata bane, ke zaki kawo min wadda zaki aura, kinci sa'ar bani da ra'ayin yin auren hadi yau da kinsha mamakina Nur, kin bata min rai tashi maza ki bani waje" Mikewa Nur ta yi cike da damuwa ta fito, ji tayi kamar ta koma gida domin batajin kafafuwanta zasu ya fita da ita bakin get din gidansu, amman sanin dole taje makarantar yasata daurewa ta fice, saidai har ta isa makarantar kuka take, kafin

ta dawo idonta duk ya kunbura.

****

Ban amince wani ya sake zuwa wajen Nur ta fita wajensa batare da iziniba ba" Abba ya fada yana daga tsaye, yayin da Aunty da Mamy sukayi kasake suna kallonshi, ganin ya juya yana shirin fita Mamy tace "Alhaji wani abu ne ya faru?"

"Ina da ikon da zan hana duk abin da bana so acikin gidan nan..." Baki Mamy ta saki, bayan ya fice ta kalli Aunty Saratu tace "To kodai yayi mata miji ne, idan ba haka ba ai Nur ta isa abarta ta fita zance kuwa, Kuma shi da kanshi ya bata dan kankanin lokaci" Tagumi Mamy ta yi batare da tace komai ba, wuni Mamy ta yi da tunanin abin, har sai da Nur ta dawo suka kula tana cikin damuwa, dan haka Mamy ta Kirata daki bayan ta tareta da ido tace mai ke damunki? Kasa Nur ta yi da kai kamar Mai jira hawaye ya fara zubo mata, dan haka Mamy tace "Ina jinki" Nur na wasa da yatsunta tace "Mamy Abba ne, kasa karasawa ta yi dalilin kukan daya kwace mata, wannan karon Mamy batace komaiba, kallo ta bita dashi tsawon lokaci sannan tace, "Yayi miki magana akan wadda ke zuwa wajenki ko?" Kai Nur ta daga, hannu Mamy ta mika ta riko na Nur zuka koma bakin gado, sannan tasa hannunta ta fara share nata hawaye tare da cewa, "Daina kuka, ki gaya min mene ne dalilin shi" Idonta akasa tace yace ne in dakatar dashi karya sake zuwa." Jimmm Mamy ta yi sannan tace "Shi mai zuwa wajen naki wane ne shi Ina kuka hadu?" Kara fashewa Nur ta yi da kuka batare da ta iya cewa komai ba, Tsawon lokaci Mamy ta dauka tana tambayanta amma taki cewa komai, dan haka Mamy ta kira Bashir nan ya warware mata komai, sosai Mamy ta shiga cikin tashin hankali tare dabin Nur da kallon Mamaki, zuwa can talli Nur din tace, "Yanzun ke idan na fahimce ki son yaron nan kike kenan?" Nur Bata iya dagowa ta kalli Mamy ba hawaye kawai take share dan haka Mamy tace, "Shikenan, ni banzan ce komai ba, domin wani lokacin abin da muke so wata kila bashi bane alheri a garemu, dan haka zan roki Allah idan alakarki dashi alherine Allah ya kawo mafita cikin sauki, idan kuma ba alheri bane Allah ya canzashi da mafi alheri, kema kije kiyi iri wannan addu'ar, shi Kuma yaron ki dakatar dashi kamar yadda Abbanku yace."Sanyi zancen Mamy yasa Nur taji a zuciya, amma maganarta ta karshe ta Kara dawo mata da damuwa, domin Bata da bakin da zata iya dakatar dashi, mikewa ta yi ta koma daki, kuka ta cigaba dayi tare da addu'ar Allah ya sausauto da zuciyar Abba, domin shi kadaine zai bada matsala ko Baffah bazai bada matsala ba kamar yadda Abba zaiyi. Bata iya kiranshi ba, har saida ya kirata, gashi a kofar gida, sannan ta sanar mishi Abba yace ya dakata da zuwa, duk kokarin ta na kada ya fahimci akwai matsala Saida ya gane, dan haka suka kusa kwana waya akan neman mafita. Haka sukaci gaba dayin waya badare babu rana yayin da shakuwa ke kara shiga tsakaninsu, Yaya Bashir kuwa kwata kwata ya daina mata magana, saidai ya kalleta ya wuce abinshi, yayin da aunty da Mamy ke Kara karfafa mata guiwa akan tayi addu'a, dan haka Nur ta dan saki jikinta tare da yin alkawari babu namijin da zata kula har Abba ya gaji ya aura mata Aliyu.

saidai halin ko in kolan da Bashir yake Nuna mata ya dameta sosai, yayin da take rasa dawa zata tattauna matalarta.

Adaddafe sati biyu suka cika, Nur ce a farfajiyar makarantar su bayan kammala bikin yaye daliban da suka kammala karatun lauyoyi, wurin da Abba da Yaya Bashir ke tsaye ta nufa, Bashir ta gaida sannan suka jera yayin da Abba yake rike da hannunta yana mai nuna zallar farin cikinshi tare da yi mata addu'a, acikin zuciyarta take mamaki yadda ya saki jikinsa da ita yau, rabon da taka fara'a a fukarshi tun kafin ya san da zancen Aliyu, suna isa Motar taga Yaya

Abdallah zaune cikin motar, gani ta yi ya kara kiba yayi wani irin haske, kuma da alama kudi sun zauna mai dan motar ma da alama mai tsada ce kuma sabuwa dal har tana sheki, a yanzun gani ta yi kamar ba wanda ta sani bane abaya, dadewa da ta yi bata ganshiba da kuma mgnr da basa yi yasa a yanzun take mishi kallon tamkar ba dan uwansu bene,, dauke kanta ta yi daga kallonshi ta mayar da hankalin wurin Yaya Bashir domin yadda yake shareta yafi kona mata rai, "Yaya Bashir zo kaji" Nur ta fada cikin sanyin jiki, zagayawa yayi ya shiga motar tare da cewa "Sai mun hadu a gida" Abba ne ya shiga motar shima tare da murmushi sannan yace "Akwai alamar Bashir yana fushi da kanwarshi" Bashir bece komaiba har motar ta tashi, tsaye Nur tayi a wurin cikin sanyin jiki tabi motar da kallo, adaidai lokacin da Abdallah ya juya hancin motar tare da yi mata wani irin kallo, kallonshi ta yi ta yamutsa fuska, a hankali yake juya motar batare da ya cire idonshi akanta ba, mamakin kallon da ya ke mata yasata saurin Juyawa ta fara manganu kasa-kasa "in kalleshi ya ce na Harare" Cikin kawayenta ta shige, Abba kuwa bayan sun kama hanya hakuri ya bawa Bashir akan fushi da yake da Nur, shidai Abdallah besa baki ba, dan besan akan abin da ake magana akai ba, adaren ranar Mamy ta sanar da Nur dawowan Bilkisu, cike da mamaki take kallon Mamy tare da cewa "Mamy tun yaushe ta dawo"
"Ta dade da dawowa kuma ta samu lafiya, ta kira number Aunty ku yafi a kirga tana nemanki, bamu gaya miki bane sabo da halinki, to jiya kuma ta kirani awaya na mata alkawarin gobe zakije"

Cike da Farin ciki Nur tace to Mamy bani number insa a wayata, amsan ta yi tasa a wayarta, washegari da wuri Nur ta shirya, Saida ta kira Bilkisu sannan ta fito ta yiwa su Mamy sallama, bayan ta isa gidan cike da farin ciki suka rungumi juna sannan Bilkisu ta Nunawa Nur wurin zama ta zauna, har yanzun dai wannan dakin ne wadda take ciki ada, saidai wannan karon akwai dan walwala a tare da ita ta yi kiba sosai harta zarce da saidai ta yi baki sosai kuma fatar jikinta ya nuna ba wani hoto take samu ba, hakama suturar jikinta, cikin rashin jin dadi Nur tace, "Ina yata wadda bansan sunantaba har yanzu" Dan Murmushi Bilksu tayi sannan tace "Sunanmu daya"

"Allah sarki" Nur ta fada cike da tausayi, murya Bilkisu ta daga ta ce "Ummi!" Karamar murya Nur taji ta amsa, dan haka ta Nur ta mike tabi inda muryan yariyar yake, ganinta tayi tana dahowa dan haka tai saurin rungomo yariyar ta dawo ta zauna tare da zuba mata Ido, sosai yariyar take kama da Bilkisu, kamar harta bace, idon Nur cike da hawaye tace "Auntymu kiga yadda ta girma, kai Masha Allah, yar dariya Bilkisu tayi, kallo Nur tabi yariyar dashi, da alama itama bata da suturar kirki, dan kunnen dake kunnenta ma yayi baki dagowa Nur tayi ta kalli Bilkisu tare da cewa, ta fara zuwa makaranta ko?

Yar dariya Bilkisu ta yi tare da cewa a'a bata fara ba Nur.

"Amma ya kamata ta fara zuwa makaranta"

Na sani Nur, amma babu yadda zanyi, ko kofar gida ba'a barina naje bare na nemi kudin dazan kaita kuma acikin gidan na babu wadda zaikaita makaranta, Nur in takaice miki Kamar wata bare haka nake acikin gidan nan, kinsan tunda wannan abin ya faru Momyn mu sun rabo da Daddy, na kasa yafewa kaina wannan abu, sun hadu tun ba'asan damu ba, gashi nazo na yi sanadin rabuwar su, wallahi Nur ni banzo duniya a sa'a ba, tun daga ranar da naga rikicin da Daddy sukayi da Momy nazama kamar gawa gani a duniya ina kallo Ina ji amma inaji tamkar acikin kabari nake, yanzun haka abu kadan zanyi kiji Daddy na zagina Kamar ba shibane wadda na sani ada dan haka ni komai baya min dadi, itama Ummi dandai yariya ce bata san

ciwon kantaba da ko dakin nan ace mata ta fita baza ta fitaba amma sai kika ana mata mugunta tana makalewa.

Cikin share hawaye Nur tace "Ki daina barinta tana fita, ku zauna tare"

"Idan na hanata fita Nur shima ba gata bane, zan iya mutuwa in barta, gara ta saba da walar koda ace zai yi sanadin mutuwarta, kinga idan ta mutu ta huta.

Wanni irin kallo Nur tawa Bilkisu tare da cewa "Wacce irin magana ce wannan"

To Nur mai zata yi a Duniyar bayan babu ni, bata da uba bare danginshi, 'yan uwana kuma sunki yadda da wannan kaddarar" Hawaye Nur ta share sannan tace, "Aunty dan da aka tsunto ma ba'asan warshiba ba a san ubanshi yana samun iyayen da zasu rikeshi kamar dan da suka haifa, kisa a zuciyarki wannan jarabawa ce kawai Aunty, sannan kuma Ni gaskiya bazan boye miki ba, ina ganin laifinki acikin wannan lamarin"

"Mene ne Laifin nawa Nur?"

Aunty karkiga kamar na miki rashin kunya dan Allah ki gaya min, Yaya Abdallah mu bashi bane Baban Ummi?, idan kuma bashi bane to waye Aunty?

CIWON 'YA MACE

BY

Fadila Lamido

ADABI WRITER'S ASSOCIATION

Page 50

Zamewa Aunty Bilkisu tayi daga kan gadon zuwa kasa, tare da fashewa da kuka, saida tayi kuka ma'ishi sannan tace, "Nur bantaba soyayya da wani namiji ba sai shi, ni nama kaina cikin? Shine saurayina na farko kuma shi na aura, acikin kwana shidda da mukayi a tare be kusance ni ba tabbas, amman akwai wani srirri tsakanina dashi" Cikin rashin fahimta Nur tace "Har yanzu baki bani amsa ba Aunty" Hawaye ne suka zobowa Bilkisu alokacin da take cewa "A zahiri bashi bane babanta, amman a badili bata da uban da ya wuce shi." Mikewa Nur ta yi tare da cewa, "Yaya Abdallah yasan da hakan?"

"Hmmm, be sani ba kamar yadda ya nuna"

To mai yasa kikayi shiru  tun abaya Aunty?

"Nur! Nayi shirune sabo da bani da hujja da kuma yanayin yadda ya bijiro da maganar ya fini gaskiya, babu wadda zai fahimce ni"

Shiru Nur ta yi tsawon lokaci zuwa can tace, "Tunanin ki kenan babu wadda zai fahimceki amma akwai, Aunty na shirya taimaka miki ki fita daga cikin wannan zargin"

"A'a, Karki fara Nur, zaki tayarmin da fininane kawai na samu abin ya fara kwanciya, bazaki iya ba Nur, kinyi kankanta, iyayenshine kawai zasu iya tursashishi, saidai su dinma babu hanyar da zasu fahimce ni."

"Aunty idan anyi shiru zancen ya kwanta mai zakicewa yariyar nan alokacin da ta bukaci son ganin Ubanta? Ni dai ki bani hadinkai kawai."

"A'a Nur, ki bari kawai, Kinga akwai zumunci a tsakanin ku, wannan maganar tana iya lalata muku zumunci, kuma daga karshe baza'a fahimce ki ba, nagode Nur bazaki iya ba."

"Zan iya Aunty, bazan yi maganar nan da kowa a gida ba, na yi wayau yanzu ba yadda kike tunani bane, karar shi zaki yi a kotu, ni kuma zan tattara hujjoji in tsaya miki, abun mai sauki ne indai kin bani hadin kai, dole zai amsa yariyar nan." Shiru Bilkisu tayi tare da cewa "Su Mamy ma ai bazasu yarda ba Nur, da sunji zaki shiga maganar komai na iya faruwa."

"Babu ma wadda zai sani Aunty, shi ya Abdallah takardan kawai za'a kai mishi sai in yaje koto" Nutsuwa ne ya fara shigar Bilkisu, domin bata tabayim irin wannan tunanin ba, ajiyan zuciya Bilkisu taitayi, yayin da take karajin nutsuwa na shiganta, saidai tana ta tunanin zumuncin Nur da Abdallah karya samu tankarda, dan haka Nur ta nuna mata ko ba itaba akwai kawayenta da zasu iya taimakawa, jin haka Bilkisu ta gamsu, har suka yanke karahen watan za'a shigar da karan kotu. Wannan ranar cike da farin ciki Nur ta koma gida, haka ma Bilkisu wani irin nishadi taji yana shigarta domin kuwa idan har akwai yadda za'ayi kowa ya gane ita ba yar isa bace zarafi kowa farin ciki da hakan. Nur kuwa aharabar gidan ta samu Abdallah da Yaya Bashir zaune, sun shinfida babban darduma, wucesu tayi bayan tawa Yaya Bashir sannu, daker ya amsa tare da hararan bayanta, Abdallah ne ya kalli Bashir yace "Wai Bashir mai ya hadaka da yariyar nan ne wai? Abin mamaki yake bani, yadda kake mata yanzun"

"Hmmm, Abdallah na kule sosai da ita, kaima ai kaban haushi shiyasa ban gaya maka ba, tun kafin abin yayi nisa na kawo maka zancen kaki saurarona, har ankai matakin da yanzun Nur ta tage wai wannan Poul din zata aura"

Wanni irin kallon Abdallah yayi wa Bashir tare da cewa "Da gaske ko wasa?"

"Wanni irin wasa kuma, dan Allah waike duk gurmin da akayi agidan baka sani ba?"

"To ni inama nake zuwa gidan, ko nazo ma ni aba'amin maganarta, yanzu ita da gaske take zata aura wadda ba musulmiba?"

"Ai ya musulunta, tun shekara 6 baya, kuma wallahi sabo da ita ya musulunta, sun dade tare wannan abun Yana Kona min rai, yama raina mutane, abin ma da yake kara kuna min rai, wai Abba cewa yayi idan ta dage bashi ita zaiyi, dan bazai mata auren dole ba, narasa mai yasa Abba ke lallabata, duk abin da take so shi yake mata, wai yasa a mishi bincike akan halayyar yaron a yanzun tunda shi take so"

"Wanni irin kallo Abdallah yayiwa Bashir, tare da cewa, "Aiko bazata aure shiba, ka bari zanyi maganin abin, ai naga ta girma yanzu, har wani kwambu takewa mutane, ni tama wuce da ajina ko kallona bata yi bare da kaisheni, ni banso Abba ya barta ta yi karatunbama, amman zanyi maganinta idan bata gaidani dan Allah ba zata gaidani dan dole" Mikewa Bashir yayi cike da haushi yana cewa "Narasa wanni iri so Abba yakewa yariyar nan, sam baya son bacin ranta, nasan tun da yace haka babu wadda ya isa ya hanashi yayi mata abin da ranta yake so cikin mu.

Bayan Bashir Abdallah yabi da kallo, har ya fice acikin gida, sai fada yake kasa-kasa, da alama sosai abin yake sosa ranshi, mikewa Abdallah yayi shima ya nufi cikin gidan, adakin Mamy ya samu Nur zaune kusa da Mamyn, sallamar da yayi Mamy ta amsa itako Nur dagowa ta yi ta kalle kofar ganin Abdallah ne ta kauda idonta tare da mikewa tsaye ta dauki wayarta da kwanon cincin din dake gabanta ta fice batare data kalli Inda yake ba, Binta da kallo Abdallah yayi har ta jawo kofar sannan ya kalli Mamy alokacin da take cewa Bashir fa?

"Ajiyan zuciya yayi tare da cewa ya wuce ai, amma kila zai dawo anjima"

"Be min sallama ba, naso na ganshi kafin ya wuce"

"Lafiya?" Abdallah ya fada bayan ya tsare Mamy da ido"

"A'a be shafekaba maganar Nur ne, kuma aikai ba shiga lamarinta keke ba" Mikewa Abdallah yayi tare da cewa "Kai Mamy, wai be shafeni ba" Juyawa yayi yana kokarin fita adakin tare da cigaba da cewa "Shikenan dai" Bin bayanshi ta yi da kallo har ya fice sannan ta tabe baki tare da cewa "Aure dai ya gagari Abdallah idan ma wani abin yake har yanzun Allah ya shiryeshi ya dawo dashi kan haya kan madaidaiciya. Lokacin da Abdallah ya fito Nur na zaune afalo, can gefe ta juyar da kanta, shiko ta gefen idon sa yake kallonta har ya fice afalon. Adaren ranar Bilkisu ta kira Nur a waya bayan ta mata bangajiya tace, Nur hankalina yana ta kara nutsuwa akan maganar shigar da karan Abdallah, sai dai ina tunanin karya rofe ido ya min rashin mutuncin da yayi min abaya.

"Hmmm, Aunty Bilki shari'a sabanin hankali ce, nasan halin Yaya Abdallah fiye da yunwar cikina, idan baki mantaba bama shiri ni dashi, nasanshi farin sani makirine, nasan ta yadda zan bollo mishi"

Amman Nur sai nake ganin idan na sakaki agaba amatsayin wadda zata karenj a kotu rikicin ku da Abdallah zai kara gaba kuma ban miki karaba"

"Kara? Har kike maganar kara Bilkisu ai wannan abin kamar taimakonshi ne za'ayi idan ya yaga laifina nasan daga karshe iyayenmu zasu fahimta, yanzun da baya magana dani din kare ki nayi, ai ki cire wannan tunanin, kisa a zuciyarki cewa baki sannan alakarmu dashi ba, ni Kuma na miki alkawarin in sha Allah Abdallah saiya karbi Ummi, Ina da tarin hojjojin da zaisa Alkali yabawa Abdallah Ummi amman sai da hadin kanki, wai to mai ya hana Abdallah ya kusanceki tsayon kwana shidan?"

Wallahi Nur haka kawai bayan ya gama wasa Dani yace wai mukulla.

Lumshe Ido Nur tayi, ganin hakarta ta fara cimma ruwa, cikin dibara Bilkisu zata fada mata yadda akayi Abdallah yayi mata wayau, afili kuwa cewa ta yi, "Ai tun barko naso da aka tambayi ki ya kusanceki kice eh kawai, tunda ya kwana dake adaki daya akuma kan shinfida daya kuma saida kika cika wata goma da auransa kika haihu dan haka aure ya bashi, matsalar kawai ke da kika ce be kusanceki, to amman nasan yanzun zaki fada min komai ai"

"Ai ni Nur yanzun mafita kawai nake nema abin yaki ci yaki cinyewa"

"To kije ki shirgar da karanshi koto da zaran an kawo mishi sammaci zanzo muyi magana"

Sallama sukayi bayan Bilkisu tawa Nur godiya.

Bayan sun gama waya falo ta fito ta zauna cike da tausayin Bilkisu a yammacin ranar gaba dayan su suna falon Mamy Aunty sai Nur, hira suke sama-sama sukaji sallamar Mamma, cikin sauri Nur ta juya ta kalleta sannan tai saurin rufe idonta kamar mai bacci, dan a yanzun yar kunya suke shiyasa sai su jima basu hadu da Zainab  da ita ba domin yanzun ba shiga cikin gidan take ba, hakama Zainab bata zuwa tunda ta gaya mata abin da Yaya Bashir yace akanta , su Mamy ne suka amsa sallamar bayan ta shigo suka nuna mata wurin zama, Ganin haka Nur ta tashi zaune tare da gaida Mamma cike da jin nauyinta, itako Mamma cike da nuna kauna ta amsa, mikewa Nur ta yi ta nufa daki alokacin ta taji Mamma na cewa "Mammy wurin ki nazo" dan haka ta kasa shigewa dakin ta makale jikin bango, muryan Mamy taji tana cewa "To gani Mamman Zainab" Cikin nutsuwa Mamma tace "Mammy Nur na zo akan maganar Nur da Aliyu na, naji cewa yanzu kunsan suna son junansu, dan Aliyu ya gaya min abin da ke faruwa, Aliyu na son Nur sosai, ta dalilinta rayuwarshi ta canza, ta dalilinta yana kula dani da kanwarshi, Kuma har gobe kullum hallayyarshi dada gyaruwa take, na fahimci a yanzun da rayuwar Nur yake koyi, Duk irin tsaron da ya kula ana bawa Nur a gida irinshi yake bawa Zainab, duk abin da

ya kula inaso kafin ma in fada yana mini, tunda Aliyu ya musulunta bansake zubar da hawayen damuwarshi ba, domin kullum nunawa yake yafi jiya kirki, a yanzun nasan samun shi nasan rashinshi, haka kuma dazaran ya shiga damuwa gabana yake kawo damuwarshi, bazan boye muku ba Ina jin dadin wannan yanayin da muke ciki, Kuma na tabbatar da cewa Nur ce ta kawo haske acikin rayuwarmu, ya jima da rabuwa da matarshi yanzu ko sunanta baya son a ambata, Mamyn Nur, Dan Allah ku taimakeni bana son ya rasata, sun dade tare, sun saba da juna, tunda yaji abin da Babanta yace ya shiga damuwa walwalarshi ta ragu, zamowa Mamma ta yi kasa ta Isa gaban Mamma ta rike kafarta tare da cewa, "Dan Allah ki taimakeni kuyi hakuri karku nuna kyama a garemu"

Yadda Mamy taji ta rukurkume kafarta yasata dafa kafadar Mamma tare da cewa tashi Mamman Zainab, ai matar mutum kabarinsa ce, duk yadda wani yaki ta da Aliyu, idan Allah ya nufa matarsa ce babu wadda ya Isa ya hana, haka Kuma duk iri son da danginta sukewa Aliyu idan Allah ya nufa ba mijinta bane ko ranar auren ne baza a daurashi ba, abin da nake son ki gane shine, wani baya taba auren matar wani, tun da naji wannan labarin addu'a nake idan Alheri ne Allah ya tabbatar, idan Kuma babu alheri Allah ya canza musu da mafi Alheri, shi kanshi Abbata gabanta ne ya tsaurara abin, amman a bayan idonta addu'a yake Allah ya zaba abin da yafi alheri" Nur dake labe ajiyan zuciya tayi tare da murmushi, acikin zuciyarta take cewa "Ai nasan Abba bazai matsa min ba, kuma nasan idan na dage Aliyu nake so zai aura minshi, domin shine ma alheri, saboda shi nake so, Kuma na dage da addu'ar Allah yasa ya zamo mijina" Muryan Aunty ta jiyo tana cewa "Mamman Zainab ki kwantar da hankalin ki, kema ki nemi zabin Allah, amman ko kadan ba yadda kike tunani bane" Mikewa Mamma ta yi sannan tai godiya, tana kokarin fita Mamy tace "Kuma idan Abbanta ya dawo zan sanar dashi zuwanki dan ya kara daukan abin da mahimcin" Sosai Mamma taji Dadi ta fita tana godiya bayan Mamy da Aunty sun Dan taka mata. Daki Nur ta koma cike da farin ciki, tshinta kanta ta yi dayin dariya ita kadai a dakin. Adaren ranar taji Baffah yazo, Mamy da Aunty falon Abba suka tafi, Dan haka ta fito falo ta zauna, tun tana jinta cikin nishadi har ta fara gajiya da zama, domin gani ta yi har goma ta buga batare da sun dawo ba, mikewa ta yi da Nufin wucewa daki taga su Mamy sun shigo, Aunty ce ta dubeta tace "Ina zaki? Bacci nake ji, zanje in kwanta" Nur ta fada tana kokarin famintan fuskarsu, Mamy ce tace "Ki yi sauri ga Baffanku can kije ku gaisa" Aunty ce tace "Anya kuwa taje?" Ji tayi Mamy tace "Gara taje tun da Abban su ya yanke magana bazaice komaiba Kuma" Ganin sunyi shiru Nur ta juya ta fita, hangosu ta yi a harabar gidan suna kokarin fita shida Bashir, dan haka ta daga daga Murya tace "Baffah!" Waigowa yayi ya kalleta, sannan ya juya yaci gaba da tafiya, Bashir ma Waigowa yayi ya Dan kalleta sannan ya bode motar ya shiga, shima Baffah cikin motar ya shiga ya zauna, Adaidai lokacin da Nur ta tsaya bakin get din tace "Baffah Ina wuni" Daker ya iya Bude baki yace "Lafiya lau" kafin ta sake cewa wani abu taga Yaya Bashir ya ja motar sun wuce, da sanyin jiki ta koma cikin gida, tana kokarin shiga falon taji su Mamy na cewa "Ai dole aji ra'ayin Ummynta, ba a yanke hukunci ba" Jin haka yasa tana shigowa ta masu sammala ta shige dakinta cike da damuwa, bayan ta gama tunanin yadda Abba ya amsa gaisuwarta, ta koma tunanin Ummy da taji su Aunty na maganar za'a nemi shawaranta, tsaki taja fali, tare da cewa "Wai dama haka ake shiga damuwa lokacin aure? Kowa sai an nemi shawaranshi? Yanzu nasan ana tambayan Ummy sai ta yi shawara da yaranta, duk su gama zugeta tunda ba sona suke ba" wayarta ta jawo ta Kira Ummy, cikin yanayi irin na wadda ya fara bacci tace, "Nur lafiya bakiyi Bacci ba har yanzun?"Eh Ummy, cikin

nutsuwa ta fara bawa Ummy labarin Aliyu daga karshe tace "Ummy idan an tambaye ki kice kin yarda karkiyi shawara dasu Yaya Jamal" Jimmm Ummy ta yi bayan tsawon wani lokaci tace "Ke ce ma zaki gaya min abin da ya dace in yi?" Kina hauka ne Nur tubabben zaki aura sabo da idonki ya rufe ko?" Can kasan makoshi Nur tace "Ummy mun dade tare, dan Allah karkice komai, yadda tai maganar Kamar ta ce wayyo Allah yasa Ummy cewa "To ni gaskiya Nur idan zan gaya miki kiji banaso, maganar iyayenki Kuma idan sunkirani bazance komaiba tunda ubanki na raye, duk abin da ya yanke shikenan, amman ke ina son ki canza tunani" "Ummy shi nake so, shakaranmu shidda tare, dan Allah ki mana addu'a kawai, kuma karki bari su Yaya Jamil su sani"  Sabo da kin dauke su makiyanki ko? "A'a Ummy, ba haka bane, ni kiyi hakuri dan Allah"
Can kasan makoshi Ummy tace "Shikenan, naji, Saida safe, kashe wayar ta yi batare da ta bari Nur ta yi magana ba, dan haka Nur ta kalli wayar ta yi murmushi kadan. Washari Misalin karfe bakwai na safe, Abdallah ne yayi sallama falon Baffah, Baffah da Bashir ya samu aciki, dan haka ya Isa daf da Bashir ya zauna, tare da gaida Baffah, bayan Baffah ya amsa ya bawa Bashir hannu suka gaisa, Baffah ne yace "Jiya da daddare ai na dauka zanzo in sameka anan?" Murmushi Abdallah yayi, tare da cewa, "Na dan jira ai Baffah da naga shiru na wuce nace da safe na dawo" Baffah ne yace "Toh hakan ma babu lalifi, Ina can gidan nakune ai, Babanku ne ya kirani, Jinjina kai Abdallah yayi alokacin da Bashir ke bin Baffah da Abdallah da kallo, ganin haka Baffah ya kalli Bashir yace, "Jiya lokacin munacen gidan Abdallah ya kirani awaya gashi yazo wurina bana gida." Murmushi Bashir yayi sannan ya kalli Abdallah dake kokarin saka wayarshi a aljihun gaban rigarshi, a daidai lokacin da Baffah ke cewa "Abdallah to ya wajen kasuwancin ku?"
"Alhamdulillah Baffah"
"Ma sha Allah, Baffah ya fada  yayin da ya sake cewa to lafiya dai ko keke nemana?" Wannan karon sunkuyar da kai Abdallah yayi tare da shafo keyarshi yace, "Lafiya lau Baffah, dama akan maganar Nur ne" Cike da Mamaki Bashir yabi Abdallah da kallo, kosawa yayi yaji wata dibarar zai billo dashi domin hana auran Nur da Aliyu, gani yayi Abdallah nata fama shafa keya, har Saida Baffah ya sake cewa "Inajin ka Abdallah?" Kanshi akasa ya ce, "Baffah dama ina santa ne, abani auranta"
Wanni irin kallo Bashir yawa Abdallah yayin da Baffah ke cewa "Ikon Allah, kai kanka ko kuwa abokinka ka ke nemanmawa?"

Batare da ya dago kansaba yace "A'a, ni ne Abba."Shiru Baffah yayi yana kallon Abdallah da har yanzu kanshi na kasa, haka shima Bashir har yanzun ya kasa cire idonshi akan Abdallah, mamaki yasashi rasa a inda yake, daker ya iya juyar da kanshi ya kalli Baffah dake dannan waya fuskarshi daure, kosawa yayi yaga mai Baffah ke shirin yi Kuma, bayan ya gama dannawa a kunnensa ya daura tare da cewa "Barka da safiya" Shiru yayi zuwa can yace "Abdallah ne yazo yanxun ya sameni akan cewa yana son Nur, zai aureta" Shiru Baffa yayi sannan yace "Nace nabashi"  saurare ya tsaya yi daga cikin wayar sannan ya cigaba da cewa, " 'Yarkace amman ai danane yake so, a'a dakata mana, ni ban maka katsalandanba, yariyar yar kace ni kuma na sanar maka d'ana naso, nasan baza'ka iya ce min a'a ba, ko ka tsallake ni kabawa dan wasu" Shiru Baffah ya sake yi zuwa can yace "Ba biye mata za'ayi ba ai" sauke wayar yayi sannan ya kalli Abdallah dake sukuye dakai har yanzun yace, "Shikenan ka je karka damu"

Godiya Abdallah yayiwa Baffah, sannan ya mike ya fita, Bashir kuwa bin Abdallah yayi da kallo har ya fice, Daker ya iya mikewa yabi bayanshi, acikin motar ya samu Abdallah jiki a sanyaye, cikin kureshi da Ido yace "Abdallah lafiyarka kalau kuwa?"

"Hmmmm, Mai ka gani Bashir?"

"Nasan tsakanin ka da Nur ba shiri kuke ba, kasha cemin ba ruwanka da ita, amman kaje kana cewa Baffah kana sonta zaka aureta, wai kana nufin bayan ka kore Aliyu zaka dawo kace wasa kake ne?"

"Hmmmm, Ba wannan maganar Bashir, da gaske nake zan aureta.

Kallon cikin Ido Bashir ya sake yiwa Abdallah tare da cewa "Ta yaya zaman ku zai yiyu ahaka alhalin ba son juna kuke ba?"

"Ni ina sonta Abdallah, kuma itama nasan nan badadewaba zata soni."

"Tab lallai, dan Allah Abdallah karka lalata mana zumunci."

"Bashir ka kwantar da hankalinka, tunda nace ina sonta Ina sonta ne. Ban damu da tasoni a yanzun ba, da zaran an daura auren anyi me wuyar, sati daya yayi yawa zata saki jikinta, in dai nine, kuma da bakinta zakaji tana yabon halina, cikin awanni zan iya canza tunaninta, domin ni kamar wahainiya haka nake, a duk lokacin da naso ina canza launi."

"Kafada Abdallah ya daga, tare da cewa shikenan Allah ya tabbatar da alheri" Motar ya bude ya fita yayin da Abdallah ke cewa "Bazakaje can gidan ba" batare da Abdallah ya juyoba yace "A'a" Motar ya tada yabar wajen, shiko Bashir dakinshi ya koma ya zauna, duk yadda ya so ya samu nutsuwa ya rasata, ganinsa yayi yanata zarga-zarga bashi zaune bashi tsaye, zuwa can yasa hannun sa ya shafi kumatusa ruwa yaji, dan haka ya kalli Hannun tare da cewa "Hawaye?, Mai yasa zanyi hawaye dan d'an uwana yace yana son Nur, Mai yasa lokacin da naga an amince mata da Auren Aliyu banyi hawaye ba?" Tsaki yaja afili, sannan yaci gaba da cewa "Ashe ni ma dai wawane, wani tsaki ya sake ja, sannan yayi murmushi ya nufi bayin dake cikin dakinshi ya wanko fuskarshi.

*******

Ku tayani Jin wani al'amari mai ban mamaki, Wai Abdallah ne yaje wajen Baffah su wai yana son Nur zai aureta"

Tukunyar dake hannun Nur ce ta subece ta fadi, Karan fafuwarta yasa su Mamy waigawa gaba daya, "Abbane yace waye yayi Bari?" Cikin sauri Mamy tace "Nur ce"

"Au tana gidan ne? Agogon dake daure a hannunshi ya kalla tare da cewa "Bata wuce makaranta ba?" Cike da damuwa Mamy ta Isa bakin kitchen din kokarin shiga take taga an turo kofar, hannu tasa ta tura amman ko motsi kofar bataiba, hakan ya tabbatar mata da kulle kofar ta yi, Aunty dake bin bayan Mamy ne ta ce "Taji abin da Abban su ke fada ne fah" Shiko Abba kofar ya fara bugawa tare da cewa "Nur to mene ne na rofe kofar kuma? Ki fito mana kiji."

Nur kuwa komawa ta yi ta jingina da jikin bango bayan abincin ya bare a kasa, Ahankali ta zame ta zauna akasa, tare da kai hannunta duk biyun ta daura a ka, saidai babu ko digon hawaye a fuskarta, bakinta ta motsa tace "Na shiga uku na lalace, wannce irin masiface? Ya Allah na rokeka karka kaddaro min auran Yaya Abdallah, mugu ne, azzalumi macuci, wadda besan darajan mace ba" Kasa ta karayi da murya tace "Mazanicine ya Rabbi karka hadani aure dashi, Fasikine masharraci, idan akwai sunan da yafi na zalinci muni Yaya Abdallah ya cancanshi" Murya Mamy taji cikin rawa sosai tana cewa, "Nur daga Jin ana magana sai ki rufe kanki aciki, kina haukane? Ki bude ki fito ai ba dole ba" Shura kafa Nur ta fara kamar mai shirin

yin birgima, kasa-kasa taci gaba da cewa, Mamy bazan iya kallon idan ku keda Abba ince bason Abdallah ba, idan kuma bance banson Abdallah ba, yaya zanyi da Aliyu, ina tsananin sonshi, shine irin namijin da nake son aure, yaya rayuwar shi zata kasance bayan ya rasa ni" Sai wannan lokacin hawaye ya zobo mata, yayin da taci gaba da cewa "Zaice naci amanarshi bayan Kuma ni shi nake so, zaice na yaudareshi tsawon shekara shidda, wallahi bazan iya rayuwa batare da Aliyu ba, ina tsananin tausayin shi, Kuma Yaya Abdallah wurin Baffah yaje" haura kafa ta sake yi tare da cewa "Idan ma wurin Abba ya tsaya ya zanyi ince bana son d'ansu? Bayan sune suka raineni har nazama cikakkiyar mutum, na shiga uku, zai yi wuya in tsallake auren Abdallah, ni gaskiya bazan aureshi ba, saidai idan mace tana auren maza biyu" a daidai wannan lokacin wayar Nur da ta fadi akasa tai kara, kallon wayar ta yi tare da rarrafawa ta isa gabanta ta dauka, ganin sunan Bilkisu yasa gaban Nur faduwa tare da tuna alkawarin su, cike da jarumta ta dauka, muryan Bilkisu taci cike da zaki tana cewa "Nur na je na shigar da kara har an taho kawo mishi takardan sammacin" Kasa cewa komai Nur tayi domin gudun karsu Mamy dake bakin kofar su jiyota.

Abba kuwa tuni hankalinshi ya tashi domin ko motsin Nur din basaji, dan haka yanzun da yaji wayarta tayi kara ya cigaba da kiran sunanta cikin tsayawa tare da bata Umarni ta bude kofar....

Alhamdulillah anan nakawa karshen Littafi na daya free ne, Littafi na biyu za'a daurashi ne akan manhajar Arewabooks, ku biyoni domin jin yadda zata kasance acikin Littafin na biyun kuma na karshe da yardan Allah, yanzu za'a fara wasan, wannan labarin salonshi daban ne, wadda baya anfani da Arewabooks yayi kokari ya sauke ayi Following dina @fadilalamido ko ta link din da ke kasa.

WhatsApp no: 07014197556
https://arewabooks.com/book?id=63ea17c2c189e841487b66f2